
# LITTAFIN RAYUWA III

## LITTAFIN JAGORA DON KANKA DA GIRMAR MA'AIKATA



DALE EVRIST
DAVID SHIBLEY

LifeBook_Volume_3.indd 1 8/24/15 11:15 AM

Daga

David Shibley da Dale Evrist

An Wallafa daga Global Advance Resources
Ma'aikata na Global Advance, Inc
www.globaladvance.org

Wannan littafi ba za a kara sayarwa ba. A wajen Hadin kan Jihohin Amurka (United State), an yardar a kara fitar da fannin darusan domin horaswa, muddin sake fitarwan za a raba kyauta ne.

Sai dai in an lura a wani wuri, dukkan Nassin an dauko su daga Littafi Mai Tsarki na sabon juyin King James ne. Izinin wallafawa 1979, 1980, 1982 daga Thomas Nelson, Inc.



LifeBook_Volume_3.indd 3 8/24/15 11:15 AM

## Abubuwan da ke Ciki

Gabatarwa

**LAFIYAYYUN IKKILISIYOYI**

33 Ka'idodi na Lafiyar Ikkilisiya……………………………………………..
34 Halaye na Makiyayi na Gaskiya (Mai kyau) …………………………………..
35 Yadda za a Kafa Sabon Ikkilisiya……………………..………………………..
36 Almajirantarwa…………..…………………………………………………..
37 Hidimar (Aiki) Kungiya ……………….……………………………………
38 Magada Tare…………………………………………………………………

**FASAHOHI DA KUMA DABARU**

39 Nazari (Bincike) da kuma Wa'azin Maganar Allah na 1……………………..….
40 Shaida Bishara………………………………………………………………
41 Kula da Wahayi (Hange) a Lokuta na Kalubala.………………………………
42 Bada 'Ya'ya da Yawa……………………………………………………….
43 Tadawa (dagawa) da kuma Sake Shugabanai Matasa (Yan kanana)…………
44 Anfani da Lokaci (Kula da Lokaci)……………………………………………
45 Hidimtawa a Wurin Aiki na Masu hidima………………………………………

**RAYUWARKA DA KUMA UMURNIN SA**

46 Zama Shugaba na Babban Umurni……………………………………………
47 Muryoyi Bakwai da zasu Canza Rayuwarka………………………………..
48 Kai Bishara ga Birninka saboda Almasihu……….………………………….
49 Shirya (tattara) Ikkilisiyar ka Saboda Girbi…………………………………
50 Mabudi (Makulli) zuwa ga Girbi……………………………………………
51 Don me Zamu Tafi (zamu Je)………………………………………………
52 Aikin ka a cikin Shirin Allah a Duniya dukka………………………………



LifeBook_Volume_3.indd 4 8/24/15 11:15 AM

## Gabatarwa

**An kira ka don ka shafar da kasarka da kuma duniya domin Almasihu**

Wannan ita ce karfafawa na wannan juzu'i na uku a cikin jerin **LittafinRayuwa.** Ginawa ne a kan littafin jagorori biyu da suka gabata, darusa a cikin **LittafinRayuwa na 3** ta kamala horaswa na shekara guda gaba daya a cikin girmar da kanka da kuma ma'aikata.

Darusa guda ashiri a cikin jagoran **LittafinRayuwa na uku** ta wakilci tushen wannan jerin. Wannan darusa ta karfafa aikin ka a taimakawa don cika Babban Umurni na Almasihu ta wurin dasawa (shukawa) da kuma gina (shayar) da lafiyayyen ikkilisiyoyi, sarrafa fasahohin ka, da kuma tace dabarun ka. Duk wannan don ta zama a cikin mahalli na jarabar kanka don ganin an san Yesu, an kaunace shi, an bauta masa, da kuma an yi masa biyayya ta wurin dukkan munate a kowace kabila da kuma kasa.

Kamar yadda yake a jazu'in da suka gabata, mun bada wannan shawara domin karban yawan anfani daga **LittafiRayuwa na 3**:

- Ka yi addu'a yayen karantawa. Ka roki Ruhu Mai Tsarki ya bayyana maka gaskiya ya kuma taimakeka ka sa ta cikin aiki wannan gaskiya da ka koya.
- Ka yi nazarin **LittafinRayuwa na 3** tare da Littafi Mai Tsarki a bude. Ko da yake an ambata yawancin ayoyin Littafi Mai Tsarki, a yawancin wuri an bada ayan da aka suba ne kadai. Wannan zata barka ka dubi shafufuka a cikin Littafi Mai Tsarki, ko ka samo maganar Allah daga littafi da aka fitar ko a na'urar lantarki. Ta wurin duban wadannan ayoyin da kanka, zaka yi ma'amala (hulda) da Nassi ta hanya da yawa da kanka kuma ka zama da karin sani na wadannan gaskiya masu karfi
- Ka karanta sashi daya kowace mako. Karanta darasi daya kowace rana har mako za ta taimakeka ka ajiye kwakwaran gaskiya da kuma babban shawara a zuciyarka da kuma ruhunka.
- Ka haddace shafin Littafi Mai Tsarki na kowace karshen darasi. Daya daga cikin kayan aikin ka mai girma a matsayinka na ma'aikaci ita ce sanin Nassin ka. Ruhu mai Tsarki zai yi anfani da maganar Allah da ka boye a cikin zuciyar ka.
- Ka yi tunani akan kwakwaran gaskiya na kowace darasi. Wadannan gaskiyar zasu canza rayuwarka! Ka bar Ruhu Mai Tsarki ya yi Magana da kai ta wurin sa wadannan tunani na bada rai da zurfi a cikin ruhunka
- Ka yi shiri don aiki akan abin da ka koya. Bangaren "Amsar Ka" a karshen kowace darasi zarafin ka ne don juyo da gaskiyar rayuwarka zuwa aikace aikacen canjin rayuwa! Ka kudurta don ka yi aiki akan abin da ka kayo.

Bari rayuwarka ta kai cikakken anfanin ta na gaba saboda daukakar Allah, daukakar Dan sa, da kuma warkar da kasashe.

David Shibley
Dale Evrist



LifeBook_Volume_3.indd 5 8/24/15 11:15 AM

WEEK 33

# Ka'idodi na Lafiyar Ikkilisiya

**Karanta Matiyu 16:18; 2 Bitrus 3:18**

A halitta, lafiyayyun abubuwa sun girma (tsiro) – sun dai yiwu. Idan ka datsa (shuka) itace mai bada 'ya'ya a lafiyayyen kasa, ka tanadi isasshen hasken rana da ruwan sama, ka ciyar, ka gyara ka kuma tsastsare itacen yadda ya kamata, za ta bada 'ya'ya. Idan yaro ya sami abinci mai gina jiki, isasshen hutu, motsa jiki, ilimi, da kuma horaswa (tarbi'a), shi ko ita zai kasance da kowane abin da ake bukata don girma cikin kyakkyawa yanayi, ya zama babban (balagaggen) mutum. Bari mu fade ta kuma – lafiyayyen abubuwa sun girma (sun tsiro)! (karanta Yahaya 15:1-5).

Abin da ya zama gaskiya ga itace da kuma yara, gaskiya ce ga ikkilisiyoyi kuma: lafiyayyen ikkilisiyu suna girma. Shi ya sa hankalinmu ba zata koma kan girman ikkilisiya ba, amma zai koma kan lafiyar ikkilisiya ne. Christian A. Schwarz a littafinsa, *Bunkasa Ikkilisiya a Yadda Take*, ya ce, "Ba zamu yi kokarin kera girman ikkilisiya ba, amma maimakon haka mu saki anfanin jikinta wanda Allah ya sa a cikin kowace ikkilisiya. Hakinmu ne mu rage cikas da zai hana girman, a duk ciki da wajen ikkilisiya." A wannan darasi, za mu yi anfani da *Bunkasa Ikkilisiya a Yadda Take* Asalin Ingantattu na Lafiyayyun Ikkilisiyoyi, zamu bukaci Karin hasken fahimtar yadda za a jagoranci lafiya, habaka ikkilisiyoyi da take girma a ruhaniyance da kuma a yawa.

**Inganci (Karko) na 1: Inganta Shugabanci.**

**An yi wannan ne kuwa domin a yanzu a sanar da hikimar Allah iri iri ga manyan mala'iku da masu iko a samaniya, ta hanyar ikkilisiya. Afisawa 3:10**



LifeBook_Volume_3.indd 6 8/24/15 11:15 AM

**Ina dai gaya maka, kai ne Bitrus, a kan dutsen nan ne zan gina ikkilisiyata, wadda ikon Hades ba zai rinjaye ta ba.**
**Matiyu 16:18.**

Littafi Mai Tsarki ta bayyana mana cewa Yesu ya ba wa mutane baye-baye ya kuma sa baye-bayen mutane zuwa ga wasu. (Karanta Afisawa 4:7-12). Lokacin da Yesu ya ba "*wadansu su zama manzanni, wadansu annabawa, wadansu masu wa'azin, wadansu kuma makiyaya masu koyarwa*" domin "*kamantawar tsarkaka domin aikin hidima*." A matsayin shugabanan ikkilisiya an kira mu mu yi anfani da baye-bayen mu da kuma ikonmu don mu shirya mu kuma saki jama'ar Allah zuwa ga hidimar da zata bada 'ya'ya. Inganta shugabanci ita ce kai hankalin shugabanci na farko akan koyarwa, horaswa da kuma shirya tumaki su zama babban jiki na ma'aikata (masu hidma) na Allah a duniya. Wannan aiki fifiko ne guda daya domin mu, kuma wane abin farin ciki ne aikin nan!

**Inganci (Karko) na 2: Fadakakken Baiwar Hidima**. Schwarz ya ce, "Aikin shugabancin ikkilisiya ita ce taimakon membobinta su gano baye-bayen su su kuma sa baye-bayen cikin hidimomin da ta yi daidai da baye-bayen." (Karanta Romawa 12:3-5) ka yi tunani a kanta, Allah yana da mutane a ikkilisiyun mu wadanda aka yi musu baiwa ta dabam daga wurin Sa domin hidima ta musamman a cikin ikkilisiyoyin mu. Aikin mu ita ce mu taimake su su gano baye-bayensu su kuma yi anfani da su da kyau. Akwai hanyar gwada baye-baye da yawa a yalwace don taimakawa da wannan. Amma ko da ba zaka iya samun wadannan gwaje-gwaje ba, ta wurin lura (sa ido) da kuma tadi (hira), za ka iya taimakon mutane su gano yadda Allah ya ba su baiwa. Wane abin burgewa ne a yi tunanin samun ikkilisiya cike da mutane wadanda sun samo baiwar da Allah ya basu don dacewa a hidima cikin jikin Almasihu.



LifeBook_Volume_3.indd 7 8/24/15 11:15 AM

**Inganci (Karko) na 3**: **Jaraba ta Ruhaniya**. A duniya yawancin ikkilisiyoyi da ke girma suna cika da mutane da ke da jarabar bidan fuskar Allah. Allah yana neman mutane wadanda suke da jaraba domin cikakken rayuwan ruhaniyar Sa. (Karanta Afisawa 5:18-21). Ba ya marmarin abin da rukuni ta musamman ke wakilta. Sai dai, Yana marmari da yanayin zuciyar su. Tambayar Allah ita ce, "Kuna yunwan kasancewa Na a sakanin ku?" Idan amsar wannan tambayar "I" ne. Allah ta wurin Kalmar Sa da kuma RuhunSa, zai hadu da su ya sawwaya su (canza su). Dole mu taimaka a kirkiro muhalli ta ruhaniya inda mutane za su iya jarabtuwa su bi kasancewar Allah.

**Inganci (Karko) na 4**: **Sigogi (Tsare tsare) Masu Aiki**. Wannan tana nufin cewa hanya da aka tsara ikkilisioyar mu tana da taimako mai kyau (anfani) a biyan bukatun mutane. (Karanta A. Manzanni 6:1-8). Sigogi (tsare tsare) an yi su domin mutane ne, ba a yi mutane domin sigogi (tsare tsare) ba. Ikkilisiyar da basu da siga mai kyau za ta iya zama da cin rai (zafi) wa mutane a matsayin ikkilisiya mara siga (tsari). Abin da muke nema ita ce ikkilisiya da aka tsara ta da kyau, bisa ga jagoranci na Ruhu, tana aiki ta hanyar da take hidimta wa mutane da kyau. Ikkilisiya da tsarin aikin bisa ga Littafi Mai Tsarki tana taimaka wa jama'a su kara hadewa da zurfi ga rayuwar ikkilisiya da kuma aikin ta.

**Inganci (Karko) na 5**: **Simar da Hidimar Sujada**. A lafiyayyen ikkilisiyu da suke girma, taruwar mako-mako na masu bi lokaci ne na simarwa, umurtawa, da kuma kasarwa. A wadannan taruwa, ibada tana da karfi, maganar ya yi daidai, kuma Ruhu ne shaida. (Karanta 1 Kor 14). Kula (luta) daga ikkilisiyoyi a fadin duniya ta nuna cewa wannan ba sakamakon hayayyafa ba ne. akwai ikkilisiyu a kauyuka da basu da hanyar samu da suke sujada kowace mako a yanayi da ke cike da rayuwa ta Allah. Abin da muke nema lokuta ne iri iri na sujada ta ainihi da kuma mika kai ga sanin Allah na Littafi Mai Tsarki, da kuma barin Ruhun Sa ya motsa ya kuma yi aiki cikin alheri da gaskiya.

**Inganci (Karko) na 6: Kowace bangare (gaba daya) na Kananan Rukunoni**. Schwarz ya ce, "Ikkilisiyu da suke girma sun kirkiro tsari na kananan rukunoni inda Kristoci mutum-mutum za su iya samun aminin (shakuwar) al'umma, taimako a aikace da kuma ma'amala ta ruhaniya." Bangare na kananan rukunoni gaba daya ba



LifeBook_Volume_3.indd 8 8/24/15 11:15 AM

ra'ayin mutum ba ne, shirin Allah ne. iyalai sune tushen kananan rukunoni. (Karanata Farawa 2:18-25). Allah ya tsara sabon aiwatattun Jama'ar Isra'ila bisa ga bangarorin kannana Rukunoni. (Karanta Fitowa 18:13-27). Ikkilisiya na farko an tsara ta bisa fannin kananan rukunoni ne. (Karanta A. Manzanni 2:42-47). Ita ce hanya mafi kyau mafi anfani don tabbatar da cewa kowane mutum ya karbi cikakken aiki (hidima) da kuma kula da shi ko ita ke bukata. Yayen da rukunonin nan suke bin salon da aka samo a Sabon Alkawari da aminci, sun zama tushen mahalli na yin addu'a, binciken Magana, da kuma ginawa, da kuma ribambanya almajirai.

**Inganci (Karko) na 7**: **Bukatar Wayar da kai na Bishara**. Bukatar wayarwa na Bishara tana kan biyan bukatan mutane nan da nan, sa'an nan a kai su zuwa ga wuri na tushen bukata – su tuba daga zunubansu su kuma bada gaskiya ga Almasihu. Wasu lokuta bukatan mutane na nan da nan sune na koyaushe wato abinci da sutura. Wasu zasu bukaci amsoshi ga tambayoyin da suke da ita game da Allah da kuma akan fadar Almasihu (abin da Almasuhi ke fadi a kansa). Har yanzu wasu zasu zama suna dandana tsosa rai mai zurfi na damuwa ko rashin lafiya na jiki inda ake bukatar addu'a. (Karanta Luka 4:16-21). Baiwa na mai bishara ya zama an kai ga taimakon salo, izawa, da kuma shirya ma'aikata na bishara. A fadin duniya ikkilisiyu da suke girma ana sanin su ta wurin mika kai don nuna kaunar Almasihu ga wadanda suke cikin bukata. A matsayin Babban Umurni, masu bi mu biya bukata mu kuma shaida bishara a yankuna da kuma duniya duka.

**Inganci (Karko) na 8**: **Dangantaka ta Kauna**. Allah ya kera mulkinSa don ta yi aiki ta kuma dage a kan tushen dangantaka ta kauna. (Karanta Matiyu 22:37-40). Ba mamaki, an jawo mutane zuwa cikin ikkilisiyoyi inda za su ji wasu su kaunace su sosai. Ba wanda yake so ya zauna shi kadai. Ikkilisiya, na dukan wurare, ta kasance da magani saboda "cuta" na kadaici, kuma mu yi – kauna irin na Kristi. (Karanta 2 Korontiyawa 5:14). A yawancin ikkilisiyu da suke girma mutane da suke so su halarta sukan ji hadewa da wasu. Babu rikitarwa a jagorancin ikkilisiyu da sun girma. Muna bukata mu tabbatar cewa kome muke yi ta maida hankali a kan kirkiro lafiyayiya, tsararriyar, muhalin mulki da ta kahu ta kuma tsaya cikin kauna.



LifeBook_Volume_3.indd 9 8/24/15 11:15 AM

## Rubutu

**HADDACEWA:**
*Sai suka himmantu ga koyarwar manzanni da tarayya da juna, da gutsuttsura gurasa, da kuma yin addu,a (A. Manzanni 2:42)*

**KWAKWARA (ASALIN) GASKIYA**
Hankalin mu kada ya zama akan girman ikkilsiya, amma ya zama akan lafiyar ikkilisiya saboda lafiyayyen abubuwa takan girma.

**MARTANIN KA (AMSAR KA)**

- Dukkan wadannan halaye guda takwas suna da muhimmanci ga lafiyar ikkilisiya.
  Nawa ne daga wadannan ka gani a cikin ikkilisiyar ku? Nawa ne aka rasa?

- Ka sami wasu shugabanai ka kuma bidi Ubangiji akan yadda za a bi lafiya mai girma a cikin ikkilsiyar ku.

- Ka sa su a rubuce matakai da za ka dauka don inganta lafiyar ikkilisiya.



LifeBook_Volume_3.indd 10 8/24/15 11:15 AM

# Halaye na Makiyayi na Gaskiya

**Karanta Yahaya 10:10-16; 1 Bitrus 5:2-4**

Don zama da kyau da tsoron Allah, shugabanai muna bukata mu kasance da zuciyar makiyayi mai kyau. Littafi Mai Tsarki ta dokace mu "Mu yi kiwon garken Allah" da yaddar rai, marmari, da kauna, mika kai (hadaya), da kuma fa'ida (da kyau). (Karanta 1 Bitrus 5:2-4). Ta wurin annabi Ezekiyel Allah ya sawata wa makiyaya na Isra'ila a da saboda kasa yin kiwan jama'a da kyau. (Karanta Ezekiyel 34:1-10). Tana da muhimmanci sosai ga Allah cewa mu a matsayin shugabanai Krista mu yi kiwon garken Sa da maida hankali mai girma da kuma kula.

Domin mu mallaki zuciyar makiyayi mai kyau mu kuma hidimta wa jama'ar Allah ta hanyar da yake so, muna bukatar zuciya na Babban Maikiyayi, Yesu Almasihu. (Karanta Ibraniyawa 13:20). A kasa wasu halaya ne na makiyayi mai kyau kamar yadda Yesu ya kwatanta (ya nuna), yana nufin shi kansa. (Kranata Yahaya 10:10-30). Bari mu dubi wadannan halaye yayen da muke koyon "ba da ranmu" saboda wadanda muke hidimtawa.

1. **Makiyayi na gaskiya yakan kiran tumakin da suna**. A al'adar zamanin (lokacin) Yesu, makiyaya suna ba wa tumakin garkensu suna. Suna zama tare dare da rana sun saba da su. Makiyayi na gaskiya ya san su kuma yakan kira su daya daya. Amma ba ya kan kira su daya daya kawai ba; yana kula da su kuma daya bayan daya. Ita ce hanyar da Yesu yake datsawa da mu- Yakan kira mu da

**Ya gudu ne fa, don shi da na sako ne, ba abin da ya dame shi da tumakin.**
**Yahaya 10:13**

**Ku yi kiwon garken Allah da yake tare da ku, ba a kan tilas ba, sai dai a kan yarda, ba ma don neman ribar banza ba, sai dai da himma.**
**1 Bitrus 5:2**

suna kuma yana kula da kowace bukatan mu. Ta haka, tana da muhimmanci cewa mutane a cikin garken mu mun san su mutum-mutum kuma muna kula da su da daddaya.

A yawancin ikkilisiyu ba mai yiwuwa ba ne ga Fasto ya san kowa sosai ya kuma biya bukatan kowa cikakke. Amma idan ka dauki lokaci ka sani ka kuma lura da wadanda suke kurkusa da kai, ka kuma koya musu su yi hakan nan ga wadanda ke kurkusa da su, za ka rayar da al'ada na daraja da na kula saboda kowane memba na garken. Kasancewa da ma'aikata na kananan rukuni mai fa'aida tana da taimako sosai a tabbatar da ingantaccen shugabanci da kuma kula ga duka. Makiyayi na gaskiya yakan yi aiki da kwazo don kirkira mahalli inda kowane memba an san shi ana kuma kula da shi sosai. (Karanta 1 Korontiyawa 12:25,26).

2. **Makiyayi na gaskiya yakan wuce gaba ya kuma fishe su waje**. A bada labarin Yahaya 10 Yesu ya bambanta kular Sa ga jama'ar Allah da kuma shugabancin Farisiyawa marar kyau. (Karanta Yahaya 10:1-16). Su masu sonkai ne masu bautar ganin ido wadanda suke kawo rikicewa kawai da kuma hukunci. Yesu ya bambamta kyalewar su da kuma karacin shugabanci na adalci da Nasa misali na bayanannen hanya da kuma lura. Makiyayi na gaskiya, Yesu ya ce, yakan ba wa tumakinsa shugaba mai karfi da kuma cancanta don a bi, mutum wanda yake kaunar su yana jagorantar su da kyau. Kamar Yesu, dole mu jagoranci mutanen mu da karfi da kuma kwanciyar hankali, muna bada


LifeBook_Volume_3.indd 12 8/24/15 11:15 AM

bayananen hange mu kuma jagorance su zuwa ga makiyaya mai danya na ciyarwa ta ruhaniya. (Karanta Zabura 23:1-2)

3. **Makiyayi na gaskiya an san muryarsa da kuma yarda da shi**. Yayen da makiyayi ya ci gaba da jagorantar tumakin sa zuwa wuri da ke da tsaro (kariya) isasshe kuma, sun sani za su iya yarda da shi. Don haka, yayen da suka ji muryarsa suna bin sa. (Karanta Yahaya 10:3-5). Jama'armu zasu yi kusa sosai su manne don su bi mu idan muna da tarihi na amincewa. Dole mu zama da bangaskiya mai kyau da su ta wurin zama da aminci da kuma a kullayomi. Yayen da muke aminci ga tumakinmu a Magana da aikatawa zamu samo kan su. Dole mu rabu da tursasawa da kuma alkawari da babu kome kuma basu kafu a cikin Magana da kuma Ruhu ba. Yayen da muka fada wa mutanen mu Magana, dole mu bi ciki. Zama shugaba a rayuwan mutane asirtacciyar amincewa ne kuma babu wanda za a dauka da wasa. (Karanta 1 Bitrus 5:2-3). Tumaki a sauwake suna da rashin kwanciyar hankali – haka ma mutane. Bari mu jagorance su da lura kuma a kullayomi.

4. **Makiyayi yakan bada ransa don kare tumakin Sa**. Yesu ya ce, dan asako, wanda tumakin ba nasa ba, zai gudu yayen da tumakin ke cikin hatsari. (Karanta Yahaya 10:12-13). Amma makiyayi wanda tumakin nasa ne kuma yana kaunar tumakin zai yi kome don ya kare ya kuma tsare su, hade da yakar kowane barawo ko kerkeci da zai yi kokarin ya cuce su. Hakika, mun san cewa Ubangiji Yesu Almasihu, Babban makiyayi, ya biya tushen farashi don ceton mu da kuma kubutar da mu daga abokan gaba na zunubi da mutuwa. (Karanta Yahaya 10:11). A matsayin makiyaya, dole mu bi gurbin Ubangijinmu mu kuma bada ranmu don mu kare mutanen mu daga yaudara, hatsari, da kuma hallaka. Dole mu hidimta musu, hidimtawa cikakke na gaskiyar Almasihu da kuma alheri zuwa gare su. Dole mu gargade su kan hatsarori na sauraron muryar wadanda za su yi anfani da su a kuma ci da gumin su ko su kawar da su a kan hanyar koyarwa na gaskiya. Haka ma, ka da mu bar wani abu na "ruhun dan asako" ya kasance a cikinmu da zai sa mu hidimta saboda anfanin kanmu, mamakon nasu bukata. (Karanta 1 Bitrus 5:2). Mu nuna gurbi mu



LifeBook_Volume_3.indd 13 8/24/15 11:15 AM

kuma hidimta, bawa marar sonkai a kullum muna sa bukata na tumakin mu kafin namu. (Karanata Markus 10:45)

5. **Makiyayi na gaskiya yakan kai tumakinsa zuwa ga wadatacceen rayuwa.** A Zabura 23, Sarki Dawuda ya yi maganar Ubangiji a matasayin makiyayin sa ne, yana kai shi zuwa cikin wurare masu danya kuma cikake. (Karanta Zabura 23.) Yesu ya ce, a matsayin makiyayi mai kyau Zai kai jama'arsa cikin danyar ciyawa da kuma cikakken rayuwa a yalwace – rayuwar wadata a cikin Sa. Yana nufin ga wannan bangare na shugabancin Fasto. Littafi Nazari Mai Tsarki na Nelson ta ce, "Barawo yakan dauke rai; makiyayi yakan bada rai. Rai a yalwace hade da ceto, shayarwa, warkaswa da saura da yawa".

   Wannan rai da Yesu yake kai mutanen Sa zuwa cikin rai madawwami – ba kawai rai mara karewa ba, amma rai wanda ke da inganci a sama. A littafin sa *Makiyayi Dubi Zabura 23*, Phillip Keller, Fasto da kuma makiyayi, ya tuna farin cikinsa yayen da yake kula da tumakinsa: "ba abin da ke sa ni farin ciki fiye da in ga tumakina suna walwalawa suna kuma cin gaba. In ga marikansu na banmamaki." Shi ne yadda makiyayi na gaskiya yake duban zarafi/nawaya na bauta wa jama'ar Allah masu tamani. Yesu, Shugaban Makiyaya, ya zo don ya tanada wa mutanen Sa rayuwa na albarka a yalwace. (Karanyta Yahaya 10:10; 1 Yahaya 3:9). Aikin mu a matsayin makiyaya a kalkashin Babban Makiyayi mu jagoranci mutanen mu zuwa wuri mai zurfi, rayayyiya da kuma kauna ta dayantaka da Kristi. Zamu yi wannan da kyau ta wurin koyarwa da kuma nuna gurbin maganar Allah, nufinsa da kuma hanyoyinsa da tamani da kuma iko. Dole mu kai tumakinmu zuwa wurin ciyawa mai danya da kuma yuwaye na hutawa na Magana da kuma Ruhu.

   Wata rana za mu bada lissafi ga Shugaban Makiyayi na yadda muka yi kiwon tumakinSa. Idan mun yi kiwon tumakin da kyau an yi mana alkawari cewa zamu karbi lada mai yawa daga mai kaunar mu Ubangiji Yesu. Babu abin da zai iya yin kyau sosai! (Karanta 1 Bitrus 5:4).



LifeBook_Volume_3.indd 14 8/24/15 11:15 AM

**HADDACEWA:**
*Ku yi kiwon garken Allah da yake tare da ku, ba a kan tilas ba, sai dai akan yarda, ba ma don neman ribar banza ba, sai dai da himma. Kada ku nuna wa wadanda suke hannunku iko, sai dai ku zama abin koyi ga garken nan. Sa'ad da kuma Sarkin Makiyaya ya bayyana, za ku sami kambin daukaka marar dusashewa. (1 Bitrus 5:2-4).*

**KWAKWARA (ASALIN) GASKIYA**
Idan za mu zama da kyau kuma shugabanai masu tsoron Allah dole mu dauki zuciya na makiyayi na gaskiya da Yesu Kristi ya nuna mana, Babban Makiyayi.

**MARTANIN KA (AMSAR KA)**

- Kowace rana, ka roki Yesu ya baka zuciya na makiyayi na gaskiya domin jama'arka.
- Ku taru da sauran fastoci a al'ummanku don ku yi wa juna addu'a a matsayin makiyaya na garken Allah.
- Ka dubi mutanen ka da ido ta jiki suna tambaya, "Yaya zan bada raina cikakke saboda wadanda Yesu ya kira ni in hidimta.

**Rubutu**



LifeBook_Volume_3.indd 15 8/24/15 11:15 AM

MAKO 35

# Yadda za a Kafa Sabon Ikkilisiya

**Karanta Matiyu 16:18; Afisawa 3:20-21**

Ikkilisiyoyin yankuna (wurare) suna tsakiyar aikace aikace na Allah a duniya a yau. Ikkilisiya ita ce babba, mafi nesa na yanar gizon kai wa ga duniya. Yesu ya yi alkawari cewa ikkilisiyarSa na gaskiya – wanda ta hada dukkan mutane a ko'ina wadanda sun mika kai gare Shi – Zai gina su kuma za su dage wa dukkan kisoshi (hari) na shaidan (ibilis). (Karanta Matiyu 16:18).

Idan kana so ka yi wani abu da zai dawwama na tsawon shekara daya, ka shuka (datsa) furanni. Idan kana so ka yi wani abu da zai dawwama na tsawon rayuwarka, ka shuka (datsa) itace. Idan kana so ka yi wani abu da zai dawwama har abada, ka kafa ikkilisiya (datsa ikkilisiya)! Wadanda sun kafa suka kuma girmar (shayar) da ikkilisiyoyi za su sami yabanyar anfani da za su ajiye a tsawun (gaban) Yesu. (Karanta Yahaya 15:8).

Yesu Kristi shi ne kan ikkilisiya. (Karanta Afisawa 1:22; 5:23: Kolosiyawa 1:18). Ta wurin ikkilisiya Allah ya bayyana hikimar Sa. (Karanta Afisawa 3:10). Ikkilisiya tana matsayin amaryan Almasihu. Kamar yadda ikkilisiyar ke kaunar maigidanta, Yesu yana wanke amaryarsa daga kowace rashin tsarkinta don cewa za a gabatar da ikkilisiya a gare Shi a cikin walkiyarta da kuma kyaun ta. (Karanta Afisawa 5:25-27). Ikkilisiya kuma tana

**Ni na yi shuka, Afolos ya yi banruwa, amma Allah ne ya girmar.**
**1 Korontiyawa 3:6**



LifeBook_Volume_3.indd 16 8/24/15 11:15 AM

**Daukaka ta tabbata a gare shi a cikin ikkilisiya ta wurin Almasihu Yesu, har ya zuwa dukkan zamanai har abada abadin. Amin. Afisawa 3:21**

matsayin jikin Almasihu. Ta wurin ikkilisiya Yesu ya nuna kaunarSa da kuma ikonsa wa duniya. (Karanta Kolosiyawa 1:24).

Ikkilisiya a fadin duniya ta sami salon Magana a jikin masu bi na wurare a cikin Kristi. Lura cewa yawancin wasikun Manzo Bulus ya rubuta wa ikkilisiyoyi da suke taruwa a birane takamaimai. (Karanta Romawa 1:6; 1 Kor 1:2; 2 Kor 2:2; Galatiyawa 1:2; Afisawa 1:1; Filibiyawa 1:1; Kolosiyawa 1:1; 1 Tasalonikawa 1:1; 2 Tassalonikawa 1:1).

Fastoci sune zasu kare (tsare) su kuma yi kiwon ikkilisiya da aka danka a kalkashin kulawar su. (Karanta 1 Timoti 3:5). Fastoci da dattawa wadanda suke da aminci ga kiran su don su zama makiyayin garken Allah zasu iya farin cikin sa sammanin (sa zuciyar) rawanin daukaka daga wurin Shugaban Makiyayi, Yesu Kristi. (Karanta 1 Bitrus 5:1-4).

Ikkilisiya na farko a Urushalima ikkilisiya ce na bishara. Hakika, mutane suna bada gaskiya ga Almasihu kowace rana. (Karanta Ayukan Manzanni 2:47). Wadancan masu bi na farko sun dauki umurnin Ubangiji da gaske don su yi shelar bishara na Yesu Almasihu ga kowane mutum a duniya. (Karanta Markus 16:15). Sun fita suna yada bishara suna kuma kafa sabobin ikkilisiyoyi. (Karanta Ayukan Manzanni 8:4; 3 Yahaya 7). A yau mun ci gaba da yin biyayya ga umurnin Almasihu ta wurin kafa ikkilisiyar zumunta na masu bin Almasihu a sakanin kowane rukunin mutane a duniya. (Karanta Matiyu 28:19; Romawa 7:9-10).



LifeBook_Volume_3.indd 17 8/24/15 11:15 AM

Samfuri (yayi) na biye ta wurin addu'a an tsara daga kungiya da suke kafa sabobin ikkilisiyoyi da himma a arewacin Indiya. Wanna ita ce bangare na duniya inda sun rage da ke da rukunin mutane da ba a kai musu bishara ba kuma da suna da karancin mashaidi. Samfurin da aka gabatar a wannan darasi, da masu kafa ikkilisiyu a Indiya suka shirya, tushen gada ka'idodin Littafi Mai Tsarki ne da kuma bisa ga umurnin da Yesu ya ba wa almajiransa kafin su tafi sabon wuri. (Karanta Matiyu 10:11-13; Luka 10:1-9).

Akwai wasu samfuri (salo) domin fara ikkilisiyoyi da suke da kyau haka nan. Yawancin ikkilisiyu an kafa su daga binciken Littafi Mai Tsarki na bishara ne. Wasu ikkilisiyu sun fara daga kananan rukunonin gida ne. zaku iya zaba daga yawan dabarun kafa ikkilisiyu masu kyau yadda da Ruhu Mai Tsarki ke jagorantarku. Abu mafi muhimmanci ita ce ka mika wannan, ta wurin alherin Allah, za ka zama mai kafa ikkilisiya.

Ga matakai don kafa sabobin ikkilisiyu, kamar yadda aka jera su ta wurin yan'uwanmu da suke aiki a sakanin mutanen da basu ji bishara ba a arewacin Indiya.

1. **Ka karbi wahayi (hange) daga wurin Allah**. Wannan a kullum ita ce mataki na farko. A fili yake ba zaka iya yin dabon kira daga Allah. Duk da haka, za ka iya bada kanka gare Shi, ka gaiyace shi ya cika nufinsa ta wurin ka. A kullum Allah zai ajiye birni ko mutane a zuciyar ka. Ka saurara ka kuma amsa wadannan gaggawar kira daga Ruhu Mai Tsarki. (Karanta Karin Magana 29:18).

2. **Ka Horas da Kungiya**. Lokacin da Yesu ya aiki almajiranSa, ya aike su biyu-biyu. Aikin kungiya daga farkon fari na ikkilisiya za ta taimaka a kafa ikkilisiya daga wuri mai karfi. (Karanta 2 Timoti 2:2).

3. **Ka gano wurin**. Ubangiji zai riga ku gaba zuwa birni ko wurin mutane inda za a karbe ku a kuma marabceku. (Karanta Luka 10:8)

4. **Ka gano "kakkarfan mutum" mai ki**. A kowace birni ko kauye, ikokin aljannu sukan nemi su rufe mutane cikin duhu. Ka roki Ruhu Mai Tsarki

domin sakankancewa don ka gano ruhun da ke hana mutane daga rayuwa a kalkashin mallakan Yesu Kristi. Sa'an nan ka tsaya cikin karfin ruhu gaba da "kakkarfan mutum" ka amsa nasara domin Yesu. "Ga shi na baku iko akan dukkan iko na magabci kuma babu abin da zai cuce ku ko kadan. (Karanta Markus 3:27).

5. **Ka yi addu'a da azumi ka tafi wurin da kake hari**. Ka tafi takamaiman wuri inda kake tunanin kafa sabon ikkilisiya. Ka taka wurin (ka zagaya) wurin kana tafiya, ka roki Ruhu Mai Tsarki domin fahimtar yadda zaka hidimta a wannan wurin da kyau. Yayen da kake addu'a, ka shaida ta wurin bangaskiya cewa za a kafa sabon ikkilisiya a nan saboda fadada mulkin Allah a wurin. (Kranata Joshuwa 1:3).

6. **Ka nemi mutane masu karbuwa (budaddun mutane) "mutum mai salama".** Idan Allah ya nawaita ka saboda wuri takamaimai, Ya riga ya shirya mutane da zasu karbe ka. Kuma, yana shirya mutum mai dabara "mutum mai salama", ya taimake ka ta muhimman hanyoyi. Ka zauna a gidan mai salama. Ka fara ikkilisiya ko a gidansa ko a gidan budaddun mutane. (Karanta Matiyu 10:11-13; Luka 10:5-9).

7. **Ka shaida bishara ka kuma kawo mutane zuwa ga bangaskiya**. Kowace ikkilisiya ya kamata ta zama ikkilisiya mai bishara gada farkon ta. Kai wa mutane bishara ta zama bangaren jini ta ruhaniya na sabon ikkilisiya. Jazircewarka a yin bishara za ta zama samfuri (manuni) domin sabobin tuba wadanda zaka horas don kawo wasu zuwa ga Almasihu.

8. **Ka almajirantar da rukuni na tsakiya**. Ka koya wa budaddun mutanen don su jawo iyalansu da kuma abokanan su ga Almasihu. (Karanta Matiyu 4:19). Abubuwa na musamman (kamar su taruwan bishara ko binciken Littafi Mai Tsarki na bishara a gidan mutum mai salama) zai tanadi zarafi domin karamci da kuma gaiyatar abokanai. Ka dora hannu akan asalin rukunin da kake



LifeBook_Volume_3.indd 19 8/24/15 11:15 AM

horaswa ka kuma umurce su su jawo iyalansu da kuma abokanan su zuwa ga Almasihu. (Karanta 2 Timoti 1:6).

9. **Ka gabatar da sabon ikkilisiya a ranan da aka sanar.** A wannan wuri, sai dai idan Ruhu Mai Tsarki ya bi da kai ta wata hanya dabam, iyakar tallatawa da kake bukata maganar baki ne kawai. Wadanda ka horas a rukuni na tsakiya zasu tafi wuraren da suke da tasiri su gaiyaci iyalansu, abokai, da kuma mataimaka zuwa sujada ta farko na sabon ikkilisiya.

10. **Ka gano ka kuma zabi shugabanai masu ruhaniya**. Za a sami wadansu daga rukuni na tsakiya da ka horas wadanda zasu fara tashi a matsayin shugabanai na ruhaniya. Ka gano su, ka koya musu abubuwan da Littafi Mai Tsarki ke bukata ga shugabancin ikkilisiya, ka kuma zabe su zuwa ga ayuka. Lura cewa Bulus ya danka wa Titus aiki ba na kafa ikkilisiyoyi kawai ba amma ya tada shugabanai a kowace gari inda aka kafa ikkilisiya. (Karanta Titus 1:5-9).

11. **Ka sake yi kuma da sabon wahayi (hange) daga wurin Allah**. Akwai wadanda suke karanta wannan darasi wadanda ba zasu kafa ikkilisiyu ba, Allah zai yi anfani da su don haifan masu ra’ayin kafa ikkilisiya! Idan wani abu ya motsa a cikinka yayen da kake karanta jimlar da ya gabata, ka rungumi aikin Ruhu a cikin rayuwarka don ya shirya ka ka fara sabobin ikkiliyu domin daukakar Allah.



LifeBook_Volume_3.indd 20 8/24/15 11:15 AM

**HADDACEWA:**
Daukaka ta tabbata ga wannan da yake ikon aikatawa fiye da dukkan abin da za mu roka, ko da za mu zata nesa, wato, aikatawa da karfin ikonsa da yake aiki a zuciyarmu. Daukaka ta tabbata a gare shi a cikin ikkilisiya ta wurin Almasihu Yesu, har ya zuwa dukkan zamanai har abada abadin. Amin. Afisawa 3:20-21

**KWAKWARA (ASALIN) GASKIYA**
Ikkilisiya ita ce tsakiyar aikace aikace na Allah a duniya. Kafa sabobin ikkilisiyu muhimmin bangare na cika Babban Umurni.

**MARTANIN KA (AMSAR KA)**

- Ka roki Allah ya baka wahayi (hange) domin Takamaiman yanki inda Yake so ya kara daukakar Sa ta wurin tada sabon ikkilisiya

- Ka fada masa tun da wuri cewa zaka yi biyayya Ga kiransa don kafa sabon ikkilisiya

- Yayen da ka karbi kiran Allah don ka kafa sabon Ikkilisiya, ka fara nan da nan don ka dauki matakai da suka dace zuwa ga fara sabon ikkilisiya

**Rubutu**



LifeBook_Volume_3.indd 21 8/24/15 11:15 AM

# Almajirantarwa

**Karanta Matiyu 28:19; Yahaya 8:31; 13:35; 15:8**

Almajiri Krista ya na kaunar Yesu, yana koyon maganar sa, nufinsa, hanyoyin sa, yana kuma rayuwa don bauta masa, a kullum da duban kawo masa daukaka da kuma yabo. Yesu ya kira mabiyansa su zama almajirai balagaggu su kuma almajirantar da wasu balagaggu. Don yin wannan dole mu fahimci menene almajiranci na Littafi Mai Tsarki take nufi, da kuma yadda za mu taimaki wadanda muke hidimtawa su yi rayuwa a matsayin almajirai na gaskiya.

A littafin kayan aiki na Almajiri, an kwatanta almajirantarwa na Littafi Mai Tsarki a matsayin zama "izawa ta wurin kauna domin Almasihu, kafaffe cikin bangaskiya na biyayya, bishewa ta wurin maganar Allah da kuma izawar Ruhu Mai Tsarki." Yesu a fili ya umurci mabiyansa su je su almajirantar ta hanyar da yayi. (Karanta Matiyu 28:18-20). Wannan darasi zata taimake mu mu san yadda zasu siffata amintattun masu bi cikin Almasihu don su zama balagaggu, almajirai masu bada 'ya'ya na Yesu Kristi.

**Don haka sai ku je ku almajirtar da dukkan al'ummai, kuna yi musu baftisma da sunan Uba, da Da, da Ruhu Mai Tsarki Matiyu 28:19.**

1. **Yesu takamaimai ya kira almajiransa su bi shi**. A zamanin Yesu, almajirai masu anfani a gaba sukan nemi izini su bi wani malami. Bin malam, sauraron koyarwarsa da kuma zama kamar Sa, a kullum an ajiye saboda masu ilimi sosai. Amma Yesu ya yi wani abu dabam sabanin abin da akan yi. Ya tafi wurin almajiransa masu anfani a gaba ya



LifeBook_Volume_3.indd 22 8/24/15 11:15 AM

**Ta haka, kowa zai gane ku almajiraina ne in dai kuna kaunar juna. Yahaya 13:35**

kira su don su bi shi. (Karanta Matiyu 4:18-22). Ya zabi mutane kawai ya sa su zama mafifitan mutane. Muna bukata mu roki Ubangiji ya nuna mana wadanda yake kiran mu don mu sa su girma (balaga), su zama almajirai masu anfani ya kuma "kira su waje." Ba dole mu jira su su zo gare mu ba. Dole mu je wurin su mu kuma kira su zuwa ga tafiya iri dabam dabam na sawwayawa ta ruhaniya.

2. **Yesu ya kira almajiransa su kasance tare da shi**. (Karanta Markus 3:14.) Yesu ya sani cewa don a koyar, horas, a kuma sawaya wadannan mutane don su zama ma'aikta masu anfani su kuma zama da halin tsoron Allah, Yana bukata ya kashe lokaci mai yawa da su. Maimakon gaiyatarsu don su yi zaman rayuwa na mulkin Allah da shi, yau da kullum. Dole mu gaiyaci mutane zuwa ga "rayuwa zuwa rayuwa" na dangantaka ta almajirantarwa. Yayen da muka marabci wadanda muke almajirantarwa zuwa cikin rayuwarmu na yau da kullum, mun kara babban damarmaki domin shaida rayuwa da kuma yadda zata zama rayuwa a cikin Almasihu.

3. **Yesu ya koya wa almajiransa maganar Allah da kyau sosai**. Daga farkon almajirancin dangantaka na Yesu da mabiyansa, Ya koya musu gaskiyar Maganar Allah. Yesu kalma ne ya zama jiki. (Karanta Yahaya 1:1). Sun saurari Yesu yana koya musu kuma sun saurare shi yayen da yake musu wa'azi Yake koya wa wadansu kuma. (Karanta Matiyu 5:1-2).



LifeBook_Volume_3.indd 23 8/24/15 11:15 AM

A sakamakon haka suka san maganar sosai. (Karanta Luka 24:44-45). Babban bangare na almajirantarwa ita ce a koya musu Nassi. (Karanta Yahaya 8:31). Ka yi anfani da kayan aikin almajiranci mai kyau da kuma Littafi mai Tsarki da zaka iya samu, don ka taimaki dalibanka-almajirai su girma a cikin fahimta su kuma aikata Maganar Allah.

4. **Yesu ya nuna gurbin inganta aiki wa almajiransa**. Yesu bai koya musu kawai ba, ya horas da su. Ya nuna musu yadda ake hidimtawa a rayuwa da kuma ikon mulkin Allah. (Karanta Matiyu 9:1-38). Koyarwar mu kada ya zama kwarya kwaryar gaskiya kawai. Dole mu tafi tare da almajiranmu mu kuma nuna musu yadda zasu yi rayuwa da kuma hidima ta hanyoyi iri iri na Ruhu Mai Tsarki. Wannan zai hada da kowace bangare na rayuwa. Tana da muhimmanci sosai a gare su su lura da tafiyar mu cikin ruhun kaskanci, yafewa, hadaya, da kuma bauta (halin bawa) kamart yadda yake a gare su don su ganmu muna addu'a da wa'azi cikin iko. Ba muna almajirantar da mutane zuwa ga kanmu ba ne, amma zuwa ga Yesu ne. (Karanta 1 Korontiyawa 2:2-5).

5. **Yesu da gangan ya saki almajiransa zuwa cikin ikon Ruhun hidima**. Yayen da Yesu ya ji ya nuna gurbin hidimar mulki isasshe ga almajiransa Ya aike su, ya sake su don su je su gwada abin da Ya nuna musu gurbin. (Karanta Luka 9:1-6). Bayan mun nunan a fili ga wadanda muke almajirantarwa abin da muke yi da dalilin da ya sa muke yin ta, sa'an nan mu sake su don aiki (hidima) kuma. Babu musanyawa ga aiwatar da kowace abubuwa da akan nuna gurbi a gare su. Sabobin wuraren aikin su zasu fito da tambayoyi masu yawa kamar yadda amsar take. Sa'an nan zasu dawo wurin mu don a taimaka musu amsa tambayoyin su mu kuma taimake su ci gaba da girma.

6. **Yesu ya tabbatar ya kuma karfafa almajiranSa ta hanya mai kyau**. Yesu ya san cewa almajiransa suna bukatar amsa (sakamako) mai kyau don karfafa karfin halinsu a cikin aiki wanda Almasihu ya kira su. Lokacin da Bitrus ya bayyana Yesu daidai cewa shi ne Kristi, Ubangiji ya fada masa cewa an bayyana masa ne daga sama. Ya kuma fada masa za a yi anfani da shi sosai a



LifeBook_Volume_3.indd 24 8/24/15 11:15 AM

gina ikkilisiyar Almasihu, sa'an da ya yi anfani da "makullin mulkin sama," wanda Yesu da kansa ya ba shi. (Karanta Matiyu 16:16-19). A karshen aikin sa a nan duniya Yesu ya karfafa almajiransa cewa zasu yi "manyan abubuwa" bayan barinsa da kuma zuwan Ruhu Mai Tsarki. (Karanta Yahaya 14:12-14). Gurbin Yesu shi ne abin da za mu bi. Dole mu gano girma mai kyau mu kuma rayar a cikin wadanda muke zubawa a cikinsu mu kuma ambata musu ita da karfafawa mai ban sha'awa.

7. **Yesu ya tunkari almajiransa ya kuma gyara su**. Kamar Yadda Yesu yake so ya karfafa almajiranSa, akwai lokaci kuma sa'ad da ya gyara su. Ya yi haka domin yana kaunarsu kuma yana so ya ga sun san gaskiya sun kuma girma su kai ga balaga. (Karanta Markus 10:35-45). Dole mu kaunaci wadanda muke almajirantarwa sosai da tawali'u amma mu kyara wadancan halaye da kuma dabi'u a cikin rayuwar su da ba daidai da darajar mulki ba.

8. **Yesu da jaraba sosai ya kaunaci almajiransa ya kuma hidimta musu**. Yesu ya mika kai ga wadanda yake zuba (kwarara) rayuwar sa a cikinsu. (Karanta Yahaya 13:1-34). Ya ba da ransa domin su ta hidimar kauna. Wannan, fiye da kowace dalili, da ya sa almajirai suka bi shi. Haka wannan zai zama gaskiya a gare mu. Idan zamu kaunaci wadanda muke almajirantar da su da kuma hidimata musu, zasu hadu da mu "a zuciya." Ka tuna, kowace abu a mulki tana aiki bisa tushen kauna, mika kai cikin dangantaka ne (Karanta Mtiyu 22:36-40).

9. **Yesu da karfin hali ya umurci almajiransa**. Sa'ad da Yesu ya almajirantar da mabiyansa sosai da kyau sa'an nan ya umurce su don su fadada mulkinsa a cikin zuciyar mutane, a hankali kuma da karfin hali (Karanta Ayukan Manzanni 1:8). Yesu ya horas da su sosai. Kome da ake bukata a fada an fade su. Dukkan abin da ake bukata a yi an riga an yi. Suna shirye. Hakika, suna bukatar hidimar Ruhu



LifeBook_Volume_3.indd 25 8/24/15 11:15 AM

Mai Tsarki na lokaci zuwa lokaci amma suna shirye don zu tafi su kuma hidimta kamar yadda Yesu ya koya musu. (Karanta Yahaya 14:18).

Idan mun yi da kyau cikin almajirantarwa za mu iya zama da wannan karfin hali haka. Muna bukata mu umurci wadanda muka almajirantar su tafi su almajirantar da wasu. Haka kuma, muna bukata mu umurce su su shaida su kuma gwada (nuna) bisharar mulkin a duk inda suka je. (Karanta Ayukan Manzanni 14:21-23).

10. **Yesu a ko da yaushe yana karfafa almajiransa**. Lokacin da Yesu ya haura sama ya kuma dauki wurin sa a dama ga Uba, Ya aiko da Ruhu Mai Tsarki daga wurin Uba don ya iza ya kuma jagoranci almajiransa. (Karanta Yahaya 15:26-27). Yesu ya ci gaba da aiki da su, bai taba barin su ko yashe su ba. (Karanta Markus 16:19-20). Dole mu ci gaba da zama a yalwace ga wadanda muke almajirantarwa. Zasu anfana daga karfafawar mu da kuma addu'ar mu. Ko da yake sun girma zuwa ga balaga akwai lokaci sa'ad da zasu bukaci shawarar mu da kuma horaswar mu.

Wata babban farin ciki na almajirantarwa ita ce zarafin bayarwa a cikin 'ya'ya manya maza da mata a cikin Ubangiji. Yayen da suka fara almajirantar da sabon tsara, hayayyafa domin Kristi da kuma milkinsa ta zama fafada (Karanta Yahaya 15:8; 2 Timoti 2:2).



LifeBook_Volume_3.indd 26 8/24/15 11:15 AM

**HADDACEWA:**
Ta haka, kowa zai gane ku almajiraina ne In dai kuna kaunar juna. Yahaya 13:35.

**KWAKWARA (ASALIN) GASKIYA**
Yesu a bayyane ya dokaci mabiyansa su Sa wasu su zama mabiyanSa.

**MARTANIN KA (AMSAR KA)**

- Ka bi da Allah dangane da mutum mutum da ya kamata ya kira don su hadu da ku a cikin dangantaka na almajirantarwa
- ka kalubalanci shugabananku su yi haka nan, ku gano wadanda da zasu taimaka su kawo girma (balaga) cikin Kristi.
- Ka dauki wani da kake almajirantarwa tare da kai yayen da kake hidimta mai wani dabam. Wannan ita ce zarafi mafi kyau ga duk samfurin hidima da kuma aikata "rayuwa zuwa rayuwan almajiranci.

## LITTAFIN RAI

### Rubutu



LifeBook_Volume_3.indd 27 8/24/15 11:15 AM

# Hidima (Aiki) a Kungiyance

**Karanta Romawa 12:3-6; Afisawa 4:11-13.**

Lokacin da Yesu ya haura zuwa sama Ya ba da baye baye wa mutane ya kuma sa baye bayen mutanen don shiryar da dukkan masu bada gaskiya (masu bi) domin aikin hidima. Ya ba da baye baye ya kuma kira wadannan mutum mutum don su hidimta tare a matsayin kungiya; su tsara su kuma shiryar da masu bi bisa ga baiwa da Allah ya ba su daidai kuma don aiki a jikin Kristi. (Karanta Markus 6:7; Afisawa 4:7-14)

Za a iya bada ma'anar kungiya kamar haka "yawan mutane shiryayye don aiki tare a matsayin rukuni." Fasto Wayne Cordeiro a littafin sa *Yin Ikkilisiya a Kungiyance* ya ce, "Gina kungiyoyi bai fara da wani irin takamaiman fasaha ba. Ta kan fara da wata takamaiman irin zuciya ne. wannan ita ce na rashin sonkai, ainihin zuciya, marmarin abu mafi kyau na Allah. A kullayomi tana yin tambaya, 'Ta yaya zan hada da wasu?' Tana sammanin farin cikin shaida dandanawa, gwagwarmaya da kuma nasarori. Ta gane cewa kamar jiki, zamu yi aiki mafi kyau a cikin kungiya (a kungiyance). Wannan ita ce yadda Allah ya tsara (shirya) mu don mu yi aiki mai kyau." A wannan darasi zamu gano yadda ya kamata mu yi aiki tare a ainihin kungiyar hidima ta wurin cikakken daukar ofisoshin hidima na Yesu ya zaba a cikin ikkilisiyar Sa. Wadannan baye baye na ofishin a wasu lokuta suna a matsayin "ma'aikatu guda biyar". (Karanta Afisawa 4:11).

**Da yake muna da baiwa iri iri, gwargwadon alherin da aka yi mana, to, sai mu yi anfani da su. In ta annabci ce, sai mu yi anfani da ita gwargwadon bangaskiyarmu, Romawa 12:6.**

**kai kuwa, sai ka natsu a cikin kowace hali ka jure wa shan wuya, kana aikin mai bishara, ka cika hidimarka. 2 Timoti 4:5.**

1. **Aiki tare a matsayin kungiyan manzanni.** Yayen da wasu ke jinkiri su sa (su bada) matsayin "manzanni" akan kowa a yau, mun yarda cewa Almasihu ya ci gaba da ba wa wasu shugabanai su shaida bishara da karfi su kuma fara sabon ayuka. A yau baiwar manzanci tana aiki lokacin da wani an aike shi ya je ya yi shelar sakon Allah na tuba da kuma fansa ya kuma kafa al'ummomin yin sujada na almajirai Krista. Yesu ya umurci manzanninsa su yi wannan abu. (Karanta Matiyu 28:18-20; Markus 16:15-20). Manzo Bulus da Yesu ya kira shi ya zama "Manzo ga Al'ummai" ta wurin yada bishara da kuma kafa ikkilisiyu a sakanin Al'ummai (Karanta Romawa 11:13) a cikin mahalli na hidimar kungiya, aikin shugaban manzanni ne ya sa kungiya su yi tunani "ta hanyar manzanci" wato, su maida hankali akan hayayyafa masu aiki da kuma ma'aikatu ta hanyar da zata dawama.

   Kungiyar manzanni suna aiki tare don aikawa da kuma su je, su hayayyafa su kuma kafa sabobin bishara. Idan babu shugaban manzanci a kungiyar hidimarku, ku kafa dangantaka ta yarda da wani da ke da baiwa ta wannan hanya – wani wanda zai zo lokaci-lokaci ya kuma sa kungiyarku yin tunani da kuma aiki zuwa ga lafiya, tsarin girma. Za ku gano cewa hidima irin na shugaban manzanci za ta inganta kungiyarku su yi tunani, yi addu'a su kuma bauta a wurin da kuma duniya gaba daya.

2. **Aiki tare a matsayin kungiyan Annabawa.** Annabi balagaggen mai Magana da yawun Allah ne ta



LifeBook_Volume_3.indd 29 8/24/15 11:15 AM

ruhaniya. Wannan wani ne mai baiwar shelar annabcin zuciyar Allah ga ikkilisiya. Annabawa na Sabon Alkawari suna karfafa, ingantawa, suna kuma gargadi. Kuma, suna taimakawa a saki annabcin alheri a dukkan ikkilisiya. Ta yin haka, wahayin abin da Allah yake yi a cikin ikkilisiya da kuma a duniya ta zama a bayyan a fili. (Karanta Romawa 12:6).

Dukkan masu bin Almasihu an kira su su zama “mutane masu annabci” (Karanta 1 Korontiyawa 14:1-3). Kowane mai bi ya kamata ya koyi jin muryar Ubangiji a fili ya kuma amsa. (Karanta Kolosiyawa 1:9). Mutum mai baiwar annabci Almasihu yana anfani da shi don taimakon ma’aikatan kungiyoyi na ikkilisiyu su neme shi domin wahayi da kuma hanya. Idan kana da mutane a sakanin ku wadanda masu hidimar annabci ne na gaskiya, ka karba daga alherin da ke a cikin rayuwar su.

3. **Aiki tare a matsayin kungiyan masu wa’azin bishara**. Mai wa’azin bishara mutum ne da aka yi masa baiwa kuma Yesu ya kira shi don ya nuna gurbi, ya iza, ya kuma shiryar da wa’azin bishara – shaida Albishir Mai dadi na Allah na ceto ta wurin Yesu Almasihu. Idan zamu zama da kungiyoyin aiki da suke jawo batattun mutane zuwa ga Almasihu, muna bukatar hihimar wadanda aka shafe (kebe) su a matsayin masu wa’azin bishara. (Karanta Ayukan Manzanni 8:4-13; 2 Timoti 4:5). Da nadama (da dana sani) wannan baiwa a kullum an kyale ta a cikin ikkilisiya. Wannan ya kai ga rashin jaraba da kuma rashin batattun mutane da ke zuwa gun Yesu. Kowane mai bi a cikin Kristi an kira shi ya shaida ma wasu wannan abin da ya sa shi (ya kai shi) ga ceto. Kadan ne suke da baiwa na yin bishara amma dukkan muna da daman a shaida bishara. Almasihu ya kira mu don mu zama bangare na kungiyoyin wa’azin bishara da ke simar da al’ummominmu da kuma kasashenmu da ikon sawayawa na bishara.

4. **Aiki tare a matsayin kungiyan Fastoci (makiyaya).** Fasto shi makiyayi/mai lura ne wanda an kira shi don ya tanadi kariya da kuma kulawa ga tumakin Allah da ke kalkashin kulawar sa. A cikin wadanda suke da baiwan fasto (makiyaya) akwai matakai dabam dabam na fahimta da kuma kwarewa cikin jagorantarwa da kuma ciyar da tumakin Allah. (Karanta 1 Bitrus 5:1-4).

Yayen da muke hidimta wa juna cikin kaskanci da girmamawa, zamu zama da karfi da kuma Karin anfani a tanadar da kauna da kuma shayarwa na kular fasto domin tumakin da muke bautawa. Yesu ya kira mu mu kara koya akan abin da ake nufi da zama “makiyayi mai kyau”, kamar yadda ya zama. Shi ne misalin mu (abin koyin mu). (Karanta Yahaya 10:1-16). Kamar yadda zuciyar makiyaya suke bunkasa a cikin rayuwar taron shugabanai kowane mutum zai sami albarka da kuma anfani. Murmushin Yesu zata zauna akan kungiyan fastoci da suke addu’oi suna kuma tattaunawa a kullum dangane da yadda zasu kara bada kula sosai ga garken Allah.

5. **Aiki tare a matsayin kungiyan masu koyarwa**. Malami mutum ne wanda Allah ya kira shi don ya bada ma’ana dalla dalla da kuma aikatawa na Nassi. Yayen da gaskiya ne cewa a yawancin yanayi an kiran fastoci malamai kuma, tana da taimako a gane cewa akwai takamaiman mutane da aka yimmusu wannan baiwa ta musamman a matsayin malaman Maganar Allah. (Karanata Ayukan Manzanni 18:24). Wadannan malama ya kamata a basu yanci don su taimaka a kafa rukunai da kuma wa’azi mai karfi da kuma koyaswa. Su yi ta jagorantar kungiyan masu koyarwa wadanda suke bincikawa suna kuma girma tare a cikin fahimtar gaskiyan Littafi Mai Tsarki. Wannan shi abin da manzanni suka yi a ikkilisiya ta farko. Sukan hadu tare su bincika su kuma shirya koyarwa. Sa’an nan su zabi wadanda zasu koyar da wasu, daga gida zuwa gida, don fahimtar gaskiya su kuma aikata su a fili. (Karanata Ayukan manzanni 2: 42; 2 Timoti 2:2). Yayen da shugabanan ikkilisiya suke aiki tare a matsayin kiungiyan masu koyarwa a cikin ci gaba da aka kafa da karfi cikn gaskiya a zuciyar mutane.



LifeBook_Volume_3.indd 31 8/24/15 11:15 AM

6. **Aiki tare a matsayin kungiyan wadanda aka yi mjusu baiwa ta ruhaniya.** Kari akan ofishoshin hidima (aiki) guda biyar da Yesu ya zaba wa ikkilisiya, da kluma baye bayen da Ruhu ya rarraba yadda ya ga ta dace, kowane mai bi yana da baiwa ta ruhaniya da ke iza shi ko ita domin wuri na dabam na hidima mai anfani. (Karanta Romawa 12:3-6); Afisawa 4:15-16). Aikin dukkan shugabanan ikkilisiya ne su taimaki wadanda suke hidimtawa su gano baye bayen su su kuma yi anfani da su saboda daukakar Allah da kuma anfanin dan adam. Ku tuna, babu wani a cikin mu wanda yake da baiwa da ya fi na wanin mu duka gaba daya. Bari mu yi aiki cikakke da baye bayen mu dabam dabam a fadin ikkilisiya tare domin daukakar Almasihu.



LifeBook_Volume_3.indd 32 8/24/15 11:15 AM

LITTAFIN

**Rubutu**

HADDACEWA:

Da yake muna da baiwa iri iri, gwargwadon alherin da aka yi mana, to, sai mu yi anfani da su. In ta annabci ce, sai mu yi anfani da ita gwargwadon bangaskiyarmu, Romawa 12:6.

**KWAKWARA (ASALIN) GASKIYA**

Lokacin da Yesu ya haura zuwa sama ya ba wa mutane baye baye ya kuma sa baye bayen mutanen don shiryar da masu bi saboda aikin hidima.

**MARTANIN KA (AMSAR KA)**

- Ka tara shugabancin kungiyarka wuri daya. Ka tabbatar ka kuma karfafa kowane memba na kungiyar domin muhimmin aiki da shi ko ita ke ji. Ku yi addu'a tare domin Karin hanyoyi masu anfani don aiki a kungiyance. Ka bunkasa shiri don taimakon kowane memba a cikin fadin hidimar kungiya a ikkilisiyarku.

- Ka samo yadda aka yi tasiri da kungiyarku da kuma simarwa ta wurin ma'aikatu biyar. Idan ka samo akwai gibi wannan. Cikin addu'a ku tattauna yadda za a cike wadannan gibi da mutane maza da mata da aka yi musu baiwa wadanda zasu taimakeka ka kara bada 'ya'yanka.

- Ka yi addu'a kowace rana domin kungiyarku. Ka kai kowane mutum gaban Yesu, ka roke shi ya taimakeka ka zama da godiya domin aikin kowane mutum. Ka roki Ruhu Mai Tsarki ya nuna maka yadda sa kowane mutum a wurin sa domin babban anfanin sa a fadada mulkin Allah.



LifeBook_Volume_3.indd 33 8/24/15 11:15 AM

## MAKO 38

**Karanta Afisawa 5:22-29; 1 Bitrus 3:7**

Allah ya kira ka/ki da kuma matarka/maigidanki ku zama abokan tarayya ta fannin rayuwa iri iri wadanda suke hidimta wa Ubangiji Yesu Almasihu tare. Yana so rayuwanku tare ta cika da albarka na zama "magada tare na alherin rayuwa." (Karanta 1 Bitrus 3:7-9). A matsayin "magada tare" kun karbi dukkan abubuwa masu kyau daidai da ke kwararowa daga alherin Allah. Gado cikin aikin fansa na Almasihu tana bude kofa ga rai a yalwace da Allah ya kudurta domin ku don ku ji dadi tare. (Karanta Yahaya 10:10); Karin Magana 5:18). Manufar wannan darasi ita ce don a tunashe ku da baiwa mai tamani da Allah ya ba wa krista ma'aurata da kuma dama na hidima tare a matsayin ma'aurata a kalkashin ikon Almasihu.

**Magada Tare cikin Kauna**. Kowane maidiga krista an umurce shi da ya kaunaci matar sa sosai, duka da kuma ta hadaya. (Karanta Afisawa 5:25-29). Kowace macen Krista an umurce ta da ta kaunaci maigidanta a kullayome, ta yin biyayya da kuma dukan zuciya. (Karanta Titus 2:4-5). Kamar masu karbar kaunar Allah a cikin Almasihu, mu yi tarayya cikin wannan kauna da mata/mazan mu a cikin aure. Wane babban dama ne muke da shi da zamu bayar mu kuma karbi shayarwa na baiwar rayuwar kauna. Akwai abubuwa kalilan da suka fi raunanawa shi ne aure da babu kauna. A tattaunawa, akwai abubuwa kalilan da ta fi kosarwa shi ne kauna da ta cika auren (aure da ke cike da kauna). Yesu ya dokaci almajiransa su kaunaci juna kamar yadda ya kaunace su. (Karanta Yahaya 13:34-

**Har nan gaba su zama ba jiki biyu ba ne, daya ne. Abin da Allah fa ya gama, kada mutum ya raba.**
**Matiyu 19:6**



LifeBook_Volume_3.indd 34 8/24/15 11:15 AM

> **Haka kuma, ku maza, ku yi zaman da'a da matanku, kuna girmama su, da yake Su ne raunana, gama ku abokan tarayya ne na Allah. Ku yi haka don kada wani abu ya hana ku yin addu'a tare.**
> **1 Bitrus 3:7**

35). Wancan doka tana aiki akan dukkan mu wadanda suka yi aure ma. Yayen da muka yi biyayya da wannan doka (umurni) mun kafa muhalli inda za a kosar (shayar) da mu kuma mu ji dadi ta hanyayi masu ban al'ajibi.

**Magada Tare cikin Girmamawa (martabawa).** Bulus da Bitrus sun fada mana cewa mazaje da mataye su girmama su kuma martaba (yi biyayya wa) juna. (Karanta Afisawa 5:22-29; 1 Bitrus 3:1-7). A darajanta wani ana nufin ka bashi babban cancanta da daraja ga wannan mutum. Ka rike (ajiye) shi ka kuma nuna masa yadda kake gode wa Allah da ya bada shi a gare ka. Kowane mutane ma'aurata suna da zarafi mai banmamaki don zama ma'aikata na daraja ga juna. Ma'aurata a cikin hidimar shugabanci suna da iyawa don karfafa juna da kuma taimakon juna don su ji karfin gwiwa a cikin kiran sa/ta. Tana da muhimmanci sosai mu furta kalmomi na girmamawa da kuma darajantawa wa juna a kullum. Zata gina abokan tarayyar mu, ta kawata mika kansu don daukakar Allah da baye bayen da Ya ba su. Yayen da muke girmama juna muna kuma darajan juna, muna girmama Allah wanda ya hallice mu a matsayin kayan aiki masu daraja a cikin Almasihu. (Karanta Afisawa 4:29; 1 Tassalonikawa 4:4)

**Magada Tare cikin Alheri na Rayuwa.** Bitrus ya fada mana cewa mazaje da kuma mataye daya suke a wajen karban farin ciki, jinkai da kuma cikaken rayuwa na Allah a cikin Yesu (Karanta 1 Bitrus 3:1-7). Auren mu ya kamata ta bayyana albarka na hakika. A kalkashin ikon Almasihu aurenmu za ta iya cika da farin ciki, jinkai ta kuma cikawa na Ruhu. Gidajen mu zata iya zama wurare na ruhaniya mai zurfi in da rayuwa na Almasihu take a yalwace. Za mu iya hidimta alherin



LifeBook_Volume_3.indd 35 8/24/15 11:15 AM

rayuwar Allah ga juna kowace rana. Ku yi addu'a da juna da kuma domin juna kowace rana. Ku bar Ruhu Mai Tsarki ya yi anfani da mu don tabbatar da muryar annabci wa matarka/mijinki. Yayen da muke furta kalmomin ginawa, gargadi, da kuma ta'azantawa ga matayenmu mun mayar tabbatarwa da kuma karfafawa a gare su. (Karanta 1 Korontiyawa 14:3). Mune magudana na kowace rai (rayuwa) na Allah ga duk wanda ya ke jin mu. Bari wannan gudanar rayuwa ta fara da daraja ga wanda muka aura.

**Magada Tare cikin Albarka.** Bitrus ya kuma ce zarafi ne ga dukkan masu bi, hade da ma'aurata, su gaji albarka. (Karanta 1 Bitrus 3:8-9). Don a albarkatar tana nufin "samun jinkai, a bayar hannu sake, ko a sa murna." Wannan shi ne yadda Allah yake albarkatan mu kuma shi ne yadda za mu albarkaci juna. A matsayin miji da mace ya kamata mu mai da hankali akan albarkatan juna. Mu albarkace su da Magana da kuma aikatawa. Ka nuna jin kai ga matarka. Ka zama da kauna da juna. Ku ba da kyautai wa juna a kullum. Wannan ba sai an kashe kudi mai yaw aba; halin bayarwa da kuma karba yana sa yadda Allah ya tsara kewayen albarka cikin tafiya. Bari mu hurta kalmomin albarka a cikin sunan Yesu. Zai martaba wannan ya kuma arzuta auren mu saboda muna neman mu albarkaci abokan tarayyan mu cikin kauna da kuma rayuwa.

**Magada Tare cikin shakuwa.** Shirin Allah tun da farko shi ne domin namiji da mace cikin aure su zama aminai ta gaskiya. (karanta Farawa 2:23-25). Bisa ga Manzo Bulus kauna, girmamawa, da kuma shakuwa (amini) na ma'aurata hoto ne na kauna kuma shakuwa marar yankewa na Almasihu da kuma ikkilsiya. (Karanta 5:30-32). Shakuwa (amini) da matarka ya zama a mataki na: jiki, motsa rai, da kuma ruhaniya. Ya zama akwai shakuwa ta ruhaniya, a bidi fuskar Allah da gaskiya tare cikin addu'a da kuma a bude ta shaida maganar Allah da juna. Ya zama akwai shakuwa na motsa rai, sadarwa da juna ta yin gaskiya, la'akari, da kuma kauna. Ya zama akwai shukawa ta jiki, cika shirin Allah domin ma'aurata don su ji dadin cika yin jima'i a cikin kariya da kuma tsarkakiyar hadi na auren krista. Idan auren mu suna sadar da kaunar Kristi da kuma ikkilisiya (amaryar Sa) ga duniya, dole mu zauna cikin zurfi da kuma zama cikin shakuwa. Wannan zai kawo farin ciki sosai a gare mu, tsaro ga 'ya'yan mu, da kuma albarka ga juna.



LifeBook_Volume_3.indd 36 8/24/15 11:15 AM

**Magada Tare cikin bada 'ya'ya (hayayyafa).** Dokar halita da Allah ya ba wa Adamu da Hawa'u ita ce su "Hayayyafa su kuma mamaye" (Karanta Farawa 1:26-28). Nufin Allah domin ma'aurata su dandana rayuwa tare na hayayyafa. Wannan, hakika, ta hada da albarkan 'ya'ya da dayantaka zai kawo. (Karanta Zabura 127:3-5). Amma ta hada da 'ya'yan dayantaka ta "ruhaniya". Mu zama kungiya ta hidima, ta yin anfani da tasiri na rayuwar tarayya a matsayin kayan aiki na hidima mai fa'ida. Yayen da muke zama cikin kauna da kuma dayantuwa Allah zai yi anfani da mu a matsayin gurbi ga shakuwar kauna da kuma hadin kai a rayuwar wasu. Yesu ya kira mu mutum mutum da kuma tare don mu "je mu bada 'ya'ya". Alkawarin sa a gare mu shi ne 'ya'ya da muka bayar tare zai dawama har abada. (Karanta Yahaya 15:16-17.

**Magada Tare cikin cikawa (kammalawa).** Nufin Allah domin auren mu ya zama da farin ciki da kuma cikuwa ta ruhaniya, motsa rai, da kuma jiki. Allah ya ba mu aure a matsayin baiwarsa na alheri a wannan rayuwa. Dole mu kula da dangantaka mai tamani da kyau, don mu iya karba da kuma farin cikin cikuwa na shakuwar abokantaka da kuma tarayya da Allah ya nufa. Ku mika kai tare cewa zaku yi shagalin aboki da Allah ya ba ku kowace rana. Sa'an nan ka mika kai don bunkasa (rayar) da ire iren hidimar tarayya da matarka. Bari Allah ya yi anfani da ku tare a matsayin magudana na kaunarsa da kuma ikonsa. (Karanta Maihadishi 4:9). Yawancin ma'aurata masu hidima sun watsar da albarkan Ubangiji a cikin aure. Bari kada a fadi wannan a kanka.



LifeBook_Volume_3.indd 37 8/24/15 11:15 AM

**HADDACEWA:**

Haka kuma, ku maza, ku yi zaman da'a da matanku, kuna girmama su, da yake su ne raunana, gama ku abokan tarayya ne na Allah. Ku yi haka don kada wani abu ya hana ku yin addu'a tare. 1 Bitrus 3:7

**KWAKWARA (ASALIN) GASKIYA**

Allah ya kira ka da kuma matarka don zama abokan tarayya na rayuwa ta hanyoyi iri iri wadanda suke hidimta wa Allah ta wurin Yesu Almasihu tare yayen da suke dandana rayuwar aure da ke cike da albarku na zama "magada tare" na alherin Allah.

**MARTANIN KA (AMSAR KA)**

- Ka zauna da matarka ku kuma auna karfi da kuma kasawa na auren ku. Ku hadu da ma'aurata da karfin su ta fi naku, ku fadi zuciyarku ku kuma bari su baku sharawa su kuma yi addu'a tare da ku.

- Ka sami lokaci don zama a kadaice, ku biyu kawai, ku kuma sake tabbatar da mika kanku don kaunar juna sosai ku kuma hidimta wa Ubangiji tare da aminci.
- Idan baku yi haka tukuna ba, ku bi cikin wannan darasi tare a matsayin masu aure.

**LITTAFIN RAI**

**Rubutu**



LifeBook_Volume_3.indd 38 8/24/15 11:15 AM

MAKO 39

# Nazari (Bincike) da kuma Wa'azin Maganar Allah

**Karanta Joshuwa 1:8; Ishaya 40:8; Irimiya 23:29; 2 Timoti 3:16.**

Wanne littafi ne da an fi sayarwa mafi kyau nesa ba kusa ba shekara da shekaru? Wanne littafi ne a ka fassara ta zuwa yaruruka da yawa fiye da kowace littafi? Wane littafi ne take da ikon sawaya rayuwa? Amsar, hakika, ita ce Littafi Mai Tsarki. Littafi Mai Tsarki na dauke da litattafai 66 da aka rubuta ta wurin marubuta 40 a tsawon kimanin shekaru 1500.

Littafi Mai Tsarki ita ce asalin Maganar Allah. Simamme ne daga gare shi kuma hurare ne daga gare shi. (Karanta 2 Timoti 3:16). Nassi ta bayyana kaunar Allah marar karewa wanda yake mika hannun sa na alheri zuwa ga halitta mai tawaye da ke tasowa zuwa ga hallaka. Allah ya kawo dauki ta wurin mika Dansa ya kuma bude kofa domin yan adam da ke bare (ware) don su sulhuntu a gare shi. Igiyar Kalle na fansa an tuka ta a cikin Littafi Mai Tsarki a matsayin shugaban take. Littafi Mai Tsarki na dauke da dukkan manyan labaru na kauna.

Ta wurin rubutaccen Maganar Allah ne aka gabatar da mu ga rayayyen Kalma, Yesu Almasihu. Littafi Mai Tsarki an tsara ta daga Allah don a kawo mu zuwa gare shi. Littafi Mai Tsarki kuma ajiyayyen kalmomi da kuma koyarwa ne na Mai ceto. Bulus ya yaba wa Timoti *"da kuma yadda tun*

**Maganata kamar wuta ce, kamar guduma mai farfashe dutse. Ni Ubangiji na fada.**
**Irimiya 23:29.**

**Ka yi wa'azin Maganar Allah, ka Dimanta a kai ko da yaushe, kana shawo kan mutane, kana tsawatarwa, kana karfafa zukata, a game da matukar hakuri da kuma koyarwa.**

**2 Timoti 4:2**

*kana dan karamin yaro ka san Litattafai masu tsarki, wadanda suke koya maka hanyar samun ceto ta dalilin bangaskiya ga Almasihu Yesu" (2 Timoti 3:15).*

Littafi Mai Tsarki ta tanadi dabi,a da kuma tushen da'a ta inda mutane da kuma kasashe za su iya yin nasara su kuma zauna cikin salama. Loren Cunningham, wanda ya kafa Matasa Da Aikin Bishara (Youth With A Mission), ya bayyana: "a cikin dukan tarihi, kundin a fili yake: yayen da sarkakiyar taruwa na jama'a suna da Littafi Mai Tsarki kuma suna aikata abin da take koyarwa a cikin rayuwarsu, kasa ya samu sawayawa." Babu abin da ya fi arzuta rayuwar mu kamar sanin Allah da kuma Maganar Sa.

## Binciken (Nazarin) Maganar Allah

Karatu, bincike, da kuma tunani akan Nassi kowace rana ya zama alama na kowane shugaba krista. Bari Allah ya yi maka Magana ta wurin maganar sa. Sa'an nan, lokacin da ka yi wa'azi, ka fada wa mutane abin da Ya dace. (Karanta 2 Timoti 2:15). Ga wasu shawarwari domin samun cikakken fahimta na babban littafi da aka taba rubutawa.

1. **Ka nemi naka salon nazarin Littafi mai tsarki**. Za ka iya karanata cikin Littafi Mai Tsarki kowace shekara ta wurin karanta surori uku kowace rana da kuma surori biyar kowace Lahadi. Wata hanyar nazarin Littafi mai Tsarki ita ce ta wurin bada hankalin ka ga Littafi dabam na Littafi Mai Tsarki kowace mako. Har yanzu wata hanyar don binciken Littafi Mai Tsarki ita ce ka karanta shafi na Nassi a lokaci guda. Masu bincike sun karfafa nazarin maganar Allah da kuzari tun da aka haifi wannan ma'aikata a 1940s. sun ba da shawar salon



LifeBook_Volume_3.indd 40 8/24/15 11:15 AM

"ZAMUS (SPECK)" na binciken shafin Nassi. A kowace shafi na Nassi a duba ga:

**Z**unubai da za a kauce wa
**A**lkawarai don a amsa
**M**isalai da za a bi
**U**murnai da za a yi biyayya
**S**anin (Ilimin) Allah.

Tana da azanci, ko menene salon ka na nazarin Littafi mai Tsarki, ka yi ta karanta maganar Yesu kowace rana kamar yadda aka rubuta a cikin Bisharu guda hudu. Su "ruhu ne kuma raia ne". (Karanta Yahaya 6:33). Alherin maganar Sa ta "zauna a yalwace a cikin mu." (Karanta Kolosiyawa 3:16).

2. **Ka karanta Maganara Allah daidai (yadda ta dace).** Wasu mutane sun same ta da taimako a karanta Littafi Mai Tsarki a cikin yanayi na addu'a, akan gwiwar su. Ka roki Allah domin wahayi da kuma hanya (inda za a bi). (Karanta Zabura 119:18). Ya kamata mu kaunaci maganar Allah saboda bunkasar (fadadar) zuciyar Sa ne da kuma halin sa. Mai ilimin falfasa, Blaise Pascal, ya lura cewa, "sanin dan adam dole ta zama an fahimta ta wurin kauna, amma sanin mai iko duka dole ta zama kauna don a fahimce ta."

3. **Ka saurari umurnin Magana daga Ruhu Mai Tsarki**. Rhema kalman Helenanci ne ma'ana "hurci". Yayen da Ruhu Mai Tsarki ya kawo aya ko shafi zuwa hankalinmu da aikatawa ga yanayi na yanzu ko bukatar hanya, wannan it ace Kalmar rhema daga wurin Ubangiji. Wadannan sune lokuta masu banmamaki yayen da Ruhun Allah ya dauki logos (rubutaccen Maganar Allah) ya sa ta zama don kanka a cikin wahayi ko aikatawa. A wannan littafi, Asiri na Mai Jagora. F.B. Meyer ya rubuta, "Maganar igiyar wuta ce tare wanda muryar Allah hakika zai tafo (zo) wurin ka idan zuciya ta yi tsit kuma an sa hankali."



LifeBook_Volume_3.indd 41 8/24/15 11:15 AM

4. **Ka yi anfani da dukkan juyi da ke akwai.** Wasu masanan Littafi Mai Tsarki za su iya karanta Tsohon Alkawari a Ibrananci da kuma Sabon Alkawari a asalin Helenanci. Ga yawancin mu, karanta Littafi Mai Tsarki a juyi fiye da daya zai tanada fahimta dalla dalla na abin da marubutan Littafi Mai Tsarki ke kokarin fadi.

5. **Ka Haddace Nassi.** Jan Nassi tana baka babban iko a yin wa'azi. A matsayin masu hidima na Sabon Alkawari, ba a bamu iko don mu dauki ra'ayinmu ba; an ba mu iko kadai don mu shaida Maganar Allah. (Karanta Zabura 119:11).

6. **Yin Biyayya da Maganar Allah za ta cika rayuwarka da albarku da kuma nasara**. Yayen da muka furta maganar Allah, yi tunani akan maganar A;llah, sa'an nan muka yi biyayya da Maganar Allah yayi alkawari zai wadata mu ya kuma ba mu nasara. (Karanta Joshuwa 1:8).

**Wa'azin Maganar Allah**

Babban mai wa'azi na karni na sha tara, Charles Spurgeon, an tambaye shi idan zai kare Littafi Mai Tsarki, "Kare Littafi Mai Tsarki?" ya yi dariya. "Wannan zai zama kamar kare zaki ne. Zan bari ta kwance ta kuma kare kanta." Ba mu zo ga sanin cewa Littafi Mai Tsarki tunanin dan dama kawai ba. Sai dai, idan mun mika kanmu ga biyayya wa Almasihu, Zai bayyana a gare zahirin Maganar Sa. (Karanta Yahaya 7:17)

Ga yawancin fastoci, tsakiyar maganar su ita ce yin wa'azi. Yayen da ka shaida gaskiya ka sammanci ikon Magana na Allah ta yi aikin ta. Da farko, Allah yana zance da kai ta wurin addu'ar ka da kuma karatun maganarsa. Sa'an nan, Allah yana Magana ta wurin ka. Bari maganar Allah ta cika zuciyarka da kuma lamirinka a cikin makon. Sa'an nan ka yi wa'azin babu kakautawa.

Fastoci suna bukatan ciyarwa daga misalan labaru na Tsohon Alkawari, umurni mai sauki na Bisharu, da kuma matsayi na ikkilisiyar yankuna na Wasiku cikin jama'arsu. Hakinka ne kai fasto ka mika (bayar) wa jama'ar ka "dukan shawarar



LifeBook_Volume_3.indd 42 8/24/15 11:15 AM

Allah". (Karanta Ayukan Manzanni 20:27.) Ga wasu shawarwari domin sa wa'azinka ta zama da Karin anfani.

1. **Ka yi addu'a kafin ka yi wa'azi**. Ka tabbatar babu wani zunubi da baka furta ba a rayuwarka. (Karanta 1 Yahaya 1:9). Ka roki Ruihu Mai Tsarki ya cika ka ya kuma shafe (kebe) w'azin maganar Allah. (Karanta Afisawa 5:18). Kafin babban aikin wa'azi Yesu ya dauki lokaci mai tsawo yana addu'a. ya kamata mu bi misalign Ubangijinmu. (Karanta Markus 1:35-38).

2. **Ka yi wa'azin Maganar Allah wa Mutane**. Da farko, bari Allah ya yi Magana da kai ta wurin karatun Maganar Sa a dukkan mako. Sa'an nan, bari Allah ya yi Magana ta wurin ka. Ka fada wa mutane abin da Allah ya fada maka.

3. **Ka zama da karfin hali cikin iko na wa'azin Maganar Allah**. Allah yana anfani da abin da marasa bi suke dauka "wautancin wa'azi" don ya sawaya rayuka. (Karanta 1 Korontiyawa 1:21). Ruhu Mai Tsarki yakan yi anfani da maganar da aka yi wa'azi don ya kawo shankai (shawo kai), ta'aziya, da kuma warkaswa. (Karanta Ishaya 55:11; Ibraniyawa 4:12). A cikin littafin sa, Yesu, Shugaban Bangaskiyar mu, A.W. Tozer ya rubuta cewa, "Maganar Allah magani ne da take nema ta kuma hallakar da cututuka da zata haddabi rayuwar ikkilisiya."

4. **Ka yi aminci ga aya**. Allah bai baka iko ka "rike maganar Allah da yaudara ba." (Karanta 2 Korontiyawa 4:2). Kada ka yi wa'azin naka ra'ayi ka kuma mari ayar Littafi Mai Tsarki akan naka ra'ayi. Sai dai, ka bude shafufukan Nassi da Ruhu Mai Tsarki ya umurce ka don ka fade ta. (Karanta 2 Timoti 4:1-2).

5. **Ka tabbatar sakon tana da bayyananen kai hankali**. Ka bayyana tushen gaskiya na shafin. (Karanta 1 Korontiyawa 14:8). Wani ya bada shawara cewa salo mai kyau domin yin wa'azi ita ce, "bayani, kwatanci, aiwatarwa." Yin



LifeBook_Volume_3.indd 43 8/24/15 11:15 AM

anfani da sauran labaru na Littafi Mai Tsarki ita ce hanya mafi kyau don kwantata gaskiya. Wadannan labaru sun tanadi sanin Littafi Mai Tsarki kuma sun yi daidai kuma fahimtattu ne a kowace al'ada.

6. **Ka bada matakai a aikace na aiki da ta fito daga shafin**. A kullum ka tyi wa'azi da duban canza lamiri, zukata da kuma ayuka. Babban mai wa'azi na karni na hudu, Chrysostom, ya ce, "Alama na babban mai wa'azi ba shi ne mutane su fita suna cewa, 'wane irin babban mai wa'azi haka.' Amma mamakon haka su ce, 'zan yi wani abu."

7. **Ka yi addu'a bayan ka yi wa'azi, ka miaka hdimar maganar Allah**. Ka baga gaskiya cewa iri mai kyau na Maganar Allah zata bada 'ya'ya da yawa. (Karanta Ishaya 55:11; Luka 8:11,15; 1 Bitrus 1:23).

   Kome wuyar yanayin ka na hidima zata zama, ka ci gaba da wa'azin Maganar Allah. Maganar Allah zata farfasa dutse mai tauri. (Karanta Irimiya 23:29).

Wani babban hamayya na addini cewar a fahimci gaskiyar littafi da suke dauka da tsarki dole ka karanta ta a cikin asalin yaren (harshen) wanda aka rubuta ta. Amma a matsayin krista muna cewa, "A Fassara (wallafa) Littafi Mai Tsarki zuwa kowace yare (harshe) a duniya kuma ba zaka rasa wani abu ba!" Wannan ita ce iko na gaskiyar Maganar Allah.



LifeBook_Volume_3.indd 44 8/24/15 11:15 AM

**HADDACEWA:**

Hakika ciyawa takan bushe, furanni kuwa su yi yaushi, Amma maganar Allah ba za ta taba faduwa ba. Ishaya 40:8

**KWAKWARA (ASALIN) GASKIYA**

"Bari Littafi Mai Tsarki ta cika tunani, ta yi mulkin zuciya, ta kuma jagoranci kafafu. (Henrietta Mears)

**MARTANIN KA (AMSAR KA)**

- Ka mika kanka ga salon, binciken Littafi Mai Tsarki kowace rana, farawa daga yau.
- Ka mika kai ka yi aminci na shaida Maganar Allah da duban kawo masu sauraronka ga girma (balaga) cikin Almasihu. (Karanta Kolosiyawa 2:27-28).

## LITTAFIN RAI

### Rubutu



LifeBook_Volume_3.indd 45 8/24/15 11:15 AM

MAKO 40

# Shaida Bishara (Shelar Bishara)

**Karanta Matiyu 4:19; Yahaya 4:35; Romawa 1:16; 1 Timoti 2:1-4; Wahayin Yahaya 22:17**

Kafin Yesu ya h aura zuwa sama Ya umurci mabiyansa su shaida Albishir Mai Dadi game da Shi ga kowane mutum a duniya. (karanta Markus 16:15). Albarka ce mai girma da kuma daukan nawaya na kowane mai bin Almasihu da aka maye haifuwarsa ya shaida wannan Albishir Mai Dadi na ceto na Yesu Almasihu da wasu. Yesu ya ce, wadanda suka bi shi za su zama masuntan mutane. (karanta Matiyu 4:19).

Malamin Littafi mai Tsarki Dawson Trotman ya ce, "Bambanci sakanin kama kifi da kama mutane ita ce za ka kama kifi da ke da rai sai kuma sum utu. Zaka kama mutane wadanda suke a mace ka dawo da su rayayyu (da rai)." (karanta Afisawa 2:1). A cikin kayan aikin horaswa na, Shaida Yesu ba tare da Tsoro ba daga William Fay da kuma Linda Shepherd Evans, mun sami wadannankalmomin karfafawa: "Kana so ka shaida Yesu babu tsoro? Mai yiwuwa tunanin shaida bangaskiyar ka a cikin Almasihu ya sa ka jin tsoro da kuma laifi a zuciyar ka. Ba mu bukatar mu dubi gaba fiye da farkon littafi na Sabon Alkawari don ganin cewa an umurce mu da mu shaida Albishir mai Dadi. (karanta Matiyu 28:19-20). Duk da haka, Allah ba ya nufin wannan umurni ta baka jin rashin isasshe. Maimakon haka, wannan umurni ta gwada marmarin Allah don ya hada da mu a cikin shirin sa mai banmamaki don fansar yan adam."

**Sai ya ce musu, "Ku bi ni, zan mai da ku masuntan mutane".**
**Matiyu 4:19.**

Shirin ceto tana da sauki amma sako ne mai zurfin iko na kauna da kuma yanci. Za a iya fahimtar sa a fili ta wurin kowane mutum, kuma ta zama a bayyane a kuma shaida wa kowa. Wannan darasi ta yi da yadda zaka iya shaida bishara sosai da wasu ka kuma horas da mutanen da kake shugabanta su shaida bangaskiyar su cikin Almasihu ga wasu a gefen su.

1. **Ka nemi Ubangijin Girbin.** Ka tuna, girbin ruhaniyar batattu maza da mata zuwa ga bangaskiya cikin Almasihu tana wurin Allah (na Allah) ne. (karanta Matiyu 9:37-38). Ka roki Allah ya bude maka kofa na zarafi (dama) don ka shaida bishara ga wasu. Ka duba ga "zaben mai iko duka" da Allah ya zai shirya domin ka don ka hadu da mutane da suke bukatar Yesu. Ka yi addu'a domin wadanda suke cikin dangantaka da kai. Allah yana so ya yi anfani da kai don kai bishara ga abokai, membobin iyali wadanda ba su san Yesu ba tukuna. Ka yi addu'a cewa idanun su ya budu su ga gaskiya da Yesu yake rikewa. (karanta 2 Korontiyawa 4:3-4). Ka roki Ruhu Mai Tsarki ya shawo kan mutanen da zaka shaida wan a bukatar Almasihu da suke da ita. (Karanta Yahaya 16:7-11). Ka roki Ruhu Mai Tsarki ya jawo mutane ga Uba ta wurin Gaskiyar Sa da kuma kaunarsa. (Yahaya 6:44-45). Allah zai amsa addu'ar ka saboda nufinSa ne domin mutane a ko'ina su karbi kaunar Sa da kuma gafara ta wurin bada gaskiya ga Almasihu. (Karanta 1 Timoti 2:4).

2. **Ka fara hirar (tadin): ji wannan labari, ka fadi labarin Allah, ka fadi labarin ka**. A kayan aikin bishara da ya kirkiro ana kira Gwajin Allah, Mai


LifeBook_Volume_3.indd 47 8/24/15 11:15 AM

Bishara Rice Broocks ya karfafa muhimmancin fara tadi mai ma'ana akan bada gaskiya ga Almasihu. Mutane sukan so su yi Magana a kan kansu da kuma abin da suka gaskata. Yana da muhimmanci a shagalar da su ka kuma gano wane ne su da kuma abin da suka gaskata. Ka tambayi mutumin ya fada maka wani abu a kansa, tushen sa, iyalinsa, da kuma dandana rayuwarsa. Ka tambaye shi abin da ya gaskata akan Allah, sama da kuma Yesu. Idan ya gaskata da sama ya kuma gasakata da zuwa can, ka tambaye shi me ya sa. Sa'an nan ka tambaye shi idan zai so ya san abin da Littafi Mai Tsarki ya fada akan wadannan abubuwa. Idan ya amsa da tabbaci, ka fada masa labarin Allah.

Allah ya hallici duniya da abubuwan da ke cikin ta – tsirrai da kuma dabbobi kuma, a karshe mutum. (Karanta Farawa 1:1,26-28; 2:7). Lokacin da Allah ya hallici Adamu da Hawa'u, duniya babu zunubi. Adamu da Hawa'u suna jin dadin shakuwa da Allah da kuma juna. Allah ya hallici dan adam don ya ji dadin amini, dangantaka ta kauna da Shi, da juna, da kuma dukkan halitta. Amma Adamu ya zabi ya bi nasa hanya ya kuma yi wa Allah tawaye (Farawa 2:16-17; 3:6-7). Ta wurin tawayen Adamu da Hawa'u, zunubi ya shigo duniya. Yanzu dan adam ya rabu da Allah a runahiyance. (Karanat Romawa 5:12). Amma ba wannan ne karshen labarin ba, gama Allah yana da shiri mai ban al'ajibi don kawo dan adam da ya fadi zuwa ga kansa. (Karanta Luka 1:77-79; Yahaya 3:16).

Akwai manyan abubuwan da ya faru guda uku a labarin dan adam: Halitta, Faduwa da kuma fansa. Fansa, ta wurin hadayar Almasihu akan gicciye, ita ce inda bege domin dukkan yan adam ke samuwa. (karanta Kolosiyawa 1:13-14). Abin da aka rasa ta wurin "Adamu na farko" an maido da shi ta wurin "Adamu na karshe" Yesu Almasihu – ta wurin mutuwar Sa, binnewa da kuma tashin Sa. (Karanta 1 Korontiyawa 15:45-49). Allah ya yi kaunar duniya har ya aiko Dansa, Yesu, ya zama hadaya domin zunubanmu. Yesu ya biya hukuncin mu cikakke yayen da ya mutu akan gicciye. (Karanta 1 Korontiyawa 3:13-18). Ta wurin furta zunubanmu da kuma tawayen mu ga Allah, mu bada gaskiya ga hadayar Almasihu mu kuma shaida Shi a matsayin Ubangiji, zamu tsira. (Karanta Yahaya 1:12; Romawa 10:9). Wannan shi ne labarin Allah.



LifeBook_Volume_3.indd 48 8/24/15 11:15 AM

Yanzu, ka fadi labarin ka! A matsayin mai bi, kana da shaida na alherin ceto na Allah da kuma jinkan sa a cikin rayuwarka. Yayen da ka fadi wannan labari, za ta bada shaida ga gaskiya na kaunar Sa da kuma ikon mai girma. Ka yi Magana akan manyan abubuwa da Allah ya yi maka, yake yi maka da kuma abin da ka gaskata Zai yi maka a gaba. (Karanta Zabura 126:3). Yayen da ka bada labarin Allah da kuma naka labari, zak iya gaskata Ruhu Mai Tsarki ya shawo kai ya kuma jawo mutane zuwa ga Allah. (Karanta Yahaya 16:8). Ceto aikin Allah ne. aikin ka shi ne ka shaida bishara. A zahiri, idar da bishara ya kamata a kullum ta zama fifikon mu na farko. (Karanta 1 Koromntiyawa 15:1-4).

3. **Ka shaida Nassi**. Maganar Allah zata yi ma kanta Magana, idan ka bar ta. Me ya sa ba bude Littafi Mai Tsarki kawai ka kuma sa mutumin da kake shaida masa ya karanta da murya abin da Nassi ya fad aba? Idan sabo da wasu dalilai ake gani ba ta da taimako a sa su karanta, zaka iya karanta Nassin da murya. Saboda wannan ya yi aiki, kana bukatar Littafi Mai Tsarki da kuma shjafufuwa na ceto kadan don karatu.

   Yawancin shaidu masu anfani domin bada labarin Almasihu "hanyar Roma" domin ceto: (Karanta Romawa 3:23; 5:8; 6:23; 10:9,13). Wasu shafufuka na ceto sun  hada da ayoyi na biye: (Karanta Yahaya 1:12; 3:3,16; 14:6; 2 Korontiyawa 5:15; Wahayin Yahaya 3:20). Yayen da akwai sauran Nassoshi da zaka iya yin anfani da su, wadannan zata zama da taimako.

4. **Ka hatimce Matakin (Hanyar).** Idan mutumin da kake shaida bangaskiyar ka da shi ba ya shirye don ya karbi Almasihu, kada ka karaya (kada ka yi sanyi). Ka yi abin da Allah ya kira ka don ka yi. Asalin ma'anar bishara an tanada daga Roy Fish, Farfesa na bishara na tsawon lokaci a Kudu maso Yamman Baptist Theological Seminary: "aikin Bishara jarabar shaida ce na Albishir Mai Dadi na Yesu Almasihu cikin ikon Ruhu Mai Tsarki da dukkan mutane domin manufa na bi da su ga bada gaskiya cikin Almasihu a matsayin Ubangiji da kuma Mai ceto da su kuma, zasu shaida Shi ga wasu."



LifeBook_Volume_3.indd 49 8/24/15 11:15 AM

Idan mutumin yana shirye ya karbi Almasihu, ka jagorance shi cikin addu’ar ji a zuciya inda zasu juyo daga zunubansu su kuma karbi Yesu Almasihu a matsayin mai ceton su da kuma Ubangijin su. Saukin gabatar da Bishara an tanada a mako na 1 na LittafinRayuwa.

Yayen da ka bi da wani zuwa ga Almasihu, ka taimake shi ya fara rayuwar yin addu’a, karatun Littafi Mai Tsarki da kuma zumunta da jama’ar Allah a cikin zumuntar masu bi na ikkilisiyar littafi Mai Tsarki. (dubi mako na 3 matakai na farko).

A matsayin fasto, tana da muhimmanci domin k aka zama mai bishara a cikin wa’azin ka, a bayyane a cikin gabatar da bisharar ka, kuma a bayyane cikin kiran mutane zuwa bada gaskiya ga Almasihu. Babu abin da zai iya sa farin cviki fiye da kai wani zuwa ga Almasihu. Sama tana murna yayen da wani mutum ya zo ga bangaskiya cikin almasihu. (Karanta Luka 15:7). Bari mu mika kanmu don kai m,utane da yawa ga Mai vceto mu kuma taimake su su ghirma su kai ka balaga cikin Almasihu.



LifeBook_Volume_3.indd 50 8/24/15 11:15 AM

**HADDACEWA:**

Amma za ku sami iko sa'ad da Ruhu Mai Tsarki ya sauko musu, za ku zama shaiduna a Urushalima, da duk kasar Yahudiya, da ta Samariya, har ya zuwa iyakar duniya. Ayukan Manzanni 1:8

**KWAKWARA (ASALIN) GASKIYA**

Albarkaci mai girma, dama ce, kuma nawaya ne ga kowane mai bi na Almasuhu ya shaida Albishir Mai dadi na ikon ceto na Yesu da wasu.

**MARTANIN KA (AMSAR KA)**

- Ka dauki lokaci kowace ran aka yi addu'a saboda batattu. Ka roki Allah ya yi anfani da kai don shaida bangaskiyar ka ka kuma kai wadanda basu san Almasihu bag a bada gaskiya gare Shi.
- Ka rubuta labarin ka kuma ka haddace ta don ka iya bada labarin ka da sauki da kuma da karfin gwiwa.
- Kullayomi ka horas da wasu masu bi don shaida bangaskiyar su cikin almasihu da kyau. (dubi mako na 1).

## Rubutu



LifeBook_Volume_3.indd 51 8/24/15 11:15 AM

# Kula da (samar da Kudin) Hange (Wahayi) a Lokuta na Kalubala

**Karanta Luka 6:38; 2 Korontiyawa 9:6-11; Filibiyawa 4:19.**

A yau kasashe da yawa suna kan karayar tattalin arziki. A sakamakon haka, ikkilsiyu da kuma ma'aikatu da yawa suna gwagwarmaya don su sami isasshen kudi da zasu ci gaba da aikin hange da Allah ya ba su. Duk da haka Allah ya ci gaba da bada wahayi mai girma. Ta yaya, a wadannan lokuta, za mu iya tanadar kudi na hangen da ke a zuciyar mu?

Wata labari a Tsohon Alkawari ta tanadi muhimman ka'idodi domin samun kudin wahayi, ko ma a lokuta na tattalin arziki mawuyaci. (Karanta 2 Sarakuna 4:1-7). Akwai ka'idodi a wannan ayar da ta bamu basira akan yadda za mu sami kudin hangen mu, ta wurin tanadin al'abiji na Allah, ko da ma a mauyacin yahayi na tattalin arziki ne.

1. **Ka dauki kasafion kadarorin ka**. Elisha ya tambayi matar. *"Menene kike da shi a gidan ki"?* (2 Sarakuna 4:2). Ta wannan hanya, dole ka tambai kanka, "Menene kake da ita a gidan ka"? Menene kadarori da kake da su a yanzu? Kadarorin ka zai iya hadawa da abokanai, iyawarka, dangantakar ka, lafiyar ka, ra'ayoyin ka, da kuma baye baye ta ruhaniya, da kuma kudi.

**Kawo lissafin wakilcinka, don ba sauran ka zama wakilina.
Luka 16:2.**

2. **Ka fadada aikin ka (hidimar ka).** Annabin ya fada wa matar *"Ki je ki roki tanduna daga ko'ina… kada kin emo kadan"* (2 Sarakuna 4:3). Mu ma ya kamata mu nemi hanyoyi da za mu fadada ma'aikata (hidimar) da Allah ya sa a kalkashin kulawarmu. Ya zama dole ga matar ta hada da wasu mutane domin ta iya karbar tanadi na ban al'ajibi. Haka mu ma dole mu hada da wasu a cikin hange mu kuma jawo daga kadarorin mu. Zaku samu cewa yawancin mutane zasu bari ka "karbi aron tandunan su" don ganin hangen ka ta cika (ta kammalu).

3. **Ka saki "yaran ka" a cikin hidimar (cikin aiki).** "*ke da yaran ki*" (2 Sarakuna 4:4). Akwai yara na ruhaniya "yara maza da mata" Allah yana marmarin ya ba ka. Tana da muhimmanci ka gaiyace su don su yi aiki tare da kai a cikin "zuba" tanadin Allah. (Karanta Ishaya 60:4)

4. **Ka zuba daga abin da kake da shi**. Elisha ya umurce ta "*ku zuba man a cikin tandunan*" (2 Sarakuna 4:4). Matar ba ta yi tunanin tana da shi da yaw aba, amma sa'ad da ta fara bayarwa daga kadan da take da shi, ta dandana tanadi na al'ajibi. Ta wannan hanya, yayen da ka inganta kayan aikin ka da kake da shi yanzu Allah zai yalwata ka da tanadi.

5. **Ka ci gaba da kawo sabobin tanduna**. Sai ta ce wa yaron ta, "*Ka kawo mini wata tandun*" (2 Sarakuna



LifeBook_Volume_3.indd 53 8/24/15 11:15 AM

4:6). Abin takaicin, yaron ya ce babu sauran tanduna wanda za su zuba al'ajibin Allah. Abin a fili take: muddin a kwai "tanduna da babu kome a ciki" – mutanen da ke cikin bukatar tanadi na al'ajibi na Allah – tanadin al'ajibin tana ci gaba da gudana. Duk da haka, idan muna tunanin muna da shi da yawa – idan ta ishemu da yawan abin da muke d shi yanzu, gudanar tanadi na Allah zai dauke. Tana da muhimmanci mu lura cewa matar ne da yaronta, ba Allah ba, wadanda suka kudurta dukan yawan da kuma lokaci na al'ajibi. Muddin akwai tanduna da yawa akwai Karin al'ajibai! Ci gaba da kawo sabobin mutane – tanduna da babu kome a ciki.

Menene kake da shi – a yanzu haka – a gidan ka? Ka da yaya ne bukatar ka ta zama, kana da wasu kaya yanzu haka da zaka iya inganta ma'aikatan ka. Yayen da ka yi shi, al'ajibin zai fara. Don haka, ka nemi hanya, kowace rana, don ka bada wani abu wa Allah da kuma wani abu wa mutane.

A matsayin ma'aikatai (masu hidima) kada mu yarda kama mu a tarkon son kudi. (Karanta 1 Timoti 6:10). Duk da haka, a matsayin masu kula wadanda suke so su daukaka Allah, dole mu mai da hankali ga kudi da kuma anfaninta ga duk babban kyaun ta da kuma babban muni (muguntar) ta. Menene matakai da zaka dauka faraway daga yau don karban kudaden da ya wajaba don ka rike wahayin da Allah ya ba ka?

- *Ka fahimci muhimmancin kudi*. Wata rana zamu tsaya a gaban Ubangiji mu kumam ba da lissafi na abin da muka rike. (Karanta Luka 16:2; 2 Korontiyawa 5:10). Harold Myra da Marshall Shelly, mataimaka na tsawon lokaci na Bill Graham sun rubuta, "yawancin fastoci – ko marubuta ko manazarta ko makida da wakoki – sun nutse a cikin hikimar su da kuma ayukansu, ba su tunani da yawa akan yiwuwar tsari da ya dace. Wadannan kalilan ne wadanda suka yi lissafin fadada tasirin su."



LifeBook_Volume_3.indd 54 8/24/15 11:15 AM

- *Ka shugabantar ta wurin zama misali (gurbi).* Ikkilisiyarku suna kallon ka, kuma a kullum suna koyi da kai (kwaikwayon ka). (Karanta 1 Bitrus 5:2-3). Idan ka bar kwaryan karban baiko ta wuce ba tare da ka ba da kome ba, mutane suna gani. (littafi Mai Tsarki ta gargade mu game da bayarwa da za a gani ko a yaba. (Karanta Matiyu 6:3-4). Duk da haka, zuciyar karamci ba zata boyu ba. (Karanata Matiyu 5:14-16).
- *Ka koyar da abin da Littafi Mai Tsarki ya fada akan bayarwa*. Yesu ya koyar sha'anin kudi da kuma yadda za a yi anfani da ita. Idan Yesu ya koyar da wannan darasi tana da muhimmanci ga almajiransa, haka mu ma. A matsayin fastoci, hakin mu ne mu ba wa mutanen mu dukan umurnin Allah. (Karanta Ayukan Manzanni 20:27).
- *Ka tabbatar wa taruwar jama'ar ka alkawarin Allah ga wadanda suka bayar.* (Karanta Luka 6:38). Allah bai hyi alkawarin iri ga wadanda suke da nufi mai kyau ba: Ya ba da iri ga masu shuka. (Karanta 2 Korontiyawa 9:10). Alkawari na banmamaki da cewa Allah zai tanada dukkan bukatun mu an rubuta wa ikkilisiya wanda ya ba wa Bulus domin hidimar san a aikin bishara. (Karanta Filibiyawa 4:19).

Fa'ida na gaba domin tanadi na al'ajibi tuntuni tana "gidan ka!" Yanzu haka kana da kadara da ke ba ta aiki da zaka iya ingantawa. Yayen da ka fara zubawa daga abin da tane nan tuntuni a cikin gidan ka, Allah zai kawo tanadi na al'ajibi.



LifeBook_Volume_3.indd 55 8/24/15 11:15 AM

**HADDACEWA:**

Ku bayar, ku ma sai a ba ku mudu a cike, a dankare, har ya yi tozo, har yana zuba, za a juye muku a hannun riga. Mudun da kuka auna, da shi za a auna muku. Luka 6:38.

**KWAKWARA (ASALIN) GASKIYA**

Ka dauki kasafin abin da Allah ya ba ka tuntuni. Kana da al'ajibi tuntuni a cikin gidanka!

**MARTANIN KA (AMSAR KA)**

- Ka kudurta abin da kake da shi a matsayin kadarori ka kuma sa su cikin aiki domin dalilin Almasihu.
- Ka sa gurbi (misali) na bayarwa a matsayin salon rayuwarka.
- Ka yi shiri don koya wa iyalin ikkilsiyar ka abin da Littafi Mai Tsarki ya fada akan daukaka na Almasihu na wakilci da kuma anfanin ta.



## Rubutu



LifeBook_Volume_3.indd 56 8/24/15 11:15 AM

MAKO 42

# Bada 'Ya'ya da Yawa

## Karanta Yahaya 15:4-5,8.

Abin buga Tenis tana da asalin wuri inda karfin ka da kuma abin bugawa zasu hadu da karfi. Abin buka kurket tana da asalin wuri inda nauyin jikin ka da kuma abin bugawan zai hadu domin bugawa da kyau. Masu wasa suna kwatanta ta da "wuri mai dadi." Ita ce wuri na fadada anfani. Yan wasu sun koyi yadda zasu saukaka karfin su domin fadada shafa ta wurin hadewa da kwallo a wurin da ya dace akan bugawar sa.

Ta wannan hanya haka, za ka iya "yin wasa ga karfin ka" yayen da takamaiman bangarori suka hadu. Tare sukan hada "wuri mai dadi) na ka na aiki (na hidima). Yayen da kake hadewa a wancan wuri mai dadi a cikin hidimar ka, babu abu mafi biyewa. Za ka san ta, da kuma wadanda suke zuba maka ido ga shugabanci za su san ta.

Wuri mai dadi na hidimarka ita ce inda za ka dandana ba da 'ya'ya mai girma kuma mafi biyewa na goyon bayan ka. Sakamakon za ta zama wasu gudanarwan mulki a gida na gaske.

Amma ta yaya zaka hade a wuri mai dadi a cikin hdimar ka? Da farko dole ka gano bangarori biyar da suka hadu don su zama wuri mai dadi na hdimar ka. Wadannan bangarori su ne:

**Yadda ake daukaka Ubana ke nan, in kuna 'ya'ya da yawa, ta haka kuma kuke tabbata almajiraina. Yahaya 15:8.**



LifeBook_Volume_3.indd 57 8/24/15 11:15 AM

**Ba kyakkyawan itace da yake haifar munanan 'ya'ya, ba kuma Mummunar itace da yake haifar Kyawawan 'ya'ya. Luka 6:43**

1. **Kebewa (shafewa).** Kebewa ta fi sauki a kwatanta da a ba da ma'anar. Hakika, kebewa Ruhu mai Tsarki ne da ya ingantu a cikin ka a wuri na musamman na hidima. Kebewa ta na sakar da gaibi. Yayen da kake hidimtawa a kalkashin kebewa, kome mai yiwuwa ne.

Wasu tashar jirage suna yin anfani da abin da wasu suke kira "Damara na rike (daukan) mutane." Yayen da kake tafiya akan wannan damarar injin, ko da yake baka sa wani karfi a fili, kana dai ci gaba ne da sauri. Kana da tunanin cewa an dauke ka tare ta wurin karfi da ya fi naka. Shafewar Ruhu Mai Tsarki tana kamar tafiya ne akan damarar dauka (Rikewa) ne. akwai karfi mai tsarki a cikin dukkan abin da kake yi. Yayen da ka hidimta a cikin iko na kebewar ka, akwai tabbacin sakewa a cikin abin da kake yi. Ko da yake za ka ji gajiya a cikin jiki, akwai kuma ginuwa a ciki ko lokacin da kake hidimtawa. Kebewa na aiki ingantawa ne da kuma kammalawa.

A cikin Littafi Mai Tsarki, annabawa ko firistoci a kullum suna kebe (shafe) mutane saboda aiki na musamman ta wurin shafe kansu da mai, irin na Ruhu Mai Tsarki. (Karanta Zabura 89:20). Yayen da aka kebe ka, alherin Allah na iyarwa tana aiki iri iri. Wannan kebewa na Ruhu zai iyar da kai ka cika kiran ka, aikin da aka baka a rayuwa. Akwai wuri na kebewa na dabam ga kowane mai bi. Wasu zahirin kebewa ne saboda kasuwanci. Wasu an kebe su cikin Bishara, gudanarwa, koyarwa ko warkarwa. Masu bi kalilan ne aka kebe su domin dukan abubuwa na bisa, da kuma sauran su. A



LifeBook_Volume_3.indd 58 8/24/15 11:15 AM

kalkashin kebewar Ruhu, baye bayen na ruhu sukan yi aiki da sauki. Wannan ta kai mu ga bangare na wuri mai dadi na biyu.

2. **Baye baye**. Lokacin da Ruhu Mai Tsarki ya sauko akan masu bi a cikin Almasihu, Ya zao yana bada baye baye. (Karanta Romawa 12:6-8; 1 Korontiyawa 12:7-10; Afisawa 4:11). Akwai wasu baye baye ta musamman da suka mamye cikin rayuwarka. Wadannan baye baye da suka mamayu an bayar domin a shiryar da kai saboda kira da dabam na Allah a cikin rayuwar ka da kuma domin hayayyafar hidimar. (Karanta 1 Korontiyawa 12:11). Amma bai baye na ruhu za ta iya lalacewa ta wurin kin yin aiki (anfani), ko yayen da ka dogara akan salo da ta gabata (na baya) maimakon la'akari da aikin Ruhun Allah a yanzu. Shi ya sa Bulus ya roki Timoti, "Ka iza baiwar Allah wanda ke a cikin ka" (2 Timoti 1:6). Yayen da aka farfado da baiwar ruhu an kuma yi aiki (hidimta) a cikin kebewar ruhu, kana samun wuri mai dadi ke nan.

3. **Iyawa**. Ko da ma wadanda ba su san Almasihu ba a kullum a na cika su iyawa. Halin iyawa ba baye bayen ruhu ba ne amma kusan a kullum suna darajanta juna (suna aiki tare). Iya yin Magana sosai yana tafiya daidai da baiwar ruhu na gargadi. Marmarin yi bincike da kuma nazari tana hade da baiwar ruhu na koyarwa. A tunanin yin adalci da kuma rashin adalci za a iya hadawa da baiwar ruhu na annabci. La'akari (lura) da shan wuya a kullum yana daidai da baiwar ruhu na tausayi. Halin ingancin shigabanci zai iya tafiya da baiwar ruhu na shugabanci.

 Allah ya albarkace ka da wasu halin iyawa, amma muna bukatar taimako na wasu a bangarori inda ba mu da karfi. Wasu fastoci suna da kyau a kirkirawa da kuma rike yanar gizon ikkilsiyun su. Wasun mu muna bukatar taimako a waje. Wasu fastoci suna da karfi a bada shawara: wasu suna samin ta da gajiyarwa. Shi ya sa bunkasa kungiyar hidima ta na da muhimmanci sosai



LifeBook_Volume_3.indd 59 8/24/15 11:15 AM

.

Majikin Karusai na Wuta ya nuna labari mai tsotsa zuciya na Eric Liddell, Wanda ya ci lamabar zinariya na Olypic wanda daga baya ya yi aikin bishara a China. A majikin Liddell yayi Magana mai zurfi akan halin iyawa da kuma samin kiran ka na dabam da kuma wuri mai dadi. "Allah ya halicce ni da manufa (da dalili) – saboda China," Liddell, ya lura dangane da makomar sa, "amma Ya yi ni da sauri, kuma lokacin da na yi gudu nakan ji nishadin Sa." Wannan manuni ne ga murmushin Allah akan Liddell na daukar baiwar iyawa na Allah. Wane iyawa kake da shi, yayen da ka yi aiki da su, ka kan ji nishadin Allah?

Mai tunkarar aiki Reggie McNeal ya lura cewa, "Manyan shugabanai sun bambanta da shugabanai masu kyau, a barin, saboda mataki da aka bunkasa su da kuma gini akan karfin su. Wadannan shugabanai sun fitar cewa harbin su mafi kyau a sa babban taimakon su ga duniya ita ce domin su sami da kyau sosai abin da tuntuni suke da kyau a ciki.

4. **Jaraba.** Mene ne manyan shugabanai suka mallaka (rike) na bai daya?a cikin Magana, jaraba. Jaraba ita ce rurawa na ciki da ke iza ka zuwa ga makomai ka da Allah ya shirya. Kafin fitattun ma'aikatu su a iya gina zuciyar wani sai ta zama farin huji. A bankwanan ga Bob Pierce, wanda ya kafa World Vision da kuma Samaritan's Purse, Paul Rees ya lura cewa wadannan ma'aikatu ba ita ce kungiyoyi na farko ba; su ne "waurin zubar jinni daga Bob Pierce karyawar zuciyar sa." Dr. Pierce addu'a sa mai tsada kuma ta kafa murya domin rayuwar sa: "bari zuciyata ya yi dushe saboda abubuwa da ke cimma allah zuciya."

   Menene ta ba ka karayar zuiciya? Menene sharadi a duniya ta sa ka fushi? Wane sharadi ne a cikin birnin ka ta sa ka kuka? Wannan it ace babban asiri na tushen jarabar ka. Kuma tushen jarabar ka ita ce babban asiri ga makomar ka.



LifeBook_Volume_3.indd 60 8/24/15 11:15 AM

5. **Bukata**. Menene ka duba da kanka a matsayin halin rashin hakuri? William Wilberforce ya zo ya ga bautarwa a ko'ina a Daular Burtaniya a matsayin rashin kaubuwa da kuma rashin hakuri. William Carey ba zai iya hakurin kekasashiyar rashi yin bishara, jahilcin Indiya ba. Martin Luther King, Jr. ba zai iya hakuri na rarrabuwar kawuna a Amurka ba.

Idan zaka iya zama babu damuwa da makantaccen ido a hali na damuwa a duniya, sa'an an hakika, kana hanyar samun ta'azantuwa. Babban laifi ita ce nesa ba kusa ba kristoci sun agama rayuwar su ba bu sanin kiran su da kima aikin su. Manzo Bulus ya rubuta cewa "Ina da haki a kai na" (1 Korontiyawa 9:16). Menene umurnin ka mai tsarki? Ina ne bukatan mai da hankalin ka mafi karanci? Menene aiki da zuciyar ka ta ce, "Wannan Dole in yi"?

Duniyar mu tana rufe a cikin bukatar mutane – amma guguwar tsunami na duniya na zafi ba ita ce aikin ka ba. Wannan zai zama abin takaici. Duk da haka idan ka binciki zuciyar ka, Allah zai rura jarabar ka; bayanannen kira don jefa rayuwarka cikin daga bukata ta musamman zata shiga zuciyar ka/zata bukaci shigarka ciki da kuma kai daukin ka. Wannan ita ce takamaiman aikin ka da kuma bangare marar magnatuwa a cikin wuri mai dadi na hidimarka. Inda Ruhu ya kebe, baye baye na ruhuniya, halin iyawa, jarabar mamaya da kuma bukatar dan adam suka hadu – ka gane wuri mai dadi na aikin ka. Yayen da bangarorin nan suka hadu, za ka ba da 'ya'ya mai yawa. Yayen da ka hade a can, haka nan shafar ka zata zam.

A hidimar ikkilisiya, akwai wasu ayuka da dole ne ka yi su kawai. Akwai wasu taruruka da dole ne ka halarta, mutane suna rokon lokacin ka, sakonin yanar gizo da kuma sakon kar ta kwana suna kararowa domin ka amsa su. Yayen da aikin yi da yawa na nan da nan suna bidan hankalin ka, ba zasu samu dukka ba ko ma yawancin kai hankalin ka. Na gaskata daya daga cikin dabaru na ibilis a cikin rayuwar mu ita ce kawar da hankali (dauke hankali). Zalunci na yanzu yanzu zata iya zama cikakken gabatar da kara game da kiran rayuwar ka da kuma 'ya'yan da zasu dawama.



LifeBook_Volume_3.indd 61 8/24/15 11:15 AM

Mai yiwuwa abubuwa da yawa a yau zasu yi kokari su ture ka (kawar da kai) daga wurin ka mai dadi. Kjuma idan ka bar wannan, bada ‘ya’yan ka wa Almasihu zata zama kadan. Don haka ina rokon ka ka tsara yau da kuma kowace rana don ka kasha lokaci mai yawa a wurinka mai dadi na hidima. Abu daya tabbatacce: yayen da kake cikin kasancewar Allah, haka zaka bugi wuri mai dadi na hidimarka. Addu’ar mu ita ce za ka hadu a wuri mai dadi kuma, a sakamakon haka, za ka ba da ‘ya’ya mai yawa ga Almasihu da kuma mulkin Sa.

**HADDACEWA:**

Ni ne itacen inabin, ku kuwa rassan. Wanda ya zauna a cikina, ni kuma a cikinsa, shi ne mai yin 'ya'ya da yawa. Domin in ba game da ni ba, ba za ku iya kome ba. Yahaya 15:5

**KWAKWARA (ASALIN) GASKIYA**

Wuri mai dadi na hidimar ka ita ce inda kebewa, baye baye, halin iyawa, jaraba da kuma bukatar ka suka hadu. Wannan ita ce wuri na yin 'ya'yan ka da yawa.

**MARTANIN KA (AMSAR KA)**

- A wane wuri ne na hidimar ka kake dandana mabuwayin tabuwa na ikon Ruhu da kuma yake iyar da ka?
- Menene baye baye na ruhaniya da sun mamaye ka?
- Wadanne iyawa kake da su wanda, yayen da kake aiki da su, ka kan ji nashadin Allah?
- Menene ta ke karya zuciyar ka ta kuma sa kana so ka daki bagadi?
- Wane hali ne kake duba ba na yin hakuri (kyallewa) ba?

**LITTAFIN RAI**

**Rubutu**



LifeBook_Volume_3.indd 63 8/24/15 11:15 AM

MAKO 43

# Tada da kuma Sakar Shugabanai Matasa (Dagawa da kuma Sake Shugabanai Yan kanana)

**Karanta Zabura 78:1; Yahaya 15:9-16**

Daya daga manyan abubuwa da za mu iya yi don tabbatar cewa ikkilisiya ta kasance da karfi a gaba ita ce mu kassafa rayuwarmu a cikin dagawa (tayarwa) da kuma sake shugabanai matasa. Zabura 78 ta fada mana cewa kowace tsohon tsara hakinta ne ta mika bangaskiyar (amincewar) su cikin Ubanagiji da kuma sanin hanyoyin sa ga tsara na gaba. (Karanta Zabura 78:1-7).

Ya ya dokaci Isra'ila su horas da tsara na gaba su san Shi, su kaunace Shi su kuma san yadda zasu yi tafiya a tafarkun Sa. (Karanta Maimaitawar Shari'a 6:1-6). Manzo Bulus ya umurci dan sa ta ruhaniya, Timoti, ya tada wasu shugabanai ta yadda Bulus ya tada shi, mika sawayawa ta gaskiya na Maganar Allah a gare su, da kansa da kuma da iko. (Karanta 2 Timoti 2:2). Yi la'akari da abin da Yesu ya yi da mabiyansa na kurkusa: Ya zuba musu gaskiyar sa, rayuwarsa, da kuma kaunar sa a cikin su, ya taimake su su zama balagaggun almajirai su kuma zama ma'aikata masu anfani. (Karanta Yahaya 15:9-16).

Allah shi ne Allah na magada; Yana so sani na kirkin sa da kuma daukakar sa a mika ma kowace tsara. (Karanta Zabura

**Ba za mu boye wadannan abubuwa daga 'ya'yanmu ba, amma za mu fada wa tsara Mai zuwa labarin ikon Ubangiji, da manyan ayukansa, da abubuwan banmamaki wadanda ya aikata. Zabura 78:4**



LifeBook_Volume_3.indd 64
8/24/15 11:15 AM

> **Kada ka yarda kowa ya raina kuruciyarka, sai dai ka zama gurbi ga masu ba da gaskiya ta wurin Magana da hali, da kauna, da bangaskiya, da kuma tsarkaka.**
> **1 Timoti 4:12**

78:4; 100:5). Wannan gaskiya ne a ginin ikkilisiyar Almasihu hakan nan. Almasihu yana so kowane shugaba matashi za zama da gado da zai karba daga tsohon shugabanai, kuma kowane tsohon shugaba yana da gurbi da zai bari wa matasan shugabanai. Wannan darasi zai baka shawarwarin hanyoyi guda shida don samar da shugabanai da za su taimaka a bunkasa a kuma saki shugabanai masu tasowa cikin hidimar Almasihu.

1. **Lokaci**. Taka dauki lokaci don horas da wani cikakke ya zama mai anfani a rayuwa da kuma aiki. Babu yanke; babu maye gurbi. Yesu ya zambi almajirai goma sha biyu domin "su kasance tare da shi." Burin sa shi ne "ya aike su su je su yi wa'azi." (Karanta Markus 3:14). A matsayin shugabanai a cikin ikkilisiyar Almasihu, a kullum a kwai kalubala a gare mu mu san yadda za mu lura da lokacin mu da hikima. Wannan shi da dalilin da ya sa dole mu san fifikon hidimar mu. Bayan hidimta wa iyalanmu, fifiko mafi muhimmanci ta zama daukan lokaci da yawa muna zuba rayuwar mu cikin shugabanai na tsara nag aba. Domin idan ba tare da mun kaunace su sosai mun kuma horas da su sosai ba, ba mu da karfi a gaba.

   Wannan ita ce yadda Yesu ya gaskata ya kuma aikata. Ya dauki lokaci mai yawa da mutane wadanda za a dokace su fda shaida da kuma nuna iko na Mulkin Allah bayan Ya tafi. (Karanta Luka 3:13-15). Dalili guda da ya sa Yesu ya iya daukan lokaci mai yawa da almajiransa ita ce, Yana zaune kurkusa da al'umma na shugabanai masu tasowa. Ya aikata salon rayuwa zuwa rayuwa na aikin da ta ba shi karbuwa da su. Da gangan ya dauke su tare da Shi; sun kalle shi yana



LifeBook_Volume_3.indd 65 8/24/15 11:15 AM

wa'azi, warkaswa, da kuma fitar da aljannu. Domin Yesu, tsare tsare ne ga almajiranci horaswa ta zama rayuwar Mulki da kanta. Yayen da ya dauki lokaci don ya zauna da su ya kuma bayyana musu rayuwar sa a gaban su, bayan lokaci sun fahimci abin da yake nufi da a yi rayuwa da kuma sshugabanci a cikin kebewa, kyakkyawa, da kuma fa'ida. Yesu shi ne shugaban malamin mu. Bari mu bi misalin sa.

2. **Yi Magana**. Kome da kome a cikin Mulkin Allah tana aikatuwa ne a tushen lafiyayen alkawarin dangantaka. Yesu ya ce Babban Umurnai biyu sune: mu kaunaci Allah da dukkan ranmu, zuciyarmu, mu kuma kaunaci wasu kamar kanmu da dukkan ranmu – cikamakin shari'a da kuma annabawa ke nan. (Karanta Matiyu 21:34-40). Wadanmnan dokoki biyu duka akan dangantaka ne. An kira mu ga dangantaka da Allah da kuma wasu cikin Magana da aikatawa. (Karanta Kolosiyawa 3:17). Don mu yi danganata mai kyau da shugabanai matasa dole mu dauki lokaci mai yawa muna Magana da su. Muna bukata mu ji zuciyar su kuma suna bukata su ji namu zuciya. Yesu a kullum yana shagalar da mabiyansu cikin hira ta yin tadi, yana fito da su waje da kuma maganganun sa a cikin su. (Karanta Matiyu 16:134-19). Wannan ya taimaki almajirai su karbi irin jagoranvci da kuma horaswa da suke bukata don cin gaba da koyo da kuma girma. Kamar Yesu, dole mu bi damarmaki don samin tadi mai ma'ana da shugabani masu tasowa. Dole mu yi Magana da su ta kowace iri, cikin danganataka kuma a kullum, cikin kauna kuma za su kaunace mu domin ta.

3. **Tabawa**. Manzo Bulus ya kaunaci matashin sa da suke koyan aiki, Timoti. A wasikarsa na karshe zuwa ga Timoti ya nuna cewa shi "kaunataccen da" ne. (Karanta 2 Timoti 1:2). Yayi la'akari da halin ruhaniya, motsa rai, da kuma rayuwar danganataka na Timoti. (Karanta 2 Timoti 1:3-7). Ko suna tafiya gefe da gefe ko suna zama nesa da juna, Bulus a kullum ya ci gaba da taba rayuwar Timoti. Hakan nan, shugabanan mu matasa suna bukata su ji tabawa ta kauna daga wurin mu. Suna bukatar Magana ta kauna da kuma kauna a aikace don sadar musu yadda muka sa su a matsayin 'ya'ya ta ruhaniya maza da mata.



LifeBook_Volume_3.indd 66 8/24/15 11:15 AM

Suna bukata su ji mun dauki lokaci don bincikawa akan lafiyar su, don a kaunace su a kuma hidimta musu. A bangaren iyalin Allah, muna bukata mu yi danganata da ‘ya’yan mu ta ruhaniya maza da mata da kauna da kuma zurfafan kula.

4. **Koyarwa.** Yesu ya san gaskiyar cewa almajiransa suna bukatar su fahimci yadda zasu bi da rayuwar su da kuma aikinsu. Ya koya musu cikake ya kuma sha kansu dangane da dukkan abin da ya shafi rayuwa a Mulki. (Karanta Matiyu 5-7). Saboda wannan, ya umurce su su tafi su koyar da wasu abin da ya koya musu. (Karanat Matiyu 28:18-20). Da shugabanan mu masu tasowa dole mu bi misalin Yesu, Bulus, da sauran su, dole mu koya musu sosai. Mu tuna: idan mun koya wa shugabanan mu matasa rukuni mai kyau zamu haifar da almajirai masu inganci wadanda zasu koyar da wasu rukuni mai kyau. Ko muna yin anfani da shiryayen tsari, koyarwa bisa koyarwa a cikin Nasosshi, ko duka, dole mu koyar, koyar, koyar. Kuma yawancin koyarwa misali ne. (Karanta 1 Bitrus 5:2-3).

5. **Horaswa**. Idan mun dubi koyarwa a matsayin “menene” muka kuma dubi horaswa a mtsayin “yaya”, za ta bamu bayanannen da kuma Karin cikakken duba na yadda za mu tada shugabanai matasa mu kuma saki wadannan shugabanai matasa. Kowane shugaba matashi da ke girma yana bukatan hannu da yawa akan batsira (dandanawa). Suna bukatar jagorancin mu da kuma gurbi, amma dole kuma mu sake su don su yi aikin hidima. Yi la’akari da gurbin da yesu ya bar mana: ya koya wa almajiransa, ya nuna msu gurbin cika da ruhun hidima, sa’an nan ya sake su zuwa cikin kowace aiki da ya nuna musu. (Karanta Luka 9:1-6). Idan Yesu ya sakar zuwa cikin aiki wadanda har yanzu suna kan girma cikin kwartewar su, mu yi haka nan. Ko yaya matakin horaswar mu za ta kasance, dole ta nuna “hoto” na gurbin Yesu, nuna aiki da kuma bada aiki.



LifeBook_Volume_3.indd 67 8/24/15 11:15 AM

6. **Tafarki.** Tafarki tana kan auna ci gaba ne. ya kamata mu jagorantar da shugabanan mu yan matasa da kyau, muna taimakon su su zama da tunai mai kyau na inda suke a cikin cin gaban koyarwa da kuma horaswa. Dole mu taimake su su auna bunkasar halayen su, da kuma sanin littafi Mai tsarki da kuma fasahohin aikin su. Za mu iya yin haka ta wurin yin tambayoyi, ba da jarabawa, lura, da kuma ba da littafi ami tsarki, shawara ta jagorancin Ruhu. Duk wadannan za a yi su ne cikin mahallin dangantaka dake ci gaba. Dole mu sani sosai wadanda muke rayarwa da kuma sakewa yayen da suke tasowa don zama shugabanai masu bada 'ya'ya na tsara na gaba. Abin farin ciki guda mai girma na hidima ita ce ganin 'ya'ya na ruhaniya maza da mata suna yin fice domin mulkin Allah, suna hayayyafa suna kuma bada 'ya'ya fiye da yadda muka yi. (Karanta Yahaya 14:12; 3 Yahaya 4).

Musa ya yi nasarar horas da Joshuwa don ya jagoranci jama'ar Allah. A zahiri Joshuwa ya ga darajar wannan jagoranci. Duk da haka bababn abin tausayi na rayuwar Joshuwa shi ne bai bar magiji mai inganci ba. Joshuwa ya yi babban nasara amma ya fadi (kasa) ya shirya tsara mai zuwa saboda kalubaloli da zasu fuskata. A sakamkon haka mutane suka kauce nan da nan cikin hargitsi na ruhaniya. (Karanta Littafin Mahukunta 2:7-12). Zaka iya tabbatar da wannan: kowace lokaci ka kassafa cikin tsara nag aba za ta zama albarka daga wurin Allah. Zai iya zama babu hikimar (batsirar) kassafawa.



LifeBook_Volume_3.indd 68 8/24/15 11:15 AM

**HADDACEWA:**

Abin da ka ji a guna a gaban shaidu masu yawa kuwa, sai ka danka wa amintattun mutane, wadanda su ma za su koya wa wadansu. 2 Timoti 2:2.

**KWAKWARA (ASALIN) GASKIYA**

Babban abu guda da zaka iya yi ita ce, ka tabbatar cewa ikkilisiya ta kasance da karfi a gaba kuma ka sa rayuwar ka a tada shugabanai matasa ka kuma sake su.

**MARTANIN KA (AMSAR KA)**

- Idan ba ka yi ba tukuna, ka roki Ruhu Mai Tsarki ya bayyana daya ko fiye shugabanai matasa don ka gaiyace su cikin matakin koyarwa da kuma horaswa.
- Idan ka san wasu ma'ikata wadanda su tabbatar da mataki na tada shugabanai matasa, ka roki haduwa da su ka kuma nemi kowace irin kayan aiki da suke da shi don taimakon ka.
- Ka dauki wanaki talatin a cikin Bishara ta hannu Luka kana lura (la'akari) gurbin Yesu na horas da shugabanai masu tasowa.

**LITTAFIN RAI**

**Rubutu**



LifeBook_Volume_3.indd 69 8/24/15 11:15 AM

MAKO 44

# Anfani da Lokaci (Kula da Lokaci)

**Karanta Zabura 90:12; Yahaya 9:4; Afisawa 5:15-18; Kolosiyawa 3:17.**

Kowace minti a kidaye take – kuma za mu ba da lissafi na kowace minti. Lokaci baiwa ce mai girma da Allah ya ba mu: sauran dukan albarkunsa suna aukuwa ne cikin yanayi na lokaci. Idan lokaci baiwa ce na Allah a gare mu, abin muke yi da lokaci baiwar mu ne zuwa gare shi.

Al'adu dabam dabam suna duban lokaci ta hanyoyi dabam dabam. Yawancin mutane da ba sa al'adun mutane Yamma sukan ji cewa mutanen Yamma (turawa) masu bauta wa lokaci. Da murmushi, mutumin Afirka ya lura cewa, "Turawa suna da agogo amma babu lokaci. Afirka suna da lokaci amma babu agogo." Mutumin Filifin ya danganta agogo mai tsada da Turawa suke sakawa a matsayin gunki ne a hannayen su."

Ko menene yadda duban lokacin mu take, abu daya tabbatacce ita ce: Za mu ba da lissafi wa Yesu na yadda muka yi anfani da lokacin da aka kayyade mana. (Karanta 1 Korontiyawa 3:13; 2 Korontiyawa 5:10). Ba mamaki mai Zabura ya yi addu'a cewa, "Ka koya mana mu sani ranmu na dan lokaci ne" (Zabura 90:12) kuma Bulus ya roki masu bi cewa, "ku ceci lokaci" (Afisawa 5:15-16; Kolosiyawa 4:5). Ba da 'ya'ya saboda Yesu ta bukaci cewa mu gode wa darajar lokaci

**Saboda haka, sai ku mai da hankali kwarai da Zamanaku, kada ku zama kamar marasa hikima Ku yi matukar anfani da lokaci don kwanaki mugaye ne. Afisawa 5:15-16.**



LifeBook_Volume_3.indd 70 8/24/15 11:15 AM

(mu darajanta lokaci) mu kuma koyi yadda za mu inganta zarafi (damarmakin).

Yesu ba taba yin wasa da lokaci ba. (Karanta Luka 13:32). Ya yaba wa Maryamu saboda kin matsi da ke kewaye da ita ta zauna a tsawayen Sa. (Karanta Luka 10:38-42). Ga wasu shawarwari don taimakon ka "ka yi matukar anfani da lokaci" (Afisawa 5:16).

1. **Ka fara ranar ka (yinin ka) da dare kafin wayewan gari.** A gaban Ubangiji ka sake duban ranar (yinin) da ta gabata (ta wuce). Ka mika yinin ka a gare Shi, ka roki cewa yawancin 'ya'ya da zai dawwama zai zama sakamakon aikin ka da ka yi a ranan. Ka jera alkawura da kuma abin da dole su sami hankalin ka gobe. Ka mika wadannan abubuwa ga Ubangiji ka kuma roke shi ya rig aka gaba da jinkan Sa. Sa'ad da ka kwanta don yin barci, ka yi tunani akan kyautar Allah. Bari zuciyar ka ta raira wakar yabo. (Karanta Afisawa 5:19). Dawson Trotman ya sake jadadawa cewa, mu yi barci fa "HWLW" – "KalmanSa maganar san a karshe."

2. **Yayen da ka tashi ( ka farka), ka ba da bangare na farko na yinin ka wa Allah**. Ka yi alkawarin ka na farko na yinin ka da Ubangiji, bada wannan lokaci gare shi a matsayin nunan fari na bayaswa. (Karanta Maimaitawar Shari'a 26:10). Yayen da muka ba da wani bangare na yininmu ga Allah a cikin sujada, addu'a da kuma karanta maganar Sa, an kara mana lokaci sau biyu. (Karanta Luka 6:38). Martin Luther ya yaba cewa,

"Ina da abubuwa da yawa da zan yi a yau cewa zan yi addu'a sa'oi biyu maimakon daya!"

3. **Ka roki Allah saboda aikin yi naka na yini (na rana).** Ka yi addu,a akan yinin ka. A lokacinka na safe a gaban Allah, ka gaiyaci Ruhu Mai Tsarki ya ba ka bayanannen hanya domin yinin ka. (Karanta Zabura 31:3).

4. **Ka rayu (ka yi rayuwa) domin har abada**. Salo na rike lokaci mafi kyau da na sani ita ce a rayu saboda har abada. Rayuwa da daraja na har abada za ta taimake ka da sauri ka daidai abin da take da muhimmancin gaske. (karanta Zabura 39:4).

5. **Rayuwa cikin hasken na kursiyin shari'a na Almasihu**. Karshen nasara a cikin wannan rayuwa ita ce a ji Ubangiji ya hurta "Madalla" akan rayuwarmu. Ka yi rayuwan yau cikin haske na wannan rana lokacin da za ka tsaya a gaban Yesu don ka ba da lissafi na anfani da lokacin da ya ba ka. (Karanta Matiyu 25:21; Romawa 14:10; 2 Korontiyawa 5:10).

6. **Ka tuba daga dukan kiwiya**. Shiririta hakika "zunubi ne mai kisa" saboda za ta iya yi maka fashi na nafanin ka. (Karanta Karin Magana 18:9; 20:4; 24:30-34).

7. **Ka rayu (ka yi rayuwa) ta wurin fifiko, ba ta wurin fifikon kanka** ba. Marmarin Manzo Bulus ita ce ya ziyarci ya kuma hidimta a Roma. Duk da haka, fifikon mika kansa ga wadanda ba su ji bishara ba ta hana shi daga kai wa Roma da wuri fiye da yadda ya yi. Menene fifikon ka domin kassafa lokacin ka? (Karanta Romawa 15:20-22)



LifeBook_Volume_3.indd 72 8/24/15 11:15 AM

Mutane da yawa suna sa buri akan babu – kuma suna buga ta! Sukan sami kadan saboda ba burin da ta cancanta ba ne. Abubuwa kadan ne kawai a cikin rayuwarmu a gaskiya na nan da nan ne kuma suna da muhimmanci ko da yake abubuwa da yawa suna kuka domin mu kai hankali nan da nan. Ka roki Ruhu Mai Tsarki ya taimakeka ka sakankance abin da ke wajibi (tilas) kuma da muhimancin gaske.

8. **Ka saka jari cikin iyalinka**. Na san faston Uganda wanda ya sa ta a aikace ya sami kofin shayi da kuma ya hada da matarsa kowace yamma. A sakamakon haka aurensu ya zama gurbin daukaka na Kristi da ya faranta zuciyar mutane da yawa. (Karanta Matiyu 5:16). Saka jarin lokaci da matarka da kuma yaranka zai biya babban riba.

9. **Ka yi nasara "mintin nasarori".** Fasto a Scottish mai tsoron Allah ya sami daukaka saboda ya sami "dubban nasara na minti". Ya koyi ya "sayi damarmaki", ya cike gurabai kada na lokaci da abubuwa masu ma'ana kamar addu'a, saurin kalmomin karfafawa, karanta maganar Allah, da kuma saka kalma mai kyau na shaida domin Alamasihu. Mai gyaran mota, Henry Ford, ya lura cewa, "ya zama kulawa ta cewa yawancin mutane masu nasara sukan yi gaba a lokacin da mutane suke batawa."

   Sanannen mai tuntuba na kula dalokaci ya bada ra'ayin cewa kome da kake bukatar ka yi da ta dauki mintoci biyu ko kasa da haka – ka yi wadannan yanzun nan. Wannan zai taimaka ka share hanya domin babban aiki.

10. **Ka saka jarin lokaci a bunkasawa da kuma yin anfani da baye bayen ruhaniya da suka mamaya**. Allah ya ba ka jerin halin iyawa ta dabam da kuma baye bayen ruhaniya. Yawan lokacin da zaka dauka a hidimtawa daga karfinka, haka yawan 'ya'yan zai zama. (Karanta Yahaya 15:8).



LifeBook_Volume_3.indd 73 8/24/15 11:15 AM

11. **Ka koyi wakiltawa (ka ba da wakilci) ko yaushe da kuma a duk inda ya wajaba**. Surukin Musa, Yetro. Ya koya masa darasi na shugabanci guda daya babba. Wakiltawa taka ribambanya shafar ka ta kuma cece ka daga karar da karfin ka. (Karanta Fitowa 18:13-24).

12. **Ka fara yinin ka tun da wuri**. Idan ka tashi da wuri, kana cikin kamfani mai kyau – an san Yesu da tashi da wuri don ya yi addu'a. (Karanta Markus 1:35). Bincike na manyan shugabanan kasuwa na Amurka an tarar cewa abu na bai daya na wadannan hadin kan shugabanan nan ita ce tashi da wuri (farka da wuri).

    Wayar tangarahu, na'ura mai kwakwalwa na kan teburi, yanar gizo, shafin sada zumunta na facebook, sakonni, twitin – wadannan kayan aiki zasu yi mana aiki, ta yi aiki gaba da mu. Wadannan kayan aiki za ta iya inganta anfanin ka. Duk da haka, idan an yi anfani da yadda ya kamata, zasu iya taimako a lalatar da anfaninka. Kada ka bar fasaha ta shugabance (mallake ka). Maimakon haka, ka mallaki fasaha don daukakar Allah.

Dr. Josheph Stowell ya bada shawara cewa don a lura da lokaci da kyau ya kamata mu:

- Ka sabunta a kullum ta wurin fara kowace yini da Ubangiji
- Ka sabunta a kowace mako ta wurin yin wani abu na jin dadi da matarka kowace mako,
- Ka yi halwa kowace wata ta wurin daukan yini daya na kadaici kowace wata don ya ji muryar Allah, da kuma
- Ka sake duba kowace shekara, ta daukan mizanin shekara da kuma binikawa don ganin cewa kana kan hanya a bin nufin Allah saboda rayuwar ka.

Akwai da yawa fiye da abin da aka fada akan anfanin rike lokaci. Ka dai tuna cewa ranakun ka yi zaman su a gaban Yesu. Karshen, za bada lissafi a gare shi ga abin da ta mamaye lokacin ka.



LifeBook_Volume_3.indd 74 8/24/15 11:15 AM

**HADDACEWA:**

Ku tafiyar da al'amuranku da hikima a cikin zamanku tare da marasa bi, kuna matukar amfani da lokaci. Kolosiyawa 4:5.

**KWAKWARA (ASALIN) GASKIYA**

Kowace minti a kidaye take – kuma za mu ba da lissafin domin kowace minti.

**MARTANIN KA (AMSAR KA)**

- Menene abubuwa 2 ko 3, idan aka yi bisa tushe, zai kawo bambanci babba a cikin anfanin kanka.
- Ka yi nufin Allah yau?
- Ko kana cika nufin Allah domin rayuwar ka?

**LITTAFIN RAI**

## Rubutu



LifeBook_Volume_3.indd 75 8/24/15 11:15 AM

MAKO 45

# Hidimtawa a Wurin Aiki na Ma'aikata

**Karanta Farawa 12:1-2; Maimaitawar Shari'a 8:18; Zabura 67:1-2; Matiyu 5:16; 6:33; Luka 6:18**

A duk cikin tarihin ikkilisiya bishara ta ci gaba da yawa sosai lokacin da akwai hadin kai na kokarin wadanda aka kira su don su hidimta a aikan shugabanci na ikkilsiya da kuma wadnda an kira su don su hidimta a wurin aiki. Yesu da gangan ya zabi (cire) yan kasuwa da ma'aikata don su zama almajirai. Sa'ad da ya ke duniya, Yesu ya shirya dandali saboda nuna ikon Sa da kuma daukaka sa ita ce wurin kasuwa. Yayen da an zo zancen hidima da kuma mu'ujuzai, Yesu a fili ya shiryar wurin taruwan jama'a akan harabar haikali.

Manzo Bulus ya inganta dangantaka da wadanda suke wurin kasuwa. Wani Likita mai magani ya tafi tare da shi a yawancin tafiye – tafiyen bisharar sa (Luka). Wata mace a kasuwaci ya yi kawance da ita ta zama jigo a kafa bishara a warin da ba su ji bishara (Lydiya). Yayen da yake tafiya ya horas da wani saurayi daga wata tushen al'ada (Timoti). Ya sami girmamawa a wurin shugabanan gwamnati (Felis da Festus). A dukan lokaci Bulus ya yi aikin tenti don ya taimaka a biyan kudin tafiye-tafiyen bisharar sa. (Karanta Ayukan Manzanni 18:3).

A shekaru da yawa da sukla wuce Ruhu Mai Tsarki ya juya kan hidimtawa a wurin kasuwa. "Wurin Kasuwa" ta ta rufe bangare na rayuwa da ta yi tasiri akan

**Albarka ta tabbata ga masu kwadaita ga adalci, domin za a biya musu muradi.**
**Matiyu 5:6**



LifeBook_Volume_3.indd 76 8/24/15 11:15 AM

al'ada: Fasaha da nishadantarwa, kasuwanci, ilimi, iyali, gwamnati, jarida, addini (ko bangaskiya), da kuma wasanni. Wadansu suna danganta wadannan wurare da "Duwatsu bakwai" da ya zama dole a haura kuma tutar mulkin Almasihu ta kahu a kwalkolin domin sauyin ceton (fansar) dukkan al'ada. Tare wadannan bangarori guda bakwai sun gina al'umma, sun siffata tsarin akida (Imani), sun kuma bude gidaje ga girbi ta ruhaniya na dukan duniya. (Karanta Matiyu 5:13-16; Filibiyawa 2:15).

Babban bangare na nawaya (hakin) fasto ita ce ya shirya wadanda suke kalkashin kulawarsa don su hidimta sosai a kowace bangare na rayuwa. (karanta Afisawa 4:11-12). Fastoci su ga wadanda aka kira zuwa kasuwanci (da kuma dukkan bangarori na wurin kasuwa) a matsayin ma'akata masu dabara na bishara. Fastoci su martaba kira mai tsarki na masu bi, su darajanta aikin su a cikin Mulkin Almasihu, su kuma taimake su su yi nasara. Ga wasu hanyoyi da za mu iya taimakon wadanda an kira su a matsayin masu hidima a kasuwa da suke daukaka Allah suke kuma sawaya bangarorin su na yin tasiri ta wurin ikon Almasihu.

1. **Aiki Allah ne ke bayarwa kuma ya kamata a dube shi a matsayin ibada ga Allah**. Yawancin kristoci suna tunkuda rayuwarsu cikin abin da suke tunani a matsayin tsarki da kuma na duniya. Amma ga krista da sun sami sadarwa ta littafi Mai tsarki babu shinge sakanin biyun. Dukkan rayuwa za a dube su a matsayin tsarki – a matsayi masu lura da kuma ibada ga Allah. (Karanta 1 Korontiyawa 10:31). Aiki (ko kasuwanci) da aka yi don daukakar Allah da tunanin mulki kira ne mai tsarki. Tana nan kamar kira mai tsarki kamar kira don a zama fasto ko mai bishara. (Wahayin Yahaya 1:6;5:10).


LifeBook_Volume_3.indd 77 8/24/15 11:15 AM

Allah da kansa ma'aikaci ne – kuma babban aikin sa mutane ne. (Karanta Yahaya 4:34; 5:17; Afisawa 4:10). Yesu ya shaida cewa Ya gama aikin da aka ba shi daga wurin Uba. (Karanta Yahaya 17:4). Yesu ya ce mu yi addu'a domin ma'aikata a cikin girbi na ruhaniya. (Karanta Matiyu 9:38). A dukkan bangare na rayuwa ya kamata mu yi aikin mu kyau, da maida hakanli, ta wurin ikon Ruhu Mai Tsarki, da lamiri mai kyau, da godiya, domin daukakar Allah da kuma fadada Mulkin Sa , da kuma duba zuwa mawwami. (Karanta Matiyu 6:3-4; Romawa 12:10-11; Kolosiyawa 3:17; 1 Bitrus 4:10-11; W. Yahaya 14:13). Oswald Chambers ya rubuta cewa, "Rayuwata a matsayin ma'aikaci hanya ce da na ce 'na gode' wa Allah domin ceton sa da ba za a iya fada ba."

2. **Daya daga cikin fili mai girma na yin bishara ita ce wurin aiki**. Masakancin dan kasuwa zai yi cudanya (ma'amala) da Karin yawan batattun mutane a kowace mako fiye da yawancin fastoci ko gwararrun masu hidima. Girbin rayuka suna girke a wurin kasuwa ne. masu bi a duniyar kasuwanci ya kamata su ga kansu aikakku ne daga Allah a matsayin "masu bishara na wurin kasuwa". (Karanta Matiyu 9:37; 1 Timoti 2:4).

   Yesu Almasihu ya ba da Babban Umurni ga duk mabiyanSa. Ya kira mu don mu juyo makiyansa su zama abokanansa zuwa ga mabiyansa da suka mika kai, (Karanta Matiyu 28:18-19; Markus 16:15). An kuma dokace mu da mu kula mu kuma mulki duniya, kawo dukan bangarori na ayukan mutum cikin daidaici da mulkin Allah. (Karanta Farawa 1:28). Wadannan ayukan yi za a yi su a ta hanyaoyi da yawa na wurin kasuwa. Muna tarayya da Allah cikin kawo mulkin Sa a duniya. Allah ya na farin ciki yayen da muka tsara, gina, kirkira, magance matsaloli, kawo tsari, samo tattalin arziki, kai ga wasu. Allah yana yin anfani da mutanen Sa cikin kasuwanci da kuma ta wurin kasuwa don sawaya rayuka. Ya yi anfani da wurin cin kasuwa don ya bude kofofi na zarafi inda masu bishara ta al'ada ko masu hidimar wa'azi ba zasu iya zuwa ba.



LifeBook_Volume_3.indd 78 8/24/15 11:15 AM

3. **A matsayin wadanda suke cikin alkawari da Allah an kira mu don mu albarkaci dukkan duniya**. A madadin zuriyar Ibrahim ta ruhaniya, a hade ga Allah da alkawarin Sa na albarka ta wurin bangaskiya cikin Almasihu, an kira mu don mu isar da wadannan albarku ga dukkan mutanen duniya. A matsayin wakilan Almasihu an kira mu don mu kawo hasken Almasihu da kuma sawayawa mai iko na bishara a cikin dukan sassa na rayuwa. (Karanta 2 Korontiyawa 5:17-21). An albarkace mu – don mu zama albarka – ga dukan duniya. Wannan ita ce "kewaya alkawari" na albarka. (Karanat Farawa 12:1-3; Zabura 67:1-2; Galatiyawa 3:13-14).

4. **Allah ya ba wa wadanda suke cikin alkawari da shi iyawa don kawo wadata**. Ruhu Mai Tsarki shi ne "dama ta hamayya" a wurin aiki. Ka zama kebabbe saboda kasuwanci, ka karbi kirkirawa, ra'ayoyi masu anfani a matsayin baye baye daga wurin Allah. (Karanta Maimaitawar Shari'a 8:18). Mabuwayin fasahohi, batsira, jinkai da kuma sakankancewa suna nan a yalwace don mutanen mulki a kasuwanci. (Karanta Fitowa 31:1-5; 2 Korontiyawa 16:9) Ishaya 48:17; Kolosiyawa 1:16). Da mabuwayin makamashi a yalwace aikin mu zai zama da kyau. Masanin Tau'idi Elton Trueblood ya rubuta, "karanci da ganganci zunubi ne."

5. **A matsayin yan kasuwa cikin alkawari da Allah, an sawaya zuciyarmu kuma hanyen mu a bude ne**. hankalin mu ba akan biyan bukatun mu da kuma bukatun iyalan mu kuma ba. Allah ya riga ya yi alkawarin zai yi wannan. (Karanta Filibiyawa 4:19). Sai dai, yanzu mu ga kanmu a matsayin masu hidima na mulkin Almasihu, kirayayyu don kai albarku na bishara a duk inda muke. (Karanta 2 Korontiyawa 5:20). Ka nome "da yawa fiye da bukata" na hankali. (karanta 2 Korontiyawa 9:8.



LifeBook_Volume_3.indd 79 8/24/15 11:15 AM

6. **Mu nuna gurbin "rayuwan bayarwa" mu nemi damarmaki don mu zama albarka, kawar da talauci, mu kuma fadada ajendar mulkin Almasihu.** Harsashin salon rayuwar bayaswa ita ce zakka. Idan mun ba da na goma na shigar mu (samun mu) wa Allah, an yi mana alkawarin kariya na kudi. (Karanta Malachi 3:10-11). Fasto Robert Morris ya rubuta, "lokacin da shaidan ya zo gaba da kai da tsoro ya kuma ce 'Za ka zama fatararre, auren ka zata fadi, za ka kamu da cuta', zaka amsa masa da tabbaci, 'Babu, ni zakka ne, kuma saboda ni zakka ne Littafi Mai Tsarki ya ce Allah zai sauta wa Mai cinyewa saboda ni. hakiya, saboda ni! Allah shi ne farko a rayuwana, kuma Allah zai ceci rayuwana ya kuma kare kowace abu a cikin rayuwa na!"

   Duniya zasu gane ingancin kular Allah na bayin sa kuma za a kai su ga bangaskiya a cikin Sa. (Karanta Malachi 3:12). Wannan shi dalilin da ya sa Jim Elliot ya yi addu'a, "Ubangiji, ka wadata hanyata, ba don in kai ga matsayi mai tsayi ba, amma don rayuwata ya iya zama manuni ga daraja na sanin Allah."

   Allah ya alkawarta cewa wadanda suka bayar wa talaka ba zai rasa kome ba. (Karanta Karin Magana 28:27). Salon rayuwan bayaswa ta hada da kudi, amma ya wuce bad kudi kawai. Zaka iya ba da lokacin ka, addu'arka, karfafawar ka, fasahar ka, da kuma sauran makamashi da kake da su. Sa'ad da muka bayar, kuma kome da muka bayar, bari mu dube ta a matsayin iri da muke shukawa da za ta ba da anfani. (Karanta Farawa 8:22). Yesu ya koyar cewa lokacin da muka bayar, da abin da muka bayar, mu sammanci mayarwa a cikin jarin mu. Ka nemi hanya, kowace rana, don ka ba da wani abu ga Allah ka kuma ba da wani abu wa mutane.



LifeBook_Volume_3.indd 80 8/24/15 11:15 AM

7. **A matsayin fasto, ka nemi hanyoyi don ka karfafa yan kasuwa (da kuma wadanda suke kowace aiki) a cikin ikkilisiyar ka ka kuma tabbatar da kiran su zuwa ga hidima a wurin aikin su. Muna kebe wadanda a ka kira su don hidimar wa'azi.** Don me ba za mu kebe wadanda a ka kira su ga hidima a wurin aiki ba? Ka dora hannu akan wadanda suke bauta wa Yesu a "duwatsu bakwai" na al'ada ka kuma jawo kebewa ta Ruhun Allah akan aikin su da kuma kiransu. Ka je wuraren kasuwancin su ka yi musu addu'a a gefe cewa Allah zai sa su wadata. Fastoci su nuna girbin ba da zakka, aminci, mutunci, karamci. Hange da kuma lamiri na mulki ga masu hidima a wurin aiki. (Karanta 1 Bitrus 5:2-3).

    Ka taimaki wadanda suke hidimtawa a wurin aiki su fahimci aikin su a fadada mulkin Almasihu. Ka taimaki yan kasuwa su gina "kasuwancin Babban Umurni". Anfani domin ikkilisiyar ka da kuma domin mulkin Almasihu zai zama mai girma.



LifeBook_Volume_3.indd 81 8/24/15 11:15 AM

**HADDACEWA:**

Abin la'akari fa, shio ne wanda ya yi kwauron yafa iri, gonarsa za ta yi masa kwauron amfani, wanda kuwa ya yafa a yalwace, sai ya girba a yalwace. Sai kowa ya bayar yadda ya yi niyya, ba tare da bacin rai ko tilastawa ba, domin Allah yana son mai bayarwa da dadin rai. Allah kuwa yana da iko ya ba ku fiye da bukatarku, domin kullum ku wadata da kome ta kowace hanya, kuna ta bayarwa hannu sake, kowane irin kyakkyawan aiki. Kamar yadda yake a rubuce cewa, "Y aba gajiyayyu hannu sake, ayukansa na alhari madawwama ne."
2 Korontiyawa 9:6-9.

**KWAKWARA (ASALIN) GASKIYA**

Dukkan rayuwa tana da tsarki. Dukkan masu bi a cikin Almasihu suna da aikin yi na firist. Kowace aiki ya zama kira mai tsarki.

**MARTANIN KA (AMSAR KA)**

- Ka dauki hali na "Kasuwancin Mulki": "Allah ne ya kebe ni don in yi aiki a wurin da
ya ajiye ni, sanin cewa dukan bukatuna za a biya ta wurin Sa. Zan yi nasara yayen da na yi biyayya gare shi. A matsayin mutum da ke cikin alkawari da Allah ta wurin bangaskiya cikin Dan Sa. An albarkace ni don in zama albarka ga dukan duniya. Yau, a matsayin wakilin Almasihu, ina da zarafi na daukaka Allah, kwatanta bishara, kawar da talauci, sawaya bangarorina na tasiri da kauna, haske, da kuma rayuwa na Yesu Almasihu"

**LITTAFIN RAI**

**Rubutu**



LifeBook_Volume_3.indd 82 8/24/15 11:15 AM

MAKO 46

# Ka Zama Shugaba na Babban Umurni

**Karanta Zabura 78:72; Matiyu 28:19.**

Babban girbin rayuka na duniya tana zuwa. Wasu masu lura da aikin bishara sun gaskata cewa a kalla mutane a miliyan daya zasu zo ga bangaskiya cikin Almasihu a shekaru goma masu zuwa. Tunda ikkilisiyu a fadin duniya za ta dandana babban girma (karuwa), zai zama dole ga kowane shugaban ikkilisiya ya tashi ga matakin tasirinsa na gaba domin Almasihu. Karin shugabanai da kuma shugabanai mafi kyau za a bukace su don iza yawan sabobin tuba (masu bi) da yawa.

Allah yana kiran ka don ka zama shugaban na Babban Umurni – shugaba wanda zuciyarsa take kuna saboda daukakar Allah da kuma saboda almajirtar da dukkan duniya zuwa ga Almasihu. Addu'a na shugaban Babban Umurni ita ce, "Sunan ka da kuma shahararka ita ce marmarin zukatanmu." (Ishaya 26:8).

Amma ka zama a shirye. Yayen da mutum ya mika kansa da gaske don ya cika Babban Umurni, zai zama akan radar ibilis. Hakika, wannan ba tana nufin cewa mu koma da baya daga aikin bishara da kuma misan ba. Ta na nufin mu gane cewa wannan yaki ne na gaske da mutuwa da jin ciwo. (Karanta Afisawa 6:10-18). A shekaru kalilan da suka wuce na shaida yadda ibilis ya nufi babban bindigar sa akan wadanda suka kawo shugabanci ga aikin bishara na duniya. Dole mu yi addu'a

**Dawuda kuwa ya lura da su da zuciya daya, da gwaninta kuma ya bi da su.
Zabura 78:72.**

sosai saboda juna mu kuma mika kanmu ga tsaron abokan mu daga harin abokan gaba. (sake duban darasi na 14 da 32).

A littafin sa, *Aiki na Zuciya*, Reggie McNeal ya lura cewa, “Wadanda an kira don su zama shugabanai na ruhaniya suna jin haduwa da babban hoto na masu ra’ayin cin gaban Allah, ajendar Mulkin Sa. Suna ji mutum mutum nawaya (haki) saboda yin tarayya da Allah a aikin Sa. Za su iya yin aiki a wurin mafi tsaro, amma canza duniya ita ce burin su. Wannan damuwa ba ta dace da karshen rayuwa ba; wannan cike wuri ne a rayuwa na kira.”

Shaci na gaba an tanada daga Dr. Bill Bright kafin rasuwar sa. An yi anfani da izini daga Global Pastors Network. A wannan shacin Dr, Bright ya lura cewa halaye da shugabanai na Babban Umurni suka nuna (bayyana). Fasto ko shugaba krista wadanda suka nuna halaye goma na Babban Umurnin shugabanci za su yi zaman:

1. **Rayuwar mika kai**. Shugaban Babban Umurni ya mika kai cikakke ga ikon Almasihu a kowace bangare na rayuwa. Kullayomi zai sa kansa “a bagadi” don Allah ya yi anfani da shi saboda manufar Sa. (Karanta Romawa 12:1-2).

2. **Rayuwa bisa ga Nassi**. Shugaba na Babban Umurni ya darajanta Littafi Mai Tsarki a matsayin rubutaccen wahayin Allah ne zuwa ga mutane. Ya auna duban (fahimtar) duniyar sa da kuma dandana rayuwar sa akan mizali na Nassi. Zai nemi ya danganta rayuwarsa da maganar Allah. (Karanta Joshuwa 1:8; 2 Timoti 3:16-17).


LifeBook_Volume_3.indd 84 8/24/15 11:15 AM

3. **Rayuwar cika da Ruhu**. Mai Bishara D.L. Moody ya fadi cewa, “Mutum ba zai yi numfashi ba tare da iska da sauki ba kamar yadda Krista ma ba zai iya rayuwa ba tare da Ruhu Mai Tsarki ba.” Shugaban Babban Umurni ya bar Ruhu Mai Tsarki ya cika shi ya kuma mallake shi. Zai marabci ya kuma sammanci kawo dauki da kuma kebewa ta mabuwayi. (Karanta Afisawa 5:18).

4. **Rayuwar ceton rayuka**. Shugaba na Babban Umurni ya shaida bangaskiyarsa cikin Almasihu cikin kauna ga wasu. Ya karfafa sauran masu bi don su bada shaida a kan Yesu ga wasu, hakan nan. Yana rayuwa da nufin bishara da kuma yana dokin ganin mutane sun zo ga dangantaka da Yesu Almasihu. (karanta Karin Magana 11:30; Daniyel 12:3).

5. **Rayuwar bautawa.** Ya bi gurbi (misali) na Ubangijin sa, shuagaba na Babban Umurni ya nemi ya zama shugaba-bawa. Ya bauta wa Yesu da kuma manufofin Sa a tsarar sa. (Karanta Matiyu 23:11; A. Manzanni 13:36; Galatiyawa 5:13).

6. **Rayuwan tsarki**. Shugaban Babban Umurni ya kebe kansa saboda Allah kuma saboda Allah kadai. Ya yi da kawace zunubi a cikin rayuwarsa babu tausayi da kuma marmarin sa na faranta wa Allah rai a dukkan abin da ya ke fada, tunani, da kuma yi. Shi kamar abin da Bulus ya ce, “a ware daga bisharar Allah” (Romawa 1:1). (Karanta 2 Timoti 2:21; 1 Tassalonikawa 5:23).



LifeBook_Volume_3.indd 85 8/24/15 11:15 AM

7. **Rayuwar rashin son kai**. Shugabanai na Babban Umurni ba su yin rayuwa don su faranta kansu rai. Suna rayuwa ne domin Almasihu da kuma saboda wasu. (Karanta 2 Korontiyawa 5:15; Filibiyawa 1:21).

8. **Rayuwa ta hadaya**. Shugabanai na Babban Umurni sukan kidaya sadar farashi. Sa'an nan su manta da sadar. Sukan biya farashin don cikasa nufin Allah. (Karanta 2 Korontiyawa 12:15; 1 Bitrus 2:21-23).

9. **Rayuwar lura**. Shugaban Babban Umurni yana rayuwa dangane da zaben sa mai zuwa da Almasihu, inda zai ba da lissafi ga yin anfani da lokacin sa, mallakarsa, da kuma tasirin sa. (Karanta Romawa 14:10-12)

10. **Rayuwar nasara**. Shugaba na Babban Umurni yana jira ya karbi "Madalla" na Almasihu da za a furta a kansa. Shugaba na Babban Umurni ya fahimci cewa rayuwar nasara ta gaskiya ana aunawa ba ta wurin tsawon lokaci ba, amma ta wurin hanyar ta (jagorancin ta); ba ta wurin jam'iyun ta ba, amma ta wurin manufufin ta, ba ta wurin abin da aka tara ba amma ta wurin abin da batar (yasar), ba ta wurin rungumar na abubuwa ba, amma ta wurin rungumar Abu Daya – ya kaunaci Yesu matuka ya kuma sa mutane su kaunaci Yesu a ko'ina. (Karanta Matiyu 25:21).

Shugaba na Babban Umurni zai auna kowace abu da ya yi ko ta taimake shi a cika Babban Umurni ko babu. Hdimar sa zata bada 'ya'ya inda jama'a suke kara zama kamar Almasihu kuma ana kara rayuka a mulkin Allah.



LifeBook_Volume_3.indd 86 8/24/15 11:15 AM

A matsayin shugaba da ke tashi, dole mu sami lokaci na kadaici mu zama a ware a gaban Ubangiji. A littafin sa, *Shugabanci na Karfin Hali*, Bill Hybels ya kira mu don sake duban kasancewar mu a gaban Allah kowace shekara. Wadannan su ne tambayoyin da ya yi wa kansa lokacin sake duba na kansa na shekara:

- Kira na tabbatacce ne?
- Hange ne a bayyane take?
- Jaraba na tana kuna?
- Ina raya baye baye na?
- Ko na mika hali (rayuwa) na wa Almasihu?
- Ko girman kai na ta ragu?
- Ina shawo kan tsoro?
- Ko wasu kafofi na ciki suna raina shigabanci na?
- Ko sauri na rikakkiya ce?
- Kauna ta ga Allah da kuma mutane na karuwa?

Bari Allah ya shafe (kebe) ka don ka zama shugaba na Babban Umurni.



LifeBook_Volume_3.indd 87 8/24/15 11:15 AM

**HADDACEWA:**

Na zama kowace irin abu ga kowadanne irin mutane, domin ta ko kaka in ceci wadansu. Na yi wannan ne duk saboda bishara, domin in sami rabo a cikin albarkata. 1 Korontiyawa 9:22b-23.

**KWAKWARA (ASALIN) GASKIYA**

Allah yana kiran ka don ka zama shugaba na Babban Umurni, ka auna dukan abin da kake yi ta wurin ko tana taimakon ka cika Babban Umurni ko babu,

**MARTANIN KA (AMSAR KA)**

- Ka mika kanka yau cewa, ta wurin alherin Allah, za ka zama shugaba na Babban Umurni.

**LITTAFIN RAI**

## Rubutu



LifeBook_Volume_3.indd 88 8/24/15 11:15 AM

MAKO 47

# Muryoyi Bakwai da zasu Canza Rayuwarka

**Karanta Ishaya 6:8; 1 Sama'ila 3:9; Matiyu 11:15.**

A karshen 1940s, wani da ya kamala karatun kwaleji ya rubuta a cikin lattafin ajiye kundin sa, "Yi la'akari da kira daga Kursiyi a Sama, 'Ka tafi', da kuma magamin hanya, 'Ka ketaro ka taimaka mana,' ko kuma kira daga rayuka da ke hallaka a kalkashi, 'Aika da Li'azaru zuwa wurin 'yan'uwana, don kada su zo wannan wuri.' Ka zaku ta wurin wadannan muryoyi, ba zan taba yarda in zauna a gida yayen da Quichuas ta ke hallaka." Saurayi Jim Elliot ya ji muryoyi da suka canza rayuwar sa. Shekaru kalilan daga baya, "Ka zaku ta wurin wadannan muryoyi" ya bada ransa don yin kokarin ya kai bishara zuwa karkara na kabilar Waodoni.

Haduwa ta kwaikwayo na Ishaya da Allah ya zurfafa cikin kira na aikin bishara. (Karanta Ishaya 6:1-8). Ishaya ya ji murya daga sama, kuma rayuwarsa ta nuna alama daga wancan rana.

Sau takwas a cikin Bisharu Yesu ya yi kira da karfi, "Wanda yake da kunnen ji, bari ya ji!" Kana da kunne don jin abin da Ruhu yake fada maka, wa kasar ka, wa ikkilisiyarka wa duniya? Akwai kara guda bakwai – muryoyi guda bakwai – da za ta canza rayuwarka. Yayen da ka ji wadannan muryoyi ba za ka zama yadda kake ba.

**Sai na ji Ubangiji yana cewa, "Wa zan aika? Wa zai zama manzonmu? Sai na amsa na ce. "Ga ni! ka aike ni" Ishaya 6:8.**



LifeBook_Volume_3.indd 89 8/24/15 11:15 AM

**Sa'an nan mala'ika na bakwai ya busa kahonsa sai aka ji wadansu muryoyi masu kara a Sama, suna cewa, "Mulkin duniya ya zama na Almasihunsa, shi kuma zai yi mulki har abada Abadin. Wahayin Yahaya 11:15.**

1. **Murya daga sama umurni ne na iko**. "Wanene zan aika, kuma wane ne zai je mana?" Ishaya ya ji wannan umurni mai iko daga kursiyi a sama. Ya juya ga zuciyar aikin misan na Allah. Martanin sa nan da nan ita ce, "Ga ni nan! Ka aike ni" (Ishaya 6:8). Wannan murya daga sama, wannan umurni na iko, ta zo da karfi kuma a fili kuma lokacin da Yesu rayayye ya ba da Babban Umurnin Sa. (Karanta Matiyu 28:18-20; Markus 16:15-20; Luka 24:46-49; Yahaya 20:21; Ayukan Manzanni 1:8).

2. **Murya daga kasa kuka ne na har abada.** Yesu ya fada mana a fili cewa zabin da muke da ita kadai su ne rai na har abada tare da Allah ko hallaka ba tare da shi ba. (Karanta Yahaya 3:16). Dole mu roki Allah ya sa mana damuwa saboda batattu. Tana da kyau a tuna da makoma na har abada na wadanda ba su da Almasihu. William Booth, wanda ya kafa Salvation Army ya ce, yana ji cewa idan ma'aikatan sa zasu tafi jahannama na mintoci biyar za ta shiryar da su na dukan rayuwarsu na hidimar tausayi. Ta na da matsi a kokwawar wadannan abubuwa; za ta dame mu cikakke don motsa mu zuwa ga bishara ta tausayi. (Karanta Luka 16:24; 2 Tasalonikawa 1:7-9).

3. **Murya daga waje kuka ne na dan adam**. Lokacin da Yesu ya ga taron jama'a, Ya ji tausayin su. Bari Allah ya taimake mu mu gani da gaske taruwan jama'a da kuma bukatar su saboda Almasihu. (Karanta Matiyu 9:36; Joel 3:14). Mutane a duk duniya suna cikin


LifeBook_Volume_3.indd 90 8/24/15 11:15 AM

bakin duhu ta ruhaniya. Zuciyar su na roko domin wani ya nuna musu hanya mafita daga duhu. (Karanta Ayukan Manzanni 16:9).

4. **Murya daga ciki rada ce na wajibi (tilas).** Akwai wani wajibci mai tsarki a cikin rayuwar ka? Manzo Bulus ya gane zurfin alhaki don kai bishara ga mutane a ko'ina. Kana da wannan ganewa na wajibci mai tsarki don kai wa ga mutane da ikon yanci na bishara? (Karanta Romawa 1:14-16; 1 Korontiyawa 16:9).

5. **Murya daga baya (da ta gabata) hadi ne na tarihi**. Yawancin jarumawan sojoji na gicciye sun wuce kafin mu. Yanzu suna sama, suna mana sowa a kan tseren mu. (Karanta Ibraniyawa 12:1). Ka karfafu yau: Tarihi ta na tafiya zuwa kwalkoli lokacin da Yesu zai yi mulki akan dukkan mutane da kuma kasashe! (Karanta Ishaya 9:6-7; Wahayin Yahaya 11:15).

6. **Murya daga yanzu kira ne na zarafi**. Ka duba gefe; ko'ina ka duba akwai zarafi don fadada manufar mulkin Almasihu. Bari Allah ya ba ka hange mai girma. (Karanta Karin Magana 28:19). Bari ka zama da idanu don ganin girbin da ta nuna a duk gefen ka. (Karanta Yahaya 4:35; Romawa 13:11; Galatiyawa 6:9; Afisawa 5:16).

7. **Murya daga gaba (a gaba) kuka ne na makoma**. Wata rana Babban Umurni za ta zama Babban Kammalawa! Zai zama akwai fansassun mutane daga kowace kabila, harshe (yare), da kuma al'umma suna bauta wa Allah da kuma Dan, Yesu Almasihu. An ba mu zarafi na mutunci da kuma kira na tafiyantar da tarihi zuwa wancan abin yi mai banmamaki. (Karanta Wahayin Yahaya 5:9-10; 7:9-10).



LifeBook_Volume_3.indd 91 8/24/15 11:15 AM

**HADDACEWA:**

Sai na ji Ubangiji yana cewa, “Wa zan aika? Wa zai zama manzonmu? Sai na amsa na ce. “Ga ni! ka aike ni” Ishaya 6:8.

**KWAKWARA (ASALIN) GASKIYA**
Yayen da ka ji wadannan muryoyi guda bakwai, za su canza hankali da kuma fifiko na rayuwar ka.

**MARTANIN KA (AMSAR KA)**

- Ka bar wadannan muryoyi su jiwu sosai a cikin ruhun ka. Za su iza ka don aikin
daukaka Almasihu.

**LITTAFIN RAI**

**Rubutu**



LifeBook_Volume_3.indd 92 8/24/15 11:15 AM

MAKO 48

# Kai wa Birnin ka Bishara saboda Almasihu

**Karanta Irimiya 29:7; Yunana 4:11; 2 Bitrus 3:9.**

Ikkilisiyu nawa ne a brini ko garin ku? Daga yadda Allah yake dubawa ikkilisiya daya ne kadai – wannan haka ne, daya! Manzo Bulus ya fada wa ikkilisiya a Afisa, "akwai jiki daya kuma Ruhu guda, kamar yadda an kira mu ga bangaskiya daya da kuma kiran ku" (Afisawa 4:1-6). Ya rubuta wa masu bin Yesu da ke zaune a Afisa ya kuma gargade su su yi aiki tare cikin dayantaka – saboda girman ikkilsiya da kuma daukakar Allah. Shekaru da yawa daga baya, lokacin da manzo Yahaya ya tura wasika daga wurin Yesu zuwa ga wannan ikkilisiya, ya rubuta ta ga wannan ikkilsiya na Afisa; abin da zamu iya kira ikklisiyar birni – ikkilisiya guda ta hada da taruwan jama'a da yawa. (karanta Wahayin Yahaya 2:1.)

Daidai kafin Yesu ya haura zuwa sama Ya fada wa almajiransa su karbi iko ta wurin Ruhu Mai Tsarki su kuma kai zuwa Urushalima da bishara (Karanta Ayukan Manzanni 1:8). Wannan ita ce dai dai abin da su ka yi. (Karanta Ayukan Manzanni 2:42-47). A wannan shafi za ku lura cewa mutane suna kai wa ga birnin Urushalima da bishara ta wurin nufi daya, yayen da Ubangiji yana kara musu sabobin rayuka wadanda ake ceta zuwa ikkilisiya lokaci lokaci, kowace rana.

**In kun zauna a cikina, maganata kuma ta Zauna a cikinku, zaku roki duk abin da kuke so, za a kuwa yi muku.**
**Yahaya 15:7**

**jiki guda ne, Ruhu kuma guda, kamar yadda aka kira ku a kan begen nan guda, wanda yake game da kiran nan.**
**Afisawa 4:4.**

Domin a kai a kuma sawaya birninku ta wurin ikon Allah dole ku yi aiki tare da Jikin Almasihu ta yanayi na hadin kai da kuma kyakkyawar manufa. A wannan darasi zaku ga kwakwarar bangarori uku domin kai bishara zuwa birane da fastoci da yawa a dukan duniya suke samunta da anfani kuma da kawo sauyi.

1. **Bunkasar da dangantaka daga tushe da sauran shugabanai Krista**. Jack Dennis a cikin littafinsa, *Kaiwa zuwa Birni*, ya rubuta akan bukata domin shuagabanai a cikin birni su matsa daga “zumunta zuwa abokantaka don yin aiki tare.” Dole mu kakkarya kowace nuna bambanci (gibi) da ke raba mu idan muna so mu ga ikon Almasihu da ke zuwa ta wurin dayantaka. Dole mu matsa gaba da inda muke da kuma yankin mu don mu kasance da mutane da mai yiwuwa sun sha bamban da mu ta wasu hanyoyi. Suna da tamani a wurin Allah kuma ya kamata su zama da tamani a gare mu. A cikin addu’ar sa na Babban Firist, Yesu ya yi addu’a cewa dukkan mabiyansa za su zauna tare su kuma hidmta tare cikin kauna da hadin kai domin duniya ta gaskata bishara. (Karanta Yahaya 17:21-23). Dangantaka ta kauna na masu bi ga juna ita ce daya daga cikin shaidu manya manya ga Yesu Almasihu – aikin sa, sakon Sa, da kuma hidimar Sa. Kuma daya ne daga cikin abubuwan “jan hankali” masu girma na kasancewar Allah (Karanta Zabura 133; Yahaya 13:35).


LifeBook_Volume_3.indd 94 8/24/15 11:15 AM

Kari, Ubangiji yana so mu a matsayin shugabanai mu bunkasa abokantaka mai zurfi da juna da zata ciyar ta kuma kara mana karfi. Sauran wasu mutane da suke a kadaice a duniya shugabanai ne krista. Ibilis yana nema ya raba mu ya kuma ware (kadaita) mu, amma Ruhun Allah yana nema ya hada mu ya kuma albarkace mu da abokan tarayya da za mu iya kaunarsu mu kuma amince (yarda) da su. Babu abin da ya fi farin ciki fiye da ka tashi kowace rana ka sa mulkin Allah ya ci gaba da abokananka a duk cikin Jikin Almasihu. Bari Allah ya tanada maka wadatar abokantaka sa'ad da kake kai wa cikin bangaskiya ga sauran shugabanai krista. Irin wannan abokantaka ba ya faruwa kawai; dole ka sa jiki ga bunkasa su.

2. **Hadaddiya, sawwayawar addu'a**. Babu muhimmin abu da zai faru a cikin al'ummarku ba tare da hadin kai, jazirtaccen addu'a. Daya daga cikin alama na wannan muhimmin abu da ya kawo girmar da ikkilisiyar birni ta zama akwai dukufa ta mika kai ga yin addu'a. (Karanta Ayukan Manzanni 2:42). A cikin kayan aikin addu'ar Steve Hawthorne, Ka nemi Allah saboda Birni, ya dauko maganar fasto wanda ya ce, "wadannan addu'oi sun yi girma ka yi kai kadai." Idan zamu yi addu'a saboda Mulkin Allah ya kusa cikin birnin mu ya kuma sawaya ta, dole mu zama a hade cikin addu'a. Allah ya kira mutanen Sa su zo tare su yi addu'a tana samuwa a duk cikin Nassi. Allah ya fada wa sarki Suleimanu cewa yayen da akwai hukunci a kasa zasu shagala cikin gaskiya, kaskanci, hada kai cikin addu'a. (Karanta 2 Tarihi 7:12-14). Allah ya tabbatar wa jama'arsa cewa idan zasu yi addu'a tare cikin kaskanci da kuma bangaskiya Zai ji ya kuma amsa da taimako da warkaswa. Lokacin da Bitrus da Yahaya aka azabta musu kwarai daga shugabanan Yahudawa saboda yin wa'azin Almasihu a matsayin Ubangiji, sun koma wurin abakanansu suka fada musu abin da ya faru. Sa'ad da abokanan su ka ji maganar su, suka je ga addu'a. suka yi addu'a domin karfin hali suka kuma yi addu'a domin bayanuwar Allah da iko a Urushalima. Tare, suka yi addu'a a cikin mawuyacin hali da suke ciki. Allah ya amsa ta wurin girgiza inda suka taru, ya kuma cika su da Ruhu Mai Tsarki. A sakamakon haka, sun ga Karin ikon Allah a cikin birnin su. (Karanta Ayukan Manzanni 4:23-31).



LifeBook_Volume_3.indd 95 8/24/15 11:15 AM

Duk inda ka sami jama'ar Allah suna taruwa saboda hadaddiyar addu'a domin birnin su, yankunsu ko kasar su Allah yakan motsa kuma abubuwa sukan canza zuwa mai kyau. A wurare da yawa a fadin duniya a kwai shugabanai da suke taruwa kowace mako don yin addu'a a wuraren su. Sa'an nan, lokaci lokaci, duk wadannan rukunoni suna taruwa saboda kololuwar taruwar addu'a ta yanki don su yi addu'a suna kuma gaskata Allah domin fansa mai girma da zai shafa a wurin su. Idan akwai taruwa na shugabanai suna yin addu'a a cikin al'ummar ku, ka hade da su. Idan babu – ku fara daya! Allah zai darajanta ta.

3. **Da gangan, hadaddiyar aikin bishara**. Allah yana da dabara domin kai wa ga al'ummarka da bishara. Allah yana da dabara don sawaya yankinka ta wurin hannunsa na alheri ta wurin jama'arsa. Muddin kun zo wuri daya (kun taru) cikin zumunta, kun kuma girma tare cikin abokantaka da kuma yarda, lokaci ne da za a fara aiki tare. Yayen da mutane da suke hade suka taru tare a cikin yanayi na kaskanci da kuma daukaka, Allah zai yi Magana. Allah yakan fara bayyana abin da yake so a yi don hidimta wa mutane a cikin sunan Sa. (Karanta Ayukan Manzanni 15). Ta wurin yin sujada, addu'a, sauraron Ruhu Mai Tsarki da kuma tattaunawa, hange (wahayi) yana kasancewa a fili (dalla dalla). Sa'an nan, kamar yadda take dandanawar masu ra'ayin ci gaban ikkilisiyar birni a ko'ina, Ruhun Allah yakan fara bayyana shugabanai bayi wadanda suke shirye don aiki a matsayin kungiyar ikkilisiyar birni. Wannan kungiya tana taimakawa a aiwatar da wahayi da Allah ya bayyana.



LifeBook_Volume_3.indd 96 8/24/15 11:15 AM

Yayen da muke tafiya cikin ruhu na kaskanci babu wuya a gano menene kiran Allah domin kowane mai bi da kuma domin kowace taron ikkilisiyar wuri a cikin kai bishara ga birni. Tana da muhimmanci a tuna cewa don a kai ga yanki da kyau dole mu fahimci wani abu na tarihinta, halayen ta na musamman da kuma bukatun ta. Shugabanan yankuna su ga aikin su a matsayin masu taimakawa hanyoyi don taimakon kowane shugabanan rukuni su zama da anfani a wurin su, su gane cewa Allah ya ajiye su ya kuma ba su alheri don su hidimta a wurin. Kuma abin da ya rike kome da kome matsawa gaba sosai ita ce abokanai a cikin hidima – 'yan'uwa maza da mata a cikin Almasihu – suna neman fusakar Allah tare cikin addu'a domin birnin su. Ku yi addu'a domin wadanda suke mulki a cikin birnin ku. (Karanta 1 Timoti 2:1-4). Sa'ad da kake yin addu'a saboda salamar Allah ya habaka a cikin birnin ka, zaka sami salama. (Karanta Irimiya 29:7).



LifeBook_Volume_3.indd 97 8/24/15 11:15 AM

**HADDACEWA:**

Ba kuwa wadannan kadai nake roka wa ba, har ma masu gaskatawa da ni ta maganarsu, domin dukansu su zama daya, kamar yadda kai, ya Uba, kake cikina, ni kuma nake cikinka, haka su ma su kasance a cikinmu, domin duniya ta gaskata, cewa kai ne ka aiko ni. Yahaya 17:20-21.

**KWAKWARA (ASALIN) GASKIYA**

Domin kaiwa ga birni da kuma sawayata ta wurin ikon Allah dole ku yi aiki da babban Jikin Almasihu a cikin yanayin hadin kai.

**MARTANIN KA (AMSAR KA)**

- Ka yi addu'a kullum saboda dayantuwa a tsakanin taruwar ikkilisiya a cikin al'ummar ku.
- Ka nemi fastoci domin yin zumunta, haduwa ta addu'a, da kuma hadin kan aikin bishara zuwa ga birni.
- Ka shagalar da ikkilisiyar ku a cikin kowace kokarin hadin kai da wasu ikkilisiya don daukar ikon sawayawa na bishara zuwa ga al'ummarku

**LITTAFIN RAI**

**Rubutu**



LifeBook_Volume_3.indd 98 8/24/15 11:15 AM

MAKO 49

# Shirya Ikkilisiyar ka (Tara Ikkikisiyarka) Saboda Girbi

**Karanta Luka 10:2; Yahaya 4:35; Wahayin Yahaya 14:15.**

Girbi ta ruhaniya tattarawa ne na batattu da kuma mutane da suke da karayya zuwa cikin sabon rayuwa da kuma makoma mai zurfi a cikin Almasihu. Kuma ita ce tattarawa na almajirai da suka mika kai da kuma shugabanai wadanda suke girma a cikin manufar rayuwarsu na kawo mutane da yawa zuwa ga bada gaskiya cikin Almasihu. (Karanta Matiyu 4:19). A matsayin shugabanai dole mu shagala (shiga) cikin taimakon mutane don su ingizu mu kuma shirya su domin girbin rayuka masu tamani. Kuma muna bukata mu shagala (shiga) cikin ingizawa da kuma shiryar da mutane don su taimaka a kawo cikin girbin "masu yin girbin," – karin mutane wadanda suke da jarabar shiga cikin kawo Yesu zuwa ga mutane da kuma kawo mutane zuwa Yesu.

Na Biye su ne gaskiya guda bakwai da muke bukata mu yi la'akari dangane da girbi ta ruhaniya:

1. **Girbi wani abu ne da Yesu ya damu a kai sosai**. Sa'ad da Yesu ya ke tafiya daga birni zuwa birni yana wa'azi, koyarwa, da kuma warkaswa, sai ya lura da yadda mutane ke galabaita sun kuma bata. Yayen da ya ga halin da suke ciki ya yi bakin ciki matuka a ransa. Yanayin su ya sa shi jin tausayi. Sa'an nan, ta sa shi mika kansa, mika kai don ganin cewa wadannan batattun tumaki sun same shi

**Ka yarda, albarkarka ta kasance tare da mu, ya Ubangiji Allahnmu. Ka sa mu yi nasara game da dukan abin da za mu yi! I, k aba mu nasara a dukan abin da muke yi!**
**Zabura 90:17**



LifeBook_Volume_3.indd 99 8/24/15 11:15 AM

**Da ya fito daga jirgin ya ga babban taron mutane. Sai ya ji tausayinsu, ya kuma warkar da marasa Lafiya a cikinsu.**
**Matiyu 14:14.**

a matsayin makiyayin su na gaskiya. (Karanta Matiyu 9:35-38). Haka take a yau – Yesu ya damu kwarai a kan mutane da ba a ceta (fansa) ba wadanda suke galabaita da kuma gajiyayu, haka mu ma ya zama.

2. **Girbin tana da girma kuma da yawa.** (Karanta Matiyu 9:37). Yesu ya aiki saba'in na mabiyan Sa zuwa waje cikin birane da kuma garuruka in da yake tunanin zuwa don ya je ya yi wa'azi. Yayen da ya yi wannan sai ya ce musu, "Girbin na da yawan gaske, amma ma'aikatan kadan ne; don haka, ku roki Ubangijin girbin ya aiko da masu girbi cikin gonar Sa" (Luka 10:1-2). Yesu ya yi wannan Magana shekaru 2000 da suke wuce. A yau girbin sun fi yawan gaske. A zahiri, fiye da kashi biyu bisa uku na yawan mutanen duniya ba su da shaida da Shi ta kowace hanya. Muna da kira na zarafi (damar) nawaya (haki) na matsawa zuwa cikin filin girbi mai girma na duniya mu kuma karfafa wasu su yi haka nan.

3. **Girbin ta nuna kuma tana cikin hatsari**. A wata karo Yesu ya fada wa almajiranSa cewa girbin ba ta nuna kawai ba amma "ta yi fari" (Karanta Yahaya 4:34-38). Yayen da dawa (alkama) ta yi fari ana dauka ta zarce nuna kuma tana bukata a girbe nan da nan (yanzu yanzu). Idan ba a girbe nan da nan ba girbin zai lalace. A matsayin shugabanai, dole mu fito da tunani na nan da nan a cikin mutanen mu. Kowace rana ita ce rana da ta dace, kowace lokaci ita ce lokacin da ya kamata (yayi daidai), kuma kowane mutum shi ne wanda da ya kamata a shaida masa bishara. Dole mu tuna maganar


LifeBook_Volume_3.indd 100 8/24/15 11:15 AM

masanin Tau'idi Carl Henry da ya fada, "Bishara ita ce kadai albishir mai dadi idan ta zo a kan lokaci."

4. **Girbin tana tattare da taron jama'a da ake kauna sosai amma sun bata da zurfi**. Allah ya halicci mutane da anfani mai girma da kuma manufa. Duk da haka, cikakken anfanin su da kuma manufar su za ta iya tabbata kadai a cikin Sa. Zunubi ta kawar ta kuma bata (lalatar) da yanayin mutum, ta sa shi galabaita, kuma marar anfani ga nufin Allah da kuma aikin sa. (Karanta Romawa 5:12; Afisawa 2:12). Allah yana kaunar mutane sosai har ya ba da Dan Sa, Yesu Almasihu, a matsayin mai ceto da kuma hadaya saboda zunubansu. Yayen da mu da kuma mutane da muke jagoranta mun gane yadda mutane suke babu bege kuma babu taimako kuma babu rain a Almasihu da kuma shugabancin sa, za ta motsa mu zuwa kauna, tausayi, da kuma aikin fansa (ceto) ta yadda ta faru da Yesu . (Karanta Matiyu 9:36; 14:14).

5. **Girbin na bukatar masu girbi (ma'aikata) masu kwazo**. Dole mu horas da mutanen musaboda bishara – shaida Albishir Mai dadi na ceton Allah ta wurin Almasihu da wasu. Kwararen mai bishara Donald McGavran ya ce, "Duniya tana da mutane masu nasara fiye da a baya… amma mai yiwuwa ne a fito daga cikin filin girbin hannu wofi." Hanyar da zamu sa mutanen mu daga zaman rayuwa "hannu rabbana" ita ce ta wurin iza su saboda bishara ta wurin yin wa'azi da kuma koyarwa, ta wurin ribato mutane zuwa ga Almasihu da kansa mu kuma nuna gurbi na yin bishara mai fa'ida, da kuma ta wurin karfafa mutanen ka su shaida ma wasu dandanawar su na kai ga sanin Almasihu. Kari, kawo amintattun masu bishara wadanda suke da baiwa don su shirya mutane su shaida bishara da wasu tana da anfani sosai kuma da taimako kwarai.



LifeBook_Volume_3.indd 101 8/24/15 11:15 AM

6. **Masu girbi dole su zama masu yin addu'a su kuma shiri domin girbin**. Dole mu yi iyakan kokarinmu don mu shirya kowane memba na ikkilisiyoyin mu domin bishara. Dole mu yi addu'a da cewa Allah ya zai taimake su don su ga damarmaki da kuma bukatau, da kuma tunanin kaunar Sa mai zurfi da kuma tausayin sa saboda batattu. Kuma dole mu zama da shiri domin taimakonsu don su ga wurin su, mu kuma horas da su don su yi nasu aiki na kawo wadanda suka galabaita su kuma hada mutane ga Almasihu. Kari, yayen da muka yi addu'a da kuma shiri dole mu zama a shirye don mu aiki sabobin tuba (masu bi) nan da nan matsayin masu girbi zuwa cikin yanayi na dangantaka. A tuna, girbi mai girma tana bukatar ma'aikata masu yawa da za a kawo cikin girbin.

7. Matakin girbin tana da manufa da kuma bada 'ya'ya (anfani). Yesu ya kai hankali kuma yana da manufa a yadda yake rayuwa da kuma hidimtawa. Ya je kowace birni, gari, da kuma kauye a duk cikin Palestinu, ya bar azurtacciyar shaida na kaunar Sa da kuma iko. Yesu ya haifar da 'ya'ya masu yawan gaske a duk inda ya je; an warkar da marasa lafiya, an kubutar da masu al'jannu, kuma mutane sun ji da shawo kai da kuma bayanannen gaskiya akan yadda za su daidaita da Allah.

   Yesu ya zo duniya da aikin don fansar dan adam da kuma cika nufin Uban Sa. (Karanta Luka 19:10). A kan gicciye ya tada murya, "An gama!" (Yahaya 19:30). Aikin da aka aiko shi don ya yi an kamala. Yesu shi ne babban jagoranmu da kuma gurbin mu saboda cika aiki da kuma hidimar da ya kira mu zuwa ciki. Dole mu yi addu'a domin girbin – batattu da kuma mutane da suka galabaita. Dole mu yi addu'a domin ma'aikata (masu girbi) - Karin mutane don a kawo su cikin sabon gonar da aka ceta sabo, rayuka da aka sawaya. Kuma dole mu sa yin aiki da Ubangijin girbi da kuma aiki domin sa ta zama mana fifiko. Sa'an nan za mu ba da 'ya'ya da yawa 'ya'ya na har abada. (Karanta Yahaya 15:8) girbin yana da girma. Bari mu je mu kawo ta ciki.



LifeBook_Volume_3.indd 102 8/24/15 11:15 AM

**HADDACEWA:**

Ya ce musu, “Girbin na da yawan gaske, amma ma’aikatan kadan ne; don haka, ku roki Ubangijin girbin ya aiko da masu girbi cikin gonar Sa” Luka 10:1-2.

**KWAKWARA (ASALIN) GASKIYA**

Girbin ita ce taruwar batattu da kuma mutane da suka galabaita zuwa cikin sabon rayuwa da kuma makoma mai zurfi cikin Almasihu

**MARTANIN KA (AMSAR KA)**

- Ka yoi addu’a domin batattu a kullum ka kuma sa ikkilisiyar ku ta yi hakan nan.

- Ka yi alkawari a klullum ga Ubangijin girbi cewa za ka mori kowace zarafi don ka shaida bishara da kuma shaidar ka da wasu.

- A kullayomi ka gargadar ka kuma shirya wadanda suke karkashin shugabancinka don su kawo mutane zuwa ga Almasihua matsayin abokan tarayya cikin girbin Sa.

- Ka gina dangantaka mai karfi ta amincewa (yarda), da masu bishara masu bada ‘ya’ya wadanda zasu taimaka a iza a kuma shirya mutane saboda yin bishara.

LITTAFIN RAI

**Rubutu**



LifeBook_Volume_3.indd 103 8/24/15 11:15 AM

MAKO 50

# Mabudi (Makulli) zuwa ga Girbi

**Karanta Matiyu 9:35-38.**

A karshen ayoyi na Matiyu 9, Yesu ya ba mu mabudi (makulli) guda goma da za ta bude girbin rayuka ta ruhaniya. Wadannan makullin za su yi aiki a kowace al'ada da kuma kowace kasa. Su ne makulli da Yesu ya yi anfani don kawo mutane zuwa gare shi.

1. **Mabudi na jikuwa jagab**. "Yesu ya zaga dukan biranen su da kuma kauyukan su" (Matiyu 9:35). Da Yesu, babu wurin da bai da muhimmanci kuma babu miutanen da ba su da anfani. Duniyar mu a yau tana saurin zama birni. Kwararun masu bishara sun shawarta cewa zamu iya zuwa birni ne kawai ko "wurari da akwai dabaran zuwa." Har yanzu a dan gajeren shekaru uku na hidimar sa, Yesu ya hidimta a "dukan birane da kauyuka" na yankin sa. Wannan makullin ta tunashe mu cewa kafa iklkilisiya masu yawa ta zama fifiko. Bari Allah ya sa wuta a zuciyarka ka zuba rayuwarka a cikin ikkilisiya ta daukakar Almasihu, wa'azin bishara a kowace birni da kuma kowace kauye. Ubangijinmu ya dokace mu da mu kira kowane mutum a ko'ina zuwa ga baban bukin sa. (Karanta Luka 14:12-23; Wahayin Yahaya 19:9,17).

**Domin Dan Mutum ma ya zo ba domin a bauta masa ba, sai dai domin shi ya yi bautar, ya kuma ba da ransa fansa saboda mutane da yawa. Markus 10:45.**

2. **Makulli na yin shela (shaida).** Yayen da yake zagaya kowace birni da kowace kauye, yana "koyarwa da kuma wa'azi" (Karanta Matiyu 9:35). A matsayin masu hidimar bishara, a kullum mu zama a



LifeBook_Volume_3.indd 104 8/24/15 11:15 AM

**Ya kuwa mutu ne saboda dukan mutane, domin wadanda suke a raye, kada su yi zaman ganin dama a nan gaba, sai dai su yi zaman wannan da ya mutu saboda su, aka kuma tashe shi saboda su.**
**2 Korontiyawa 5:15.**

shirye don "yin wa'azin kalma" (Karanta 2 Timoti 4:2). Mu yi wa'azin Albishir Mai dadi na Mulkin Allah. (Karanta Luka 9:60). Ya kamata mu yi wa'azin Albishir mai dadi na mutuwar Almasihu da kuma tashin sa domin mu. (karanta Markus 16:15; 1 Korontiyawa 15:1-4). Wannan bishara ta daukaka tana da iko don ceton dukan wanda ya ji ta sun kuma bada gaskiya cikin Almasihu. (Karanta Romawa 1:16; 1 Korontiyawa 1:21).

3. **Makulli na gwadawa**. Ba koyarwa da wa'azi kadai Yesu ya yi ba, ya je yana "warkas da kowace irin cututuka da rashin lafiya" (Karanta Matiyu 9:35). Ya kamata mu bi gurbin Ubangijinmu: wa'azi, koyarwa, da kuma warkaswa. Wannan ita ce, hakika, abin da almajirai na farko su ka yi cikin biyayya da Babbam Umurni. (Karanta Markus 16:20). Mai bishara na ikkilisiyar farko, Filibus, ya bi wannan gurbi a cikin taruwar bisharar sa a biranen Samariya. (Karanta Ayukan Manzanni 8:5-8). Al'ajibai da mu'ujizai da ya nuna cewa Yesu yana da rai. Wannan hadi na bishara da kuma wa'azi, aikin tausayi, da kuma al'ajibai ta bude duniya ga gaskiya na Almasihu. (Karanta Matiyu 5:16; Romawa 15:18-19).

4. **Mabudi na tunani**. Yesu da gaske "ya ga taron jama'a" (Matiyu 9:36). Yesu bai yi tafiya dabam cikin taruwa na mutuntaka ba, zuciyar sa ta tafi kan kowane mutum da ke da bukata. Yesu ya "ga" mutane; ya dubi bukatun su, zunubansu, sosa zuciyarsu. A matsayin babban firist mai aminci, Ya yi juyayi da kasawar mu.



LifeBook_Volume_3.indd 105 8/24/15 11:15 AM

(Karanta Ibraniyawa 4:15). Amma bai bar su ba a cikin galabaitar su. A matsayin shafaffen almasihu na Allah, ya yantar ya kuma warkar da mu. (Karanta Luka 4:18-19; 1 Yahaya 3:8).

5. **Mabudi na tausayi.** Da Yesu ya ga taron mabukata. "Sai ya ji tausayin su" (Matiyu 9:36). Dukkan hdidima ta gaskiya tana kwararowa daga kauna na Allah ne. "'ya'yan ruhu kauna ne" (Galatiyawa 5:22). Kauna ce ta sa Allah ya aiko Dansa. (Karanta Yahaya 3:16; Romawa 5:8). Kauna ce take iza mu mu tafi cikin sunan Almasihu (Karanta 2 Korontiyawa 5:14-15). Bangaskiya tana aiki ta wurin kauna. (Karanta Galatiyawa 5:6). Ruhu Mai Tsarki ya zubo da kaunar Allah a cikinmu. (Karanta Romawa 5:5).

6. **Mabudi na shugabanci**. Tausayin Yesu saboda mutane ya taso saboda Ya suna "kama da tumaki da babu makiyaya" (Matiyu 9:36). Babu wanda zai jagorance su zuwa ga rayuwa ta salama da biyan bukata. (Karanta Zabura 23:1-3). Yesu ya koyar cewa wadanda zasu shugabantar a mulkin sa zasu zama kamar Sa, su zama bayi. (Karanta Markus 1042-45). Babban cancanta domin shugabancin Krista ita ce a kasance a gaban Yesu. Godiya ga Allah, wannan suna nan a yalwace ga kowane mai bi a cikin Almasihu, ko da yaya matsiyinka/ki ko mataki na horaswar ka/ki yake. (Karanta Ayukan Manzanni 4:13).

7. **Mabudi na wahayi** (hange). Ganin bukatu masu girma da kuma nawaya (hakin) mutane a gare shi, sai ya ce, "girbin na da girman gaske" (Matiyu 9:37). Yayen da wasu zasu ga bukatu na tunzurawa, shugabanai krista su ga girbi na banmamaki. Ko da yaya kin karbuwa mutanen zasu zama a wurin ku, a kwai kebabben girbi na ruhaniya da Allah ya shirya domin ka, ikkilisiyarka, da kuma ma'aikatanka. Amma dole ka sa lauje na bishara domin ka girbe hatsin! (Karanta Wahayin Yahaya 14:15-16). Allah ya tambayi Irimiya "Me ka gani?" (Irimiya 1:11). A yau Yana tamabayar ka, "me ka gani; menene wahayin ka?" An kira shugabanai don su bada wahayin Allah. Allah hure mutane masu hange na kai hankali da kuma kawo bege domin gaba mai kyau. (Karanta Karin Magana 29:18).



LifeBook_Volume_3.indd 106 8/24/15 11:15 AM

8. **Makulli na hakika (zahiri).** Yesu ya ce, "Ma'aikatan kadan ne" (Matiyu 9:37). Yana bada hakikanin gwaji ne. girbin na da yawa. Duk da haka, a yanzu babu ma'aikata da yawa don tattara girbin. Mu zama mutane da aminci a cikin bakunanmu da kuma bege a zukatanmu. Amma ba za mu rungumi kuskure (karya) da ta musanci gaskiya. A cikin hidima, mu zama mutane na bangaskiya mu fadi gaskiya. An karfafa mu don "mu kira wadannan abubuwa da suka kasance kamar basu kasance ba" (Karanata Romawa 4:7). Amma bangaskiya ba karya ba. Ya kamata mu dauki duba ta zahiri na hali, kin zama da damuwa, mu kuma kawo bukatu a gaban Allah cikin addu'a ta bangaskiya. (Karanta Filibiyawa 4:6).

9. **Makullin na shiga sakani**. Yayen da aka gano bukata na gaske, ya kamata mu "yi addu'a ga Ubangijin girbi" (Matiyu 9:38). Wannan ita ce lakabi na nasara da Yesu ya ba wa kansa. Girbin sa ne kuma shi ne Ubangiji a kan ta! Wannan shi ne ya sa zamu iya addu'a da karfin gwiwa saboda ceton wadanda muka mika rayuwarsu ga Almasihu. Mun sani yana so ya ceci batattu. (Karanta Matiyu 18:11-14; 2 Bitrus 3:9). Ya kamata mu yi addu'a babba mu kuma yi babban bangaskiya. Ubangijin girbi yana farin cikin ganin babban girbin rayuka an tara su. (Kranata IRimiya 33:33:3; Afisawa 3:20-21).

10. **Makulli na aikawa**. Yesu ya koyar cewa mu "yi addu'a ga Ubangijin girbi ya turo ma'aikata cikin gonar sa" (Matiyu 9:38). Ya yi anfani da aikatau mai karfi wanda take nufin ya tunkuda ma'aikata cikin girbin. Bukatan ma'aikata na da yawa. Shi ya sa za mu yi addu'a cewa a turo Karin sabobin ma'aikata da yawa zuwa cikin girbi na ruhaniya da ta nuna na duniya. (Karanta Yahaya 4:35; Wahayin Yahaya 14:15-16).



LifeBook_Volume_3.indd 107 8/24/15 11:15 AM

**HADDACEWA:**

Ba kuna cewa, kaka saura wata hudu ba? Ina gaya muku fa, ku duba gonaki, ku gani, sun nuna sun isa girbi. Yahaya 4:35

**KWAKWARA (ASALIN) GASKIYA**
Wadannan makulli guda goma zatsu bude kofar girbi ta ruhaniya a ko'ina a duniya.

**MARTANIN KA (AMSAR KA)**

- Ka mika girbin da ya nuna ta ruhaniya a gonar da Allah ya danka maka.

- Ka fara a yau ka yi anfani da makulli goma don ganin girbi mai girma na rayuka
saboda Almasihu, ikkilisiyar Sa, da kuma Mulkin Sa.

**LITTAFIN RAI**

## Rubutu



LifeBook_Volume_3.indd 108 8/24/15 11:15 AM

# Don me Zamu Tafi (Zamu Je)

**Karanta Markus 16:15; 3 Yahaya 7**

Tsohon Karin maganar China, "Ga wanda ya san me ya sa zai iya jimrewa ko ta yaya." a wata kalman, ga mutumin da ya san dalilin da ya sa ya aikata zai jimre kowace wahalan da ya sa shi yin haka. Maganar Allah ya bada dalilai da yawa da ya sa za mu tafi da sakon sawayawa na Almasihu. Hakika, ya kamata mu kara kokari don mu yada bishara a kasar mu. Amma sabunta bishara a nan tana daure ga sabunta aikin bishara a duniya gaba daya. Ga dalilai goma bisa ga littafi mai tsarki da ya sa za mu kai bishara zuwa ga iyakar duniya.

1. **Da farkon fari, za mu tafi saboda Yesu ya cancanta**. Yesu ya cancanci a san da shi, a yi masa biyayya a kuma yi masa sujada ta wurin kowane mutane da kuma kasa. Littafi Mai Tsarki ya ce almajirai krista na farko "Suka tafi a cikin sunan sa" (3 Yahaya 7).

   Wannan ita ce abin da ta ina masu bishara su tafi da bishara tun bayan da Yesu ya bada Babban Umurnin sa ga mabiyansa. Shugaban manzanni na Moravia, Nikolas von Zinzendorf, ya kalubalanci kristoci "su yi nasara domin Dan Rago sakamakon hadayar sa" Bishara ba akan dalili ne da farko ba, a kan Almasihu ne. mu tafi "saboda sunan Sa."

**Sai Yesu ya sake ce musu, salama'alaikun! Kamar yadda Uba ya aiko ni, haka ni ma na aike ku. Yahaya 20:21.**

2. **Mu tafi saboda Uba yana jira**. Tun bayan faduwar mutum a cikin gonar Eden, zuciyar Uba na Allah yana ta neman mutum ya dawo wurin Sa. (Karanta

**Sai ya ce musu, ku tafi ko'ina a duniya ku yi wa dukan yan adam bishara Markus 16:15.**

Farawa 3:8-9). Littafi Mai Tsarki ta ce Allah baya jin dadi kowa ya rabu da shi. Yana son dukkan mutane a ko'ina su juyo daga zunubansu su juyo gare shi. Allah yana jiya ya ka kawo mutane a ko'ina zuwa cikin rungumar kaunar Sa. (Karanta 2 Bitrus 3:9). Kana son tabbacin cewa Allah yana kaunar ka? Ka dubi gicciye! Kaunar Allah a gare ka an tabbatar da ita ta wurin hadayar fansa na Almasihu. (Karanta Romwa 5:8)

3. **Mu tafi saboda Ruhu yana motsawa.** Allah ya yi alkawari wa annabi Yowel cewa a kwanakin karshe zai zubo da Ruhun Sa akan a dukan duniya. (Karanta Yowel 2:28). Wannan ta cika a lokacin mu. A shekaru masu yawa a baya Yesu da kansa ha bayana ga daruruwan marasa bi a cikin mafarkai da wahayi, yana kawo su zuwa ga bangaskiya a cikin Sa. A dukkan duniya Ruhun Allah yana motsi, yana jawo miliyoyin mutane zuwa ga bangaskiya a cikin Yesu Almasihu. Yana bayyana daukakar tashin Sa "ta wurin tabbatawa da yawa" (Ayukan Manzanni 1:3).

4. **Mu tafi saboda girbin ya nuna**. Na yi ta yin wa'azin bishara tun ina dan karami. A duk shekarun nan ban taba ganin irin yunwa mai girma ta ruhaniya kamar yadda take a yanzu ba. Girbin ya nuna. Dole mu leka ta katanga mu kuma ga girman duniya. Yayen da lokacin girbi yayi babu wani abu a cikin shirin manoma. Aikin sa kadai itace ya tattara anfanin zuwa ciki, kafin lokacin tara anfani ya wuce. Aikinmu a yanzu ita ce mu girbe anfanin da ya nuna na mutane. Kamar yadda John



LifeBook_Volume_3.indd 110 8/24/15 11:15 AM

Wesley ya fada wa masu wa'azin sa, "kuna da aiki daya: ku ceto rayuka." (karanta Yahaya 4:35).

5. **Mu tafi saboda mutane sun bata**. Muatne sun bata ba tare da Almasihu ba. Sun yi nisa da Allah kuma a yanke daga albarkunsa da kuma alkawaran Sa. (Karanta Ishaya 53:6; Afisawa 2:12). Ko da ma kankanuwa aya a cikin Littafi Mai Tsarki ta gabatar da zabi na har abada. (Karanta Yahaya 3:16). Wadanda suka bada gaskiya ga Yesu Almasihu suna da rai na har abada wadanda suka ki bada gaskiya a gare shi zasu hallaka. Ba zai zama da damuwa sosai ba. Manzo Bulus ya rubuta akan kuhunci mai zuwa, *"ya kuma ba ku hutu har da mu ma, ku da ake kuntata wa din, a ranar bayanar Ubangiji Yesu daga Sama tare da manyan mala'ikunsa, a cikin wuta mai rurawa, yana ta saka wa wadanda suke ki sanin Allah, da kuma wadanda suka ki bin bisharar Ubangijinmu Yesu. Za su sha hukuncin madawwamiyar hallaka, suna a ware da zantin Ubangiji, da kuma madaukakin ikon sa" (2 Tassalonikawa 1:7-9).*

    Allah da gaske yake yi a kan kai Albishir Mai Dadi na Almasihu ga wadanda suke neman danganta da shi da gaske. Karniliyus ya mika kai, yana addu'a a kullum, yana bayarwa hannu sake ga matalauta ya kuma samu ziyara ta mala'ika. Har yanzu Allah ya tafi hanya mafi fadi don ya kai masa bishara don ya zo ga sanin Yesu Almasihu yua kuma sami ceto! A bin da ya faru a Ayukan Manzanni 10 da 11 ta bayyana a fili cewa Bitrus bai dauki za a gafarta zunubin Karniliyus ba har sai da ya gaskata sakon bishara. Mala'ika ya umurci Karniliyus ya aika a kirawo Bitrus "wanda zai zo ya fada maka Magana wanda ta wurin ta kai da jama'ar gidan ka duka zaku sami ceto" [abin da zai faru a gaba] (Ayukan Manzanni 11:14). Sa'an nan Ruhu Mai Tsarki ya tabbatar da aikin bangaskiyar Karniliyus.

6. **Mu tafi saboda al'ummai sun cancance ta**. Shekaru da yawa da suka gabata mai bishara, Oswald J. Smith, ya yi tambaya mai tsoka zuciya, "me ya sa sai wani ya ji bishara sau biyu kafin kowa ya ji sau daya?" Wadanda ba su da bishara sun cancanci su ji ta. Ta zama tushen haki ne na mutum. Allah ya kudurta ya karbi daukaka daga kowane mutane da kuma kasa. (Karanta Wahayin Yahaya 5:9; 7:9; 15:4).



LifeBook_Volume_3.indd 111 8/24/15 11:15 AM

7. **Mu tafi saboda an umurce mu**. Sarkin sarakuna ya umurce mu da mu tafi. Idan gaskiya mu almajiransa ne, zamu yi farin cikin yi biyayya da umurnin sa. Ya kamata zuciyar mu ta buga a ciki da zuciyar Allah don ganin daukakar sa ta zubo wa duniya da kuma ganin an yi wa dan sa sujada ta wurin dukkan kabilu da kasashe. (Karanta Yahaya 5:23)

   Yesu ya bada Babban Umurni ta wasu yanayi a dukan Bisharu da kuma a Littafin Ayukan Manzanni:

- “Don haka sai ku je ku almajirtar da dukkan al’ummai” (Matiyu 28:19).
- “ku tafi ko’ina a duniya ku yi wa dukan yan adam bishara” (Markus 16:15).
- “A kuma yi wa dukan al’ummai wa’azi su tuba, a gafarta musu zunubansu saboda sunan sa” (Luka 24:47).
- “Kamar yadda Uba ya aiko ni, haka ni ma na aike ku” (Yahaya 20:21).
- “Amma za ku sami iko sa’ad da Ruhu Mai Tsarki ya sako muku, zaku kuma zam shaiduna a Urushalima, da duk kasar Yahudiya, da ta Samariya har ya zuwa iyakar duniya” (Ayukan Manzanni 1:8).

Wannan mabuwayin aiki ne. ta fi karfin kokarin mu na mutum. Shi ya sa Almasihu ya yi alkawarin iko wanda ya fi gaban sani – iko na Ruhu Mai Tsarki – kowace lokacin da ya bada wannan mabuwayin umurni.

8. **Mu tafi saboda dole ne mu bada lissafi**. Littafi Mai Tsarki ya tunace mu cewa, a matsayin masu bin Yesu Kristi. Dole mu bada lissafi na rayuwarmu bayan mun tuba a gare shi. Yaya muka yi anfani da lokacin mu? Yaya muka kula da baye bayen mu? Yaya muka zuba mallakar mu? Duk wadannan za su zo domin a duba a kursiyin sharia na Almasihu. “Don dukan mu za mu tsaya a gaban kursiyin shari’a na Almasihu, domin kowa ya sami sakamakon abin da ya yi tun yana tare da wannan jiki, ko mai kyau ne ko kuma mara kyau” (Karanta Romawa 14:10; 1 Korontiyawa 3:1; 3:11-15; 2 Korontiyawa 5:10).



LifeBook_Volume_3.indd 112 8/24/15 11:15 AM

9. **Mu tafi saboda zarafin kadan ne kuma na yanzu yanzu**. Tarunn jama'a suna tafiya cikin hutu na har abada na Almasihu kowace minti. Shi ya sa umurnin yin bishara ta zama yanzu yanzu. Ci gaba, zarafi nay au ba suna yare kawai ba. Girbi da lokacin ta. An sa lokaci a cikinlauje kuma girbin yanzu ne! (karanta Wahayin Yahaya 14:15). Yesu ya gargadi cewa dare tana zuwa kuma dole mu yi aiki a gajertyaciyar yini na zarafi. (Karanta Yahaya 9:4; Romawa 13:11).

10. **Mu tafi saboda mu mutane ne masu makoma.** "Amma ku kabila ce zababbiya, kungiyar firistocin babban sarki tsastsarkar al'umma, jama'ar mallakar Allah, domin ku sanar da mafifitan al'amuran wannan da ya kirawo ku daga cikin duhu, ku ka shiga madaukakin hasken sa." (1 Bitrus 2:9). Krista suna ta karanta wannan aya kusan shekaru 2000. Amma idan har rukunin krsitoci za su karanta wannan shafi su kuma ta da murya, "Yana Magana a kan mu ne" ga masu bin Almasihu ne na yau.

Ta fadi a kan tsarar mu da mu rike wanna doming a wane tsara na krista su ka yi addu'a, mafarki mu ka kuma mutu – cikamakin Babban Umurni. Kuma idan ba wannan tsra na masu bi ASllah yake so ya yi anfani don yi wa duniya bishara ba, to wane ne kuma?

Wannan bas akin dalilin nasara ba – ko da ma an masu daraja a matsayin aikin bishara na duniya. Kira ne don a fada cikin sabuwar kauna da Yesu domin abin da ke da tamani a gare shi ta zama tamani a gare mu, kuma abnin da ke da fifiko a gare shi ta zama da fifiko a gare mu. Kuma a wannan wuri fifikon Ubangijinmu a bayyane yake a file: "Dan mutum ya zo ne don ya nemi abin da ya bata ya cece shi kuma" (Luka 19:10).

Kaunar Almasihu ne ta iza mu don mu tafi da Albishir Mai dadi nasa. (Karanta 2 Korontiyawa 5:14-15). Shi ya sa za mu tafi. Gaba da haka kristoci da yawa sun zama dankali a hanyar su ta wurin rayuwa, ba su da tunani na manufar Allah kuma babu tausayi na Allah. Yaya bala'I, kuma yaya rashin darajantawa ga Yesu. Ina kalubalantar ku don ku kasance a cikin kwaikwayon duniya na Allah don kwao daukaka na dukan duniya ga Dan Sa. Kamala Babban Umurni tana cika!



LifeBook_Volume_3.indd 113 8/24/15 11:15 AM

**HADDACEWA:**

Sai ya ce musu, ku tafi ko'ina a duniya ku yi wa dukan yan adam bishara Markus 16:15.

**KWAKWARA (ASALIN) GASKIYA**

An umurce mu ta wurin Almasihu don kai kaunar Sa, hasken sa, da kuma ceton sa zuwa ga kowane mutum a ko'ina.

**MARTANIN KA (AMSAR KA)**

- Yaya kai da ikkilisiyar ka kuka shiga cikin aikin bishara a wurare inda kuke zaune?
- Yaya kai da ikkilisiyarka kuka shagala cikin aikin bishara, daukar bishara fiye (gaba) da inda kake zaune?

**LITTAFIN RAI**

**Rubutu**



LifeBook_Volume_3.indd 114 8/24/15 11:15 AM

MAKO 52

# Aikin ka a cikin Shirin Allah a Duniya dukka

**Karanta Zabura 138:8; Yahaya 17:4; Ayukan Manzanni 20:24; Kolosiyawa 4:17.**

A wannan darasi na karshe na *LittafiRayuwa*, ina so in shaida muku daga zuciyata. Allah ya san asalin abin da yake yi yayen da ya kebe ka cewa za ka wakilci Yesu Almasihu a cikin sabon karni. Allah a kullum yana da bayi masu banmamaki a kowace tsara. Amma ya ba ka daraja na wakiltarSa ka kuma yi shelar daukakar sa a tsarar ka. Kamar yadda Dawuda ya bauta wa tsarar sa, ya kamata ka bauta wa tsarar ka. (Karanta Ayukan Manzanni 13:36). Allah ya tsara shugabanai na da saboda lokacin su; Yana siffata ka saboda wannan sabon karni na hidima.

Yayen da kake bauta wa Ubangiji, ka tuna cewa kai gurbi ne (misali). Wasu suna kallon ka. Wani ya taba cewa, "kai Littafi Mai Tsarki ne da wasu mutane ke karantawa." *"Kai ne wasikar mu… sananne kuma mutane ke karantawa; a fili kai wasika ne na Almasihu"* (2 Korontiyawa 3:2-3).

Sa'ad da za mu shaida alherin Allah a kullum ga wasu, a matsayin masu hidimar bishara mu zama maras tausayin kanmu, banda barin wani zunubi ko rashin biyayya a cikin rayuwarmu. Yesu ya ce, *"Ku ne hasken duniya… bari hasken ku ya rika haskakawa a gaban mutane, domin su*

**Domin kowa ya girmama Dan.**
**Yahaya 5:23**



LifeBook_Volume_3.indd 115 8/24/15 11:15 AM

*ga kyawawan ayukanku su kuma daukaka Ubanku da ke cikin Sama.”* (Matiyu 5:14,16). Hasken Yesu yana haskakawa ta wurin rayuwarmu yayen da muka bar Ruhu Mai Tsarki ya mallaki tunanin mu, maganar mu, da kuma ayukan mu.

A matsayin ka na ma’aikaci mai anfani, dole ka zama mai ceton rayuka a kullum. Zarafin ka ne kuma hakinka ne ka dauka ka fara shaida bishara da wasu. Timoti ba mai bishara ba ne; shi fasto ne. Nassi ta shaida cewa ba yana da halin mugunta ba, shirya nazari da kuma koyarwa ba. Duk da haka, Bulus ya roke shi, *“Ka yi aikin mai bishara, ka cika hidimarka*” (Karanta 2 Timoti 4:5). Abin nufi a asalin yaren ita ce yin bishara za ta baka lafiyayyen hidima. Ta wata kalma, idan bishara ba ta cikin bangare a cikin hidimarka, hidimarka a tonkware ne kuma ba cikakke ba. Don haka, idan kai fasto ne, ka zama mai koyar da bishara. Kome da muke yi a cikin hidima ta kara ta wasu bayananen hanya don cika Babban Umurni.

A matsayin shugaba krista, an kira ka kuma don ka zama mai karfafawa. Yanzu muna yaruwa a lokacin da aka yi annabci a da *“Mutane za su suma don tsoro, da kuma fargaban al’amuran da suke aukuwa ga duniya, don za a girgiza manyan abubuwa da suke a sararin sama*.” (Luka 21:26). Har yanzu a cikin *“shan damuwa saboda kugin teku da na rakuman ruwa*.” (Luka 21:25), mu zama masu tsira na bege mai girma. Saboda Yesu, muna da “*domin albarkacin abubuwa guda biyun nan marasa sakewa, masu nuna, cewa ba shi yiwuwa Allah ya yi karya, mu da muka gudu muka sami mafaka, mu karfafa kwarai mu riski abin da muka kafa bege a kai. Begen nan kuwa da muke da shi, kamar anka yake ga rai, kafaffe,*


LifeBook_Volume_3.indd 116 8/24/15 11:15 AM

*tabbatacce, shi ne kuma yake shiga har can ciki bayan labulen*." (Ibraniyawa 6:18-19). Ko da menene za mu iya jimrewa a matsayin masu bi, mu rike nasarar da kuma kyaun Yesu. "*Amma godiya ta tabbata ga Allah, shi da kullum yake yi mana jagaba mu ci nasara, albarkacin Almasihu, ta wurinmu kuma yake baza kanshin nan, na sanin Almasihu a ko'ina."* (2 Korontiyawa 2:14). Alkawarin Uba da kuma ikon Ruhu ya sa zukatan mu ta gudana da bege! *"Allah mai kawo sa zuciya, ya cika ku da matukar farin ciki da salama saboda bangaskiyarku, domin ku yi matukar sa zuciya ta wurin ikon Ruhu Mai Tsarki."* (Romawa 15:13).

Daya daga cikin tushen aikinka a matsayin shugaba Krista ita ce ka zama mai shiryawa. Lokacin da Yesu ya haura zuwa sama, Ya bada shugabanai masu baiwa wa ikkilisiya "*domin shiryar da tsarkaka domin aikin hidima, domin gina jikin Almasihu*" (Afisawa 4:11). Ba za mu zama da taurin kai a matsayin shugabanai krista ba, kuma kada mu musguna ta kowace hanya mutanen da Allah ya sa a kalkashin kulawar mu. Ba hakin ikkilisiya ba ne ta saki shugabanai fastoci zuwa cikin hidima; sai dai, hakin fastoci shugabanai ne su saki ikkilisiya gaba daya zuwa aikin hidima!

Ka danganta da aikin ka a matsayin mai shiryawa hakin ka ne a matsayin jagora. Kristanci a kullum tsara daya ne kawai a waje daga karewa gaba daya. Doka ce cewa mu zuba (saka) abin da muka mallaka ga tsara mai zuwa. Hakika, nawayarmu na farko ita ce mu tarbiyantar da yaranmu na jiki *"sai dai ku goye su da tarbiyya, da kuma gargadi ta hanyar Ubangiji."* (Afisawa 6:4). Allah bai kira ka don ka ceci duniya ka kuma rasa naka iyali ba. Nawayar hidimar ka na farko ita ce ka tabbatar cewa matarka da kuma yaranka suna murna (farin ciki, sun zama almajiran na Yesu Almasihu masu anfani.

An kira fastoci don su shiryar su kuma tara dukkan jama'ar su, amma kuma dole mu yi ta jagorantar da zababbu kadan, mu zuba rayuwarmu a cikin su. Bulus ya tarbiyanta da Timoti. Yayen da Yesu yake hidimta wa taron jama'a, ya horas da almajirai sha biyu. Kuma ko a cikin sha biyun, ya ba da hankalin sa sosai akan guda uku. A kullum ku yi ta duban matasa wadanda Allah yake kiransu saboda hidima. Ku zama mai karfafawa ta muasamman ka kuma tarbiyantar da su. A zahiri, za mu iya auna kokarin mu na gaskiya a cikin abin da muke yin don yin tasiri a kan tsara na gaba saboda Yesu Almasihu.

Ina karfafa ku ku bada hankalin ku ga wadannan abubuwa:

- *Ku bi Allah a kullum*. Ka zama da lokaci da Allah cikin addu'a, sujada, da kuma maganar Sa ita ce tushe.
- *Ka tsare mutuncin ka*. Idan mutane sun rasa yardan su a kan ka, anfanin hidimarka ta kare. Ka kafa bada da lissafi na gaskiya. Andrew Murray ya rubuta cewa, "Kaskanci ita ce uwar kirki da kuma tsaron rai."
- *Ka tsaya kan gaskiyar Nassi*. Ka gaskata Allah da maganar sa. "Har abada, Ya Ubangiji, Maganar ka a kafe take a sama" (Zabura 119:89).
- *Ka maida babban abu ta zama babban abu*. Ka daukaka Almasihu gicciyayye ya kuma tashi. Ka sa bishara da kuma almajirantarwa a tsakiya.
- *Ka kula da ingantaccen dangantaka.* Ka bada fifiko mai zurfi ga inganta dangantaka dfa Allah, matarka, iyalinka, da kuma amintattun abokanai kadan.
- *Ka girma (karu) daga hamayya*. Ka koya daga wurin masu kushe ka. Ka bincike tunanin ka. Ka masa daidai. Ka yi biyayya da Allah. Kada ka ji tsoron mutane (dubi Filibiyawa 1:28).
- *Ka kare wurin ka*. Tsohon ma'aikaci mai hazaka ya bada shawara cewa "Kullum ka kain hari daga wuri da ke da tsaro. Wurin ka ita ce auren ka da kuma iyalinka. Kada ka sa wurin zaman ka cikin hatsari."
- *Ka yarda da baiwar ka*. Ka gano ka kuma bunkasa baye bayen ka da suka mamaya.
- *Bari bankunya (ban takaici) ta yi maka aiki*. Ka yaga a fili bancin rai.
- *Ka yarda da girma ka kuma sammanci al'ajibai*. Ka yi bangaskiya. William Carey yana cikin asarin na shekarun sa yayen da ya kalubalanci krits su "yi kokarin abubuwa masu girma saboda Allah; su sammanci abubuwa masu girma daga wurin Allah."
- *Ka zuba (kwarara) rayuwarka a cikin wasu*. Ka jagorantar (tabiyaanytar) da wasu. Iliya ya zuba rayuwarsa a cikin rayuwar Elisha. Bulus ya kwarara rayuwarsa a cikin rayuwar Timoti. Yesu ya kwarara rayuwarSa a cikin rayuwar almajiransa. Wane ne Timoti din ka?
- *Ka yi abin da ya kamata (cancanta).* Ka kidaya faduwar, ka manta da tsadar, ka biya farashin.



LifeBook_Volume_3.indd 118 8/24/15 11:15 AM

- *Ka ajiye gajeren (guntun) ajiya da Allah ka kuma yi rayuwar cika da Ruhun sa*. Ka yi rayuwa ta hanyar da "kowa zai ga darajar Dan" (dubi Yahaya 5:23). Ka simar da tsarar ka don su cika Babban Umurni na Almasihu.

Rayuwar nasara ta gaskiya ana aunawa ba ta wurin lokacin da ta dauka ba ne amma ta wurin hanyar ta (inda ta nufa); ba ta wurin jam'iyar ta ba amma ta wurin manufar ta, ba ta wurin abin da take da ita da yawa ba amma tya wurin abin da aka watsar (bayar), ba ta wurin rungumar abubuwa ba amma ta wurin rungumar abu daya – a kaunaci Yesu da martaba a kuma sa mutane su kaunace shi a ko'ina.

Yayen da jerin *LittafinRayuwa* take karkarewa, muna so mu tunkare ka da wannan kalubaloli haka – kira iri haka – da aka bayar a karshen sashi na Layin gaba na Tarurukan Makiyaya a fadin duniya. An kira ka daga Allah don ka taimaka a ceto a kuma almajirantar da duniya saboda Almasihu. Allah ya ajiye ka a wurin aikin ka a wannan sa'a na tarihin ikkilisiya na gaske da kuma tarihin duniya. Yanzu ne lokacin don ka aikata.

Akwai aiki da Allah yake so a yi – a cikin ikkilisiyarka, a birnin ka, a kasar ka, a duniya – wanda kai ne kadai zaka iya yi. Zai iya zama akwai littafi a cikin ka da kai ne kadai za ka iya rubutawa, waka da kai ne kadai zaka iya tsarawa, ikkilisiya da kai kadai ne zaka iya ginawa. Ka bude zuciyarka da hankalinka! Allah ya na da babban shiri domin ka!

*"Allah mai zartar da salama, wanda ya ta da Ubangijinmu Yesu, makiyayin tumaki mai girma, daga matattu, albarkacin jinin nan na tabbatar madawwamin alkawari, ya kamala ku da kowace irin kyawawan abu, domin ku aikata nufinsa, ya kuma aikata a cikinmu abin da yake faranta masa rai ta wurin Yesu Almasihu. Daukaka ta tabbata a gare shi har abada abadin. Amin, Amin. (Ibraniyawa 13:20-21).*



LifeBook_Volume_3.indd 119 8/24/15 11:15 AM

**HADDACEWA:**

Saboda haka, da yake muna da wannan hidima bisa ga jinkan Allah, ba za mu karai ba. Ba rtuwanmu da boye-boye na munafunci, ko makirci, ko yi wa Maganar Allah algus, amma ta wurin bayyana gaskiya a fili, sai kowane mutum ya shaida gaskiyarmu a lamirinsa a gaban Allah. 2 Korontiyawa 4:1-2.

**KWAKWARA (ASALIN) GASKIYA**
Allah yana so ya yi anfani da rayuwar ka don taimakawa a cika Babban Umurni.

**MARTANIN KA (AMSAR KA)**
Zaka amsa wadannan kira don aiki?
Zaka fara a yau? Yayen da Ruhun Allah yake kiran ka ka yi wannan kuduri (alkawari), bari Allah ya albarkace ka, ya karfafa ka, ya kuma baka iko.

Ta wurin alherin Allah da kuma iyawar Ruhu, na mika…

- Zan dauki lokaci kowace rana a gaban Allah cikin yabo da kuma sujada, binciken Maganar Sa, da kuma addu'a.
- In kafa a kalla sabon ikkilisiya daya cikin watani sha biyu masu zuwa.
- In jagoranci ikkilisiya da nake hidimtawa ta zama ikkilisiya na Babban Umurni, ta maida hankali akan kai bishara ga mutane domin Almasihu in kuma sa su zama masu biyayya a gare shi, su zama almajira na tsawon rayuwa.
- Ko in tafi da kaina a matsayin mai bishara na ketare al'adu ko sa wasu su tafi a matsayin masu aikin bishara na ketare al'adu.

LITTAFIN RAI

**Rubutu**



LifeBook_Volume_3.indd 120 8/24/15 11:15 AM

### CI GABAN HORASWA SABODA HIDIMA MAI ANFANI

Global Advance sun gaskata da hadin kai da kuma tarayya. Muna aiki da ma'aikatu da yawa don tanadar da kayan aiki don shiryar da ikkilisiya da kyau da kuma shugabanan kasuwanci domin hidima mai bada anfani domin Yesu Almasihu. Muna da tarayya ta dangantaka da wadannan ma'aikatu da kuma makarantu. Muna karfafa ku ku ziyarci yanar gizon domin samun damarmaki na horaswa ta wurin kowace ma'aikata da kuma makaranta. Kuma muna sa zuciya zaku yi ta ziyartar wurin horaswa na yanar gizo Global Advance a kullayome (a kai akai) www.2tim2.org.

### MA'AIKATUN HORAS DA SHUGABANCI

Dynamic Church Planting International
www.dcpi.org

Global Training Network
www.lobaltrainingnetwork.org

Joshua Nations
www.joshuanations.org

### MAKARANTUN HORAS DA MASU HIDIMA

Christ for the Nations Institute
www.cfni.org

SUM Bible College and Theological Seminary
www.sum.edu

The King's University
www.tku.edu



LifeBook_Volume_3.indd 121 8/24/15 11:15 AM

Dale Evrist fasto ne wanda ya kafa NewSong Christian Fellowshi ya kuma ba da basira ga wannan taron ikkilisiya a dukan bangarori na cikin Nashville, Tennesse (USA). Fasto Evrist mawallafi ne, mai kirkira waka, da kuma mai bada shawara ga shugabanai Krista da yawa.

David Shibley ya kafa Global Advance (www.globaladvance.org) a 1990 ya kuma hidimta a matsayin shugaban ta na shekaru ashirin. Mawallafin takardu ne sama da 20, Dr Shibley ya ci gaba da hidimta wa Almasihu ta wurin Global Advance a matsayin wakili na duniya.



LifeBook_Volume_3.indd 122 8/24/15 11:15 AM

Ka himmantu, ka mika kanka yardajje ga Allah, ma'aikaci wanda ba hanya ya kunyata, mai kuma fassara Maganar gaskiya daidai.

2 Timoti 2:15.

Jerin **LittafinRayuwa** an kikrkira don taimakon masu hidimar bishara su zama yardajjen ma'aikata domin Yesu Almasihu da kuma ikkilisiyar Sa. An bunkasa a matsayin saikon nazari na Kankan saboda rayar (bunkasa) Kanka da kuma ma'aikata, wannan kayan aiki mai daraja ta baka taimako a aikace saboda girma a matsayin mai bin Yesu Almasihu da kuma mai hidimar Albishir Mai dadi na Yesu. Ka maida hankali a kan darasi daya kowace mako, darusa 52 ne a cikin jerin **LittafinRayuwa** an tsara su ne don a tanada shekara daya cikakke na rayar (bunkasa) kanka da kuma ma'aikata. Wannan littafi an tsara musamman saboda shugabanai fastoci a kasashe da suka bunkasa wadanda suke hidimtawa a gaba gaba na bisharar Global Advance.

**LittafinRayuwa na 3**, juzu'i na karshe a wannan jerin, tana dauke da darusa guda ashirin da ke Magana akan wadannan take (Kan magana):

- Lafiyayyen Ikkilisiyoyi
- Fasahohi da kuma Dabaru
- Rayuwar ka da kuma Umurnin Sa

Jerin **LittafinRayuwa** an wallafa ta daga Global Advance. Wannan ma'aikata na dukan duniya tana shiryar da shugabanai a fadin duniya don su taimaka a cika Babban Umurni. Wannan ma'aikata ta tanadi horaswa, kayan aiki da kuma karfafawa domin ikkilisiya, kasuwanci, mata, da kuma shugabanai yan matasa a kasashe da yawa. **LittafinRayuwa na 3**, har ma da wasu Karin kayan aiki da yawa, za a iya saukarwa a cikin yawan yaruru (harshe) da ke karuwa daga kan layin yanar gizo na Global Advance a www.2tim2.org

GLOBAL ADVANCE RESOURCES

Tada (Daga) Shugabanai. Canza kasashe



LifeBook_Volume_3.indd 123 8/24/15 11:15 AM